# FASSARAR  LITTAFIN AHLARI

## DA SHARSHI

DR. ABUBAKAR MUHAMMAD ISA

SUKAIRAJ HAFIZ IMAM

AMINU SAlisu

Haƙƙin Mallaka (HM):
Cibiyar Fassara ta Ar-Rahyan
GSM: 08036223067
Whatsapp: 07049325138
*abuamatullahi83@gmail.com*Email:

Tunasarwa:
Ba a yarda a buga ko a kwafi wani ɓangare na wannan littafi don yin amfani da shi ta kowace irin hanya ba, ba tare da izini daga marubuci ko Cibiyar Fassara ta  Ar-Rayhan ba.

An Fara Bugawa a Shekarar:
1445 = 2025

ISBN: 978-978-776-620-0

MAƊABBA'A:
Iconic Computer and Printing Services.
08033676155.

# GODIYA

Ina miƙa cikacciyar godiya ga Allah Subhanahu Wata'Alla, Mai kowa da komai, wanda ni'imominsa ba za su ƙidayu ba, sannan iyaye Saboda falalarsu da gudummawarsu wajen tarbiya, da malamai bakiɗayansu.

Haka ina miƙa godiya da jinjina da fatan alheri, ga bawan Allan da yake kashe dukiyarsa da lokacinsa, da kyakkyawan tunaninsa, a kan wannan aiki Allah ya yi masa albarka a cikin dukkanin lamarinsa, kuma ya albarkaci zuriyarsa, ya kare shi daga dukkanin sharri da abin ƙyama, Allah ya sa wannan gudummawa da yake bayarwa ta zamo masa sanadin shiga aljanna. Haka ina gode wa malamina Babban Limamanin Masallacin Juma'a na Abubakar Gumi Jibwis Mariri.

Sannan ina gabatar da keɓantacciyar godiya ga manya-manyan malaman da suka duba wannan littafin, suka sanya masa albarka da shawarwari, kamar malamina Sheikh Muhammad bin Usman, tare da nauyaye-nauyayan da suke kansa, bai hana shi ba ni cikaccen lokacin sa ba, haka Sheikh Muhammad Sanusi Abubakar ɗan'uwa ga Dr. Aminuddin, sai Sheikh Dr. Ahmad Abubakar Gumi, bisa kyawawan shawarwarinsa masu kyau game da wannan fassarar, da Dr. Nura Baba Yakasai, daga Kwalejin ilimi ta Sa'adatu Rimi, haka Dr. Tijjani Adamu Ɗiso, Saboda muhimmmiyar gudummawarsa ta gyare-gyaren ƙa'idojin rubutun Hausa dalla-dalla, sannan ba zan manta da kwamitin bibiya da tabbatar da saituwar littafin ba, ƙarƙashin jagorancin Chief editor, Dr. Muhammad Nuradden Ado Gezawa, malami a Jami'ar Tarayya ta Dutsin-Ma (Federal University Dutsin-Ma, Katsina), da sakataren kwamitin Malam Nafiu Sabiu Ahmad Mariri, da Malam Ahmad Aminu Nuhu. Ina sake godiya ga Dr. Aliyu Yunus babban limamin masallacin Juma'a na Gadon ƙaya, kuma malami a jami'ar ilimi ta gwamnatin Najeriya ta jahar Kano (Yusif Sule Maitama University), da kuma Ass. Prof. Ibrahim Muhammad Yaƙub daga jami'ar jahar Nasarawa, sai uwa-uba Prof. Hafiz Yusuf Imam babban malami a jami'ar Bayero University Kano, ta yadda ya bibbiyi littafin har ƙarshe, ya ba da gyararraki.

Haka ina miƙa godiya da yabawa ga Babban limamin masallacin (A.R.T.V Kano), Sheikh Sukairaj Hafiz Imam, duk faɗi-tashin wannan aikin tare muka yi, da abokin aikina Malam Aminu Salisu daga sashen Musulunci Legal Kano, haka kuma da ɗalibi mai albarka kuma malami Nafiu Sabiu Ahmad Mariri, da dukkanin waɗanda suka taimaka ta kowacce irin fuska, Allah ya saka kowa da mafi alherin sakamako.

DR. ABUBAKAR MUHAMMAD ISA

## GABATARWAR SHEIKH MUHAMMAD SANUSI ABUBAKAR

**بسم الله الرحمن الرحيم**

**وصلى اللهم على محمد وآله وصحبه وسلم.**

**التقريظ**

Ina farawa da sunan Allah da salati ga Annabi Muhammad da alayensa, da sahabansa bakiɗaya. Na karanta wannan littafi da Dr Abubakar ya wallafa asalin littafin Sheikh Abdurahman Al'akhdari, da marigayi Dr Aminuddeen Abubakar ya yi sharshi da tahlili, bisa tafarkin Sunna.

Haƙiƙa Dr. Aminuddeen ya fito da abubuwan ƙaruwa na ilimimuka masu yawa a aikinsa., ya bayyana irin gwagwarmayar da Sheikh Abdurrahman Al-akhdari ya sha yayin rubuta wannan littafi da ke hannun mai karatu, kasantuwarsa na daga littattafan da ya rubuta a cikin zube, ba waƙe ba, kuma Allah bai ba shi damar kammala shi zuwa ƙarshe ba.

Dr. Aminudden ya gin aikinsa yayin rubuta wannan littafi a kan bayanin matsalolin bisa ga jingina su ga ayoyin Alƙu'ani da Hadisan Annabi (S.A.W), da zantukan malamai daga Mazahabar Malikiyya, da sauran mazahabobin fiƙihu.

Sanin duk mai karatun litattafan fiƙihu, mafi yawancinsu ba su fiya ambaton ayoyin Alƙur'ani ko Hadisi ba, suna wadatuwa ne da abin da suka ƙunsa daga ma'anoninsu da aka kafa hujja da su.

Dr. Abubakar ya zo da wani ƙarin arashi, a kan waɗannan ayyuka na Sheikh Abdurrahman Al-akhdari, da Dr. Aminuddeen Abubakar, yadda ya tattaro, kuma ya kusanto da waɗannan zantuka, tare da taƙaita bayanai a cikin salo mai sauƙi, da saurin shiga ƙwaƙwalwa; daidai da zamanin da ake ciki na taƙaita zance.

Kuma hakan bai hanashi ambaton asalin inda aka ɗauko bayanan kowacce matsala da aka ambata ba. Wanda hakan zai ƙara haskakawa main karatu sanin madogara akan abin da ya karanta. A ƙarshe ina roƙon Allah ya sa wannan aiki ya amfani duk wanda ya karanta duniya da lahira.

Allah ya saka da alheri ya karɓi, ya karɓi wannan aiki da kuka gabatar a kan wannan littafi mai tarin ma'ana da albarka.

**وصلى الله وسلم على نبينا محمد وآله وصحبه.** **المخلص لك**

**محمد سنوسي أبوبكر**

GABATARWAR SHEIKH MUHAMMAD BIN UTHMAN

BABBAN LIMAMIN MASALLACIN SAHABA KUNDILA KANO, NAJERIYA.

الحمد لله وكفى، وسلام على عباده الذين اصطفى

**(تقريظ)** Yabawa da sanya albarka

Wannan aiki na Gwani Abubakar Muhammad Isa da ya yi babba ne, wanda ya cancanci jinjina da yabo. Fassara ƙunshi-ƙunshi na ilimi (متون العلمية), musamman na magabata zuwa ga harsunan da mutane ke iya karantawa, kuma su fahimta; ba ƙaramin alheri ba ne, ganin cewa hakan ɗaya ne daga cikin hanyoyin haɓaka karatu da yaɗa ilimi.

Shi saƙon Musulunci ai bai taƙaitu ga wata jama'a ko wani yanki, ko kuma yare ba. Saƙo ne gamamme kuma shimfiɗaɗɗe har ma ga duniyar waɗanda ba ma iya ganinsu, watau; aljanu, Alƙur'ani mai girma yana cewa:

"يا معشر الجن والإنس"

Wato: " Ya ku gangamin Aljanu da Mutane".

Ka ga a nan an ambaci Aljanu sannan Mutane, Saboda saƙon ba wai na duniyar mutane kaɗai ba ne, a'a saƙo ne na "nauyaya" biyu, wato dai kamar yadda na faɗa, ba wai na duniyar mutane ne kawai ba; har ma da aljanu. To ko su ma aljanun ba za su rasa masu tarjama saƙon ba , zuwa yarukansu mabambanta ba, don haka wannan aiki na Gwani Abubakar Muhammad Isa ya zo a kan gaɓa.

Ina roƙon Allah Jalla Jala-luhu, da ya karɓa mishi wannan aikin, kurakuran da ke ciki kuma Allah ya yafe mishi, Amin summa Amin.

ABUU AASIM MUHAMMAD BIN UTHMAN

Laraba 25- Shawwal-1446 Hijriyya (23/04/2025)

GABATARWAR DR. ALIYU YUNUS MUHAMMAD

بسم الله الرحمن الرحيم

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda yayi baiwa ga ɗan'adam ya aiko masa fiyayyen Manzo ya saukar masa da fiyayyen littafi, ya shiryar da shi tafarki madaidaici. Tsira da aminci su tabbata ga shugaban halitta Annabi Muhammad da alayen sa masu daraja da sahabban sa zaɓaɓɓun bayi da waɗanda suka bi hanyar su har zuwa ranar alƙiyama.

Bayan haka, Manzon Allah (S.A.W) ya faɗa cikin Hadisi ingattacce cewa: "Neman ilimi farilla ne a kan dukkanin musulmi". Malamai sun ce abin da wannan Hadisi yake nufi shi ne wajibi ne Musulmi (namiji ko mace) su nemi ilimin da za su bautawa Allah da shi, tun daga kan abin da zai inganta imaninsa da shi, da kuma abin da zai gyara ibadarsa da shi.

Wannan littafi mai albarka wato "Ahlari" yana cikin littatafai da ya kamata musulmi babba ko ƙarami ya karanta don ya fahimci yadda zai gudanar da addinin sa a matakin farko na neman ilimi, littafin ya ƙunshi bayanai masu muhimmanci wanda ya wajaba musulmi ya sani.

Aikin da malamai suke yi na fassara wannan littafi da makamantansa, aiki ne abin yabo da godiya, domin zai ƙara kusanto da ilimin addini kusa da al'umma, saboda yanayin rayuwar al'umma a yau, ba kowa ne zai samu damar zama gaban malami don ɗaukar karatu ba, kamar yadda hakan shi ne asali, to tunda hakan ba ko yaushe yake samuwa ba, sai ake fassara litattafan addini da Hausa don mutane su samu damar karantawa, kuma abin da basu fahimta ba sai su tambayi malamai ƙarin haske.

Ina addu'ar Allah ya saka wa malamanmu da alheri, ya biya su da gidan aljanna a bisa hidimtawa addinin Allah. Dr Abubakar da ya ɗauki nauyin irin wannan aiki muhimmi Allah ya saka masa da alheri, ya ƙara masa ƙwarin gwiwa don ci gaba da irin waɗannan ayyuka.

Rubutawa: Aliyu Yunus Muhammad (PhD)
Limamin Masallacin Usman Bin Affan Kofar Gadon Kaya, Kano,
Malami a Jami'ar Yusuf Maitama University of Education Kano.

# GABATARWAR ASSOCIATE PROF. IBRAHIM MUHAMMAD YAKUBU

سلام الله عليكم

## Taƙrizi

Godiya ta tabbata ga Allah Maaɗaukakin Sarki, Amincin Allah su tabbata ga Manzon tsira Annabi Muhammad da iyalansa da Sahabansa.

Bayan haka na duba wannan littafi mai muhimmanci da Dr. Abubakar Isa Alhafiz ya fassara, kuma gaskiya zai amfanar matuƙa, musamman a cikin zamanin nan da muke ƙishirwar ilimi. Allah Ubangiji ya karɓi wannan aiki, kuma ya zama sadaka mai gudana.

Saboda alaƙar aikin da Salla ina kira ga hukumar, ko ƙungiyoyi, ko masu hannu da shuni, su taimaka wajen bugawa da yaɗawa, don ya zama guzuri ranar Alƙiyama.

Associate Prof. Ibrahim Muhammad Yakubu

Faculty of Art, Deparment of Islam  and Development Studies

Nasarawa State University, Keffi

GABATARWAR FARFESA HAFIZ YUSUF IMAM

MUKADDIMA

Ina farawa da Sunan Allah Mai rahama Mai jinƙai, da kuma neman Tsira da Amincin Allah su tabbata ga Fiyayyen Talikai Annabinmu Mohammad mai zaburarwa da kuma umarni ga Al'ummar Musulmi kan neman Ilimi tun daga zanin haihuwa har zuwa mayafin ƙarshe na shiga ƙabari. Tsira da Amincin su tabbata ga Alayensa da Matayensa da Sahabbansa har zuwa kanmu da suran dukkan masoyansa baki ɗaya, Aamiin.

Bayan haka, na duba wannan mahimmin littafin mai suna *(Fassarar Littafin Al-akhdhari Na Sheikh Abdurrahman)* wanda Babban Limamin Juma'a na Masallacin ARTV Malam Sukairaj Hafiz Imam tare da Na'ibinsa Gwani Abubakar Muhammad Isa suka fassara daga harshen Larabci zuwa harshen Hausa. Duk da cewar Littafin *"Akhdhari",* an wallafa shi ne a cikin harshen Larabci, littafi ne mai matuƙar mahimmanci wanda ya taka mahimmayar rawa wajen ilimantar da Al'ummar Musulmi musamman ma na Kasar Hausa baki ɗaya. Domin littafi ne wanda ya ƙunshi bayanai kan Addinin Musulumci da kuma yadda ake gudanar da shi tun daga kan tsarki da alwala da sallah da kuma sauran dukkan shika-shikan Musulumcin nan guda biyar.

Babu shakka, wannan aikin na fassara wannan littafin zuwa harshen Hausa, aiki ne gagarumi wanda a yanzu ake da matsananciyar bukatarsa domin ƙarancin malamai masana harshen Larabcin waɗanda sukan karantar da shi tare da fassara shi ga ɗalibai. Amman a yanzu wannan littafin nasu zai sauƙaƙa wa masana wajen karantar da shi da kuma samun sauƙin fahimta wajen ɗalibai masu karantawa. Domin Littafin an tsara shi kan Babi-babi, da kuma Fasalai waɗanda kowanensu sun ƙunshi mahimman ayyukan na addinin Musulumci da kuma bayanan yadda ake gudanar da su daki-daki a cikin sauƙi. Sannan kuma littafin zai ƙara wa masu karatu da kuma masu neman Ilimi wata kyakkywar fahimta ta ainihin nassin Larabcin da kuma cikakkiyar ma'anarsa a cikin harshen Hausa wato (Riba biyu ke nan.)

Bugu da ƙari, malaman nan wato Imam Sukairaj da Gwani Abubakar, sun yi amfani da ƙa'idojin rubutun Hausa da kuma aiki da daidaitacciyar Hausa ingantacciya kuma sassauƙa wajen fassarar da kuma gudanar da wannan mahimmin aikin nasu na wallafa wannan littafin mai suna (Fassarar Littafin Akhdhari). Don haka, ina gode masu kuma ina yaba masu tare da kyakkywan fata na Allah ya saka masu da mafifitan alheransa na duniya da lahira.

A ƙarshe, ina mai ba da umarni/shawa ga al'umar Musulmi maza da mata, yara da manya da su rungumi wannan littafin hannu bibbiyu wajen karanta shi da karantar shi, da kuma amfani da ilimin da yake tattare a cikinsa. Kuma ina fatan Malaman nan Imam Sukairaj da Gwani Abubakar ba za su yi ƙasa a gwiwa ba wajen ci gaba da ire-iren waɗannan ayyukan na alherai a koyaushe, domin samun gamewar fa'ida a tsakanin al'ummar musulmi bakiɗaya, Aamiin.

**Farfesa Hafiz Yusuf Imam,**
**(Sarkin Yakin Makaman Kano),**
Department of Arts and Humanities,
School of Continuing Education (SCE),
Bayero University, Kano.

# GABATARWA

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Maɗaukakin sarki, tsira da aminci su ƙara tabbata ga fiyayen halitta Annabi Muhammad da iyalansa da Sahabbansa da kuma waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa har ranar ƙarshe.

## Taƙaitaccen Tarihin Imamu Malik Ɗan Anas

Imam Mālik ɗan Anas ɗan Mālik ɗan Abī 'Āmir al-Asbahī an haife shi ne a birnin Madina a shekara ta 93 Hijira / 712 Miladiyya, kuma ya rasu a can a shekara ta 179 Hijira / 795 Miladiyya. Asalinsa daga ƙabilar Asbahiyyu ce, wadda ta fito daga Yemen.

Imam Mālik ya taso a gida mai kishin addini da ilimi. Mahaifinsa da kakansa malamai ne, kuma hakan ya sa ya tashi da sha'awar neman ilimi tun yana ƙarami. Ya fara karatun Hadisi yana da kimanin shekara goma zuwa goma sha ɗaya. Ya yi karatu a wuraren malamai sama da ɗari uku (300), ciki har da fitattun Tabi'ai. Daga cikin manyan malamansa akwai Nafi'u, wanda ya karɓi ilimi daga Abdullahi ɗan Umar Allah ya ƙara musu yarda, da Ibn Shihab Az-zuhri, da Rabi'atur-ra'ay. Daga Nafi'u ne Imam Mālik ya samu jerin malamai mai suna "Silsilatuz-zahab", watau sarƙar zinariya saboda ingancinta.

Ya shahara wajen daraja da girmama ilimi da Sunna. An ce idan zai karanta Hadisi, sai ya yi wanka, ya sa turare, ya zauna da ladabi domin girmama maganar Manzon Allah Sallallahu alaihi wa Sallama. Ya kasance mai ƙin faɗin fatawa ko karantar da wani abu sai ya tabbatar da ingancinsa. Idan aka tambaye shi wani abu da bai sani ba, yana iya cewa "Ban sani ba" ba tare da jin kunya ba. Wannan ya nuna tsoron Allah da adalcin da ke cikin zuciyarsa.

Littafinsa mafi shahara shi ne "Almuwaɗɗa" wanda yake ɗaya daga cikin littattafan Hadisi na farko da aka rubuta cikin tsari da ƙa'ida. Littafin ya

haɗa Hadisan Manzon Allah Sallallahu alaihi wa Sallama, fatawowin Sahabbai da Tabi'ai, da kuma ijtihadinsa a fannoni daban-daban na Fiƙihu. Akwai kusan Hadisi 1,720 a cikin wannan littafi, kuma ya kasance hujja ga malamai da dama a fannin fiƙihu da Hadisi.

Mazhabar Mālikiyya, ta dogara sosai da Ayyukan mutanen Madinah (Amalu Ahl al-Madinah), wato yadda mutane a Madina suka ɗauki Sunna a aikace, domin sun fi kusa da zamanin Annabi Sallallahu alaihi wa Sallama. Haka kuma, mazhabar na amfani da hadisi, ra'ayi (ijtihad), da ƙa'idojin ƙiyas da maslaha. Wannan mazhaba ta samu karɓuwa sosai a ƙasashe da dama musamman a yammacin Afirka kamar Najeriya, Mali, Senegal, Mauritania, da kuma ƙasashen Arewa irin su Maroko, Tunisiya, da Aljeriya.

Imam Mālik ya kasance mai natsuwa da kamun kai. Bai yarda da kusantar sarakuna ko amsar kyautukansu ba saboda tsoron kada siyasa ta shafi gaskiya. A wani lokaci, an yi masa duka da azaba saboda ya ƙi yarda da wata fatawa da gwamnatin Abbasiyya ke son ya amince da shi. Duk da haka, bai sauya ra'ayinsa ba, kuma hakan ya ƙara darajarsa a idon al'umma.

Ya rasu a Madina a shekara ta 179 Hijira, kuma aka binne shi a cikin makabartar Baƙi'a, kusa da ƙabarin Sahabbai da sauran manyan malamai. Bayan rasuwarsa, tasirinsa bai gushe ba. Dalibansa sun yaɗa iliminsa a faɗin duniya, kuma har zuwa yau, malamai da ɗalibai suna cin gajiyar koyarwarsa. Daga cikin shahararrun ɗalibansa akwai Imam Ash-Shafi'i, da Imam Muhammad al-Shaybani, ɗalibin Imam Abu Hanifa.

A taƙaice, Imam Mālik ɗan Anas ya kasance ginshiƙi ne a ilimin addini, musamman a fannin Hadisi da Fiƙihu. Iliminsa, taƙawarsa, da hikimarsa sun sa ya zama ɗaya daga cikin manyan malamai da Musulunci ke alfahari da su har zuwa yau.

## Taƙaitaccen Tarihin Mawallafin Littafin Ahalari

Shi ne Sheikh Abu Zaid Abdur-Rahman ɗan Muhammad as-Sagir ɗan Muhammad ɗan Amiru wanda aka fi sani da Al-Akhdari.

An haife shi  a shekarar hijira ta 920 wanda ya yi daidai da 1514 na miladiyya. Ya yi fice wajen ilimi da kyawawan ɗabi'u. Ya yi karatu a hannun manyan Malamai a ƙasar Jaza'ir kamar Mahaifinsa Sheikh Muhammad as-Sagir da ɗan'uwansa Ahmad ɗan Muhammad as-Sagir da Sheikh Abu Abdullahi Muhammad ɗan Aliyu al-Kharubi da kuma Shiekh Abdur-Rahman ɗan Karunu Ahmad Murabiɗi da sauransu.

Ya rubuta litattafa kamar haka: Al-Jauharul Maknun fis Salasati funun, ASiraj fil Hai'ati, Adduratul baida fi ahsanil fununi wal ashbahi, mukhtasarun fi fiƙhil Ibadati da dai sauransu.

Ya kasance ana ƙirga shi a matsayin manyan Malami fitattu na zamaninsa. Ya rasu Hijra na da 983 daidai da 1575 Miladiyya.

## Taƙaitacciyar Gabatarwa Game Da Fassarar  Da Kuma Sharhi

Sanin ilimin da zaka bautawa Allah da shi yana ɗaya daga cikin mafificn dukkan al'amura, Tsarki da Sallah sune manya-manyan jigon abubuwan da ake bautar Allah dasu. Hakan ya zama wajibi akan kowane musulmi ya sansu, domin ba ilimi ne da wani yake ɗaukewa wani ba. Wannan ya sanya naga ya dace na matso da nesa kusa ta hanyar fassara da kuma yin taƙaitaccen bayani akan littafin Ahalari wanda ya ƙunshi tsarki da kuma Sallah domin sauƙaƙa fahimtar yadda za a bautawa Allah cikin sauƙi kuma a ilimance.

Haƙiƙa littafin Ahlari ya samu karɓuwa a garuruwan Musulmai, wannan ya saka mu a nan ƙasar Nijeriya da maƙwabtanta ake karanta shi a duk wani zaure, ko kuma Majalisi da ake koyar da addini a matsayin abu na farko da ake fara koyan ibada da shi. Malamai da dama sun yi wa littafin hidima wajen yi masa sharhi a yaruka daban-daban na duniya. Mafi kyawun sharhin

da yazo hannuna shi ne wanda Marigayi Dr. Aminuddini Abubakar ya rubuta a matsayin kundin da aka ba shi a digirin digirgir (Ph.D) a Jami'ar Bayero da kuma gamamman sharhin da Walid ɗan Fakki ɗan Ibrahin As-Sudani ya yi.

Hausa yare ne da sama da mutum miliyan hamsin suke Magana da kuma rubutu da shi a sassa daban-daban na faɗin duniya. Kuma irin wannan ayyukan na fassara litattafan addini daga larabci zuwa Hausa sun yi ƙaranci a cikin harshen, haka, ya sanya na rubuta nawa littafin da harshen Hausa domin ba da gudummawa da kuma sauƙaƙa fahimtar addini ga ma'abota wannan harshen.

Ina fatan shugabanni da ƙungiyoyi zasu bada irin tasu gudummawar wajen haɓɓaka irin wannan ayyukan domin bunƙasa harshen Hausa da kuma sanar da al'umma ilimi cikin hasrhensu domin samun sauƙin fahimta.

A ƙarshe muna roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya karɓa daga gare mu kuma ya sanya al'umma su fa'idanta daga wannan aikin, ya sakawa duk waɗanda suka bada gudummawa ta kowace irin fuska da mafificin alheri. Abin da ya zama na zamiya a cikin wannan rubutun Allah ya yafe mana.

Dr. Abubakar Muhammad Isa
Sukairaj Hafiz Imam

## اَلْحَمْدُ للهِّ رَبِّ الْعَالَمِينَ

*"Da sunan Allah mai Rahma mai jin ƙai. Godiya ta tabbata ga Ubangijin halittu"*

- ✓ Malam ya fara littafinsa da "Bismillah" kamar yadda yake al'adar marubuta littattafan Fiƙihu da Hadisi da Sira da kuma sauran fannoni na Ilimi.
- ✓ Kamar yadda aikata hakan yana daga cikin koyi da Kur'ani wanda gabaɗaya tsarinsa a kan irin wannan gwadaban yake tafiya.
- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Duk al'amarin da ba a fare shi da faɗin sunan Allah ba; mai yankakkiyar Albarka ne"[1]
- ✓ Ita godiya girmamawa ce da kuma kambamawa daga wanda aka yi wa ni'ima zuwa ga wanda ya yi ni'imar.
- ✓ Godiya sifface da ta ke nuna siffanta abin godiyar (Ubangiji) da dukkan siffofi na kamala da ƙasaita.
- ✓ Haƙiƙanin nuna godiya ga Allah shi ne kwatanta dukkan umarninsa da kuma nisantar dukkan hane-hanensa a fili da kuma ɓoye[2]
- ✓ Ubangiji shi ne mahaliccin halittu gabaɗayansu kuma shi ne mamallakinsu, mai tafiyar da al'amuransu.

## وَالصَّلاَةُ وَالسَّلاَمُ عَلَى سَيِّدِنَا مُحَمَّدٍ خَاتَمِ النَّبِيِّينَ وَإِمَامِ الْمُرْسَلِينَ:

*"Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa kuma shugaban Manzanni"*

- ✓ Sannan Malam ya cigaba da yi wa Ma'aiki - tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi salati- domin sauke haƙƙi na biyu bayan haƙƙin farko da yake na Ubangiji ne.
- ✓ Mafi girman ni'imar Allah a kan halittarsa ita ce samuwar Ma'aiki.

---

[1] Ahmad ibn Ali ibn Hajar al-Asƙalani "Takhrijul Ahadisil Kashshaf" (1/24), Abu Zakariyya Yahya ibn Sharaf an-Nawawi "Al'azkar", shafi na (202)

[2] Fakrud Dini ar-Razi "Tafsirul Kabir" (1/197)

- ✓ Ma’anar salatin Allah ga Annabi, shi ne yabawar da Ubangiji yake yi wa Ma’aiki a cikin manya-manyan mala’ikunsa.
- ✓ Ma’anar tsira da amincin Allah, shi ne kuɓutar Ma’aiki daga dukkan wani aibu a duniya da kuma Lahira, ko da yake tabbataccan abu ne ga Annabi, kaɗai dai mun faɗa saboda cika umarnin ubangiji maɗaukakin sarki.[1]
- ✓ Haƙiƙa cikin yi wa Annabi Salati akwai lada sosai, ko babu komai ya ishi bawa in ya yi wa Ma’aiki Salati ɗaya Allah zai yi masa guda goma.[2]
- ✓ Shugabancin Annabi tabbataccen al’amari ne da babu mai shakka a kansa (sai dai wanda ba Musulmi ba) domin da kansa Ma’aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Ni ne shugaban ‘yan'adam ba tare da alfahari ba”[3]
- ✓ Da shi ne - tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi - dukkan Annabta ta cika kamar yadda Kur’ani ya bayyana.[4]

## أَوَّلُ مَا يَجِبُ عَلَى الْمُكَلَّفِ تَصْحِيحُ إِيمَانِهِ

*“Farkon abin da yake wajaba a kan baligi ya inganta imaninsa”*

- ✓ Wajibi: Shi ne aikin da dole sai ka aikata kuma in ka aikata zaka samu lada, haka, in ka bar shi za a yi maka uƙuba.[5]
- ✓ Baligi: In aka ce baligi a shari’ance ana nufin mutumi mai hankali da hukuncin Shari’a ya hau kansa.[6]
- ✓ Inganta Imani yana zama wajibi a kan mai hankali, Baligi wanda saƙon Musulunci yazo masa, kuma yana da lafiyar saurare da kuma gani.

---

[1] Suratul Ahzab, aya ta (56)
[2] Muslim ɗan Hajjaj “Sahihu Muslim” (384)
[3] Ibn Majah “Sunan Ibnu Majah” (4308)
[4] Suratul Ahzab, aya ta (40)
[5] Muhammad bn Salihu Al’Usaimin “Al-Usul fi Ilimil Usul”, shafi na 11
6 Aminuddini Abubakar “Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat”, Shafi na 115

- ✓ Yana tabbatuwa ne ta hanyar kaɗaita Allah shi kaɗai wajen yin Imani da kuma yin Ibada saboda Allah shi kaɗai. Na farko shi ne kore yin dukkan wani aiki ba don Allah ba (Riya), na biyu shi ne kore sanyawa Allah kishiya.
- ✓ Imamul Kurdubi yana cewa: "Farkon abin da yake wajibi ne a bayyana shi; shi ne kaɗaita Allah kuma ba ya halatta a ɓoye hakan"[1]
- ✓ Imani: "Kalmar Imani a shari'ance tana nufin gasgata Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cikin dukkan abin da yazo da shi daga ubangijinsa, kuma hakan ya dace da furucinsa da kuma ayyukansa"
- ✓ "Haka kuma Imani yana ƙaruwa ta hanyar ayyukan ɗa'a kamar yadda yake raguwa ta hanyar ayyukan saɓo"[2]
- ✓ Imani yana da rukunai guda shida:

  i) Imani da Allah, ii) Imani da Mala'ikunSa,

  iii) Imani da LittattafanSa, iv) Imani da ManzanninSa,

  v) Imani da Ranar Lahira,

  vi) Imani da Ƙaddara (Mai kyau ko mara kyau)
- ✓ Rabe-raben Tauhidi
  - Kaɗaita Allah wajen ayyukansa: Shi ne cikakken Imani da cewa Allah shi ya halicci komai, kuma komai a ƙarƙashin mulkinsa yake, shi ne yake azurta kowa, kuma shi ne mai rayawa, kuma yake kashewa, haka kuma shi ne mai yadda yaso.
  - Kaɗaita Allah wajen bauta: Shi ne ƙudurce kaɗaituwar Allah da aiwatar da dukkan dangin wata bauta ta dukiya ko ta jiki ga Allah kaɗai. Misali:
    a. Addu'a (Allah shi kaɗai ake roƙo cikin abin da wani ba zai iya yi ba sai shi),

[1] Abu Abdullah Muhammad ɗan Ahmad al-Kurdubi "Ahkamul Kur'an" (2/128)

[2] Abu Zaidil Kairawani "Risala", shafi na (10)

   b. Haka Bakance da kuma Yanka dabba duk ana yin su ne kaɗai saboda shi.
   c. Kamar yadda Sallah da Azumi da Zakka da sauran Ibadu ba a yin su sai ga Allah kaɗai.
- Kaɗaita Allah cikin sunayensa da kuma Siffofinsa: Shi ne kaɗaita Allah cikin dukkan SunayenSa da kuma Siffofinsa da suka zo a cikin Kur'ani da kuma Hadisai ba tare da kamantawa ko kwatantawa ko canjawa ko korewa ba.

✓ Abubuwan da suke warware Imani

- Babbar Shirka wato sanyawa Allah kishiya cikin bauta masa.
- Bautar wani abu ba Allah ba, da niyyar neman kusanci ga Allah.
- Kudurce fifikon dokokin da ba na Allah a kan na Allah.
- Kyamatar wani abu daga cikin sunnonin Ma'aiki.
- Jiɓantar kafirai
- Yin izgili ga wani abu na addini.
- Yarda da wani hukunci koma bayan na Allah
- Kafircewa ɗaya daga cikin Annabawa
- Imani da Bokanci

✓ Hanyoyin inganta Imani:

- Soyayyar Allah da kuma Manzonsa,
- Kaunar magabata na ƙwarai da kuma koyi da su,
- Soyayya da kuma Kiyayya don Allah,
- Ka so wa ɗan uwanka abin da kake sowa kanka na alheri,
- Barin jayayya da ƙarya ko da kuwa cikin raha ne,
- Yaɗa Sallama.

ثُمَّ مَعْرِفَةُ مَا يُصْلِحُ بِهِ فَرْضَ عَيْنِهِ كَأَحْكَامِ الصَّلاَةِ وَالطَّهَارَةِ وَالصِّيَامِ

*"Sannan ya san abin da zai gyara farillan da suke kansa kamar hukunce-hukuncen Sallah da Tsarki da kuma Azumi.*

- ✓ Bayan bawa ya kyautata imaninsa ya zama wajibi ya san abin da zai inganta farillan da suke kansa kamar sanin hukunce-hukuncen Sallah, wanda ya ƙunshi sanin Farillanta da Sunnoninta da Mustahabbanta da Sharaɗanta da kuma abubuwan da suke ɓatata.
- ✓ Haka wajibi ne a kan Baligi ya koyi hukunce-hukuncen tsarki domin shi (Tsarki) sharaɗi ne na ingantuwar Sallah. Cikakken bayani zai zo a gaba.
- ✓ Sannan wajibi ne a kan Baligi ya san hukunce-huncen Azumi wanda ya ƙunshi sanin Farillansa da Sunnoninsa da Mustahabbansa da Sharaɗansa da kuma abubuwan da suke ɓata shi.
- ✓ An taƙaita farillan a kan Tsarki da Sallah da kuma Azumi domin sune suke hawa kan kowanne muslmi, ba kamar Zakka da kuma aikin Hajj ba waɗanda ba kan kowa suke hawa ba, sai waɗanda Allah ya ba wa dukiya da kuma iko.[1]
- ✓ Sanin farilla wajibi ne a kan kowanne baligi kasancewar ba a bautawa Allah a kan jahilci. Magabata sun haɗu akan bai halatta ga Baligi ba ya aikata wani aiki a cikin Ibada (Sallah, Zakka, Azumi, Aikin Hajj da sauransu) ko Mu'amala (Cinikayya, Auratayya, Shugabanci da sauransu) har sai ya san hukuncin Allah a ciki.

وَيَجِبُ عَلَيْهِ أَنْ يُحَافِظَ عَلَى حُدُودِ اللهِ

*"Wajibi ne a kan Baligi ya kiyaye iyakokin Ubangiji"*

- ✓ Wato ya kiyaye dokokin Allah ta hanyar sanin Wajibai da Mustahabbai da Haramun da kuma Makaruhai.

---

[1] Aminuddini Abubakar "Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat" (115)

- ✓ Wajibi ne a kan Baligi ya miƙa wuya cikin dukkan hukunce-hukuncen Allah.
- ✓ Haka, ya nisanci dukkan abin da zai kaishi ga fushin Allah ta hanyar bijirewa hukunce-hukuncesa saboda tsoron kar ya afka cikin fushin Allah.

وَيَقِفَ عِنْدَ أَمْرِهِ وَنَهْيِهِ

*"Ya tsaya in da aka umarce shi kuma ya hanu da abubuwan da aka hane shi"*

- ✓ Dole ne a kan Baligi ya aikata abubuwan da aka umarce shi da su kuma ya bar abin da aka hane shi da aikatawa na dukkan saɓo da kuma ababan ƙi.
- ✓ Da haka ne mutum yake zama cikakken Mumini, kamar yadda aya ta 7 cikin suratul Hashri da aya ta 36 cikin suratul Ahzab da aya ta 65 cikin suratun Nisa'i da kuma makamantansu suka bayyana.

وَيَتُوبَ إِلَى اللهِ سُبْحَانَهُ قَبْلَ أَنْ يَسْخَطَ عَلَيْهِ

*"Ya tuba zuwa ga Allah tun kafin ya yi fushi da shi"*

- ✓ Lokcin da Baligi ya ƙetare iyakokin Ubangiji; wajibi ne a kansa ya gaggauta tuba tun kafin Allah ya yi fushi da shi.
- ✓ Tuba yana daga cikin mafi muhimman al'amura a wajen manyan bayin Allah domin shi ne mataki na farko da suke takawa wajen komawa izuwa ga Allah.[1]
- ✓ Tuba na nufin barin saɓo da kuma aikata ayyuka nagari.
- ✓ Wato idan baligi ya aikata wani aiki na saɓo ta hanyar barin abin da yake wajibi ne ko kuma aikata wani aiki da aka hana shi; tilas ne a kansa ya tuba ga Allah.

---

[1] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", shafi na (19)

- ✓ Wajibine ga dukkan wanda ya aikata saɓo ko kuma ya bar abin da yake wajibi ne da ya tuba zuwa ga Allah, tuba na gaskiya saboda faɗin Allah Maɗaukakin sarki a cikin suratut Tahrim aya ta 8 da suratun Nur aya ta 31 da suratu Hud aya ta 3 da sauransu.
- ✓ Annabi tsira da amicncin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Ya ku mutane! Ku tuba izuwa ga Allah, domin ni ina tuba izuwa gare shi sau ɗari a rana"[1]
- ✓ Tuba yana da babbar falala a wurin Allah ta yadda mai zunubi in ya tuba (tuba na gaskiya) zai zama kamar wanda bai taɓa yin zunubin ba.
- ✓ Tuba in aka bi bayansa da kyawawan ayyuka; Allah yana canza zunuban zuwa lada kamar yadda yake a cikin suratul Furƙan aya ta 70.
- ✓ Mala'ikun da suke ɗauke da Al'arshi da kuma wanda suke gefansu suna nemawa waɗanda suka tuba gafarar Ubangiji kamar yadda yake cikin suratu Gafir (7)

**وَشُرُوطُ اَلتَّوْبَةِ النَّدَمُ عَلَى مَا فَاتَ، وَالنِّيَّةُ أَنْ لاَ يَعُودَ إِلَى ذَنْبٍ فِيمَا بَقِيَ عَلَيْهِ مِنْ عُمُرِهِ، وَأَنْ يَتْرُكَ الْمَعْصِيَةَ فِي سَاعَتِهَا إِنْ كَانَ مُتَلَبِّسًا بِهَا**

*"Sharuɗan Tuba: Yin da-na-sani cikin abin da ya aikata na saɓo, Kudurcewar ba zai sake komawa ga saɓon ba cikin abin da ya rage na rayuwarsa. Kuma ya bar aikata laifin kwata-kwata in ya kasance mai cuɗanya da shi"*

- ✓ Malam ya fara da ambaton sharuɗan tuba da babu makawa sai da su tuba yake zama ingantacce.
- ✓ Ana tuba ne cikin ɗaya daga cikin laifuka, ko dai laifin da yake Ubangiji aka yi wa shi, sharaɗan tubansa uku ne:
- ✓ Yin nadama cikin abin da baligi ya aikata na saɓa wa Allah

[1] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (2702)

- ✓ Ya daura niyyar ba zai sake komawa zuwa ga wannan saɓon ba cikin abin da ya yi saura na rayuwarsa.
- ✓ Ya bar saɓon da kuma abubuwan da suke ka ishi ga aikata saɓon
- ✓ Ko kuwa haƙƙin da yake da alaƙa da ɗan uwanka ɗan'adam, shi ma wannan Allah ba ya yafe haƙƙin wani.
- ✓ Ko dai haƙƙi na dukiya, wajibi ne a mayar da ita ga ma'abociyarta, in kuwa ya rasu tilas ne a mayar da ita ga magadansa. A halin ba a samu magadan ba; za a yi sadaƙa da wannan haƙƙin da niyyar Allah ya kai masa ladan.
- ✓ Haƙƙi na zubar da Jini ta hanyar duka ko kisa da sauransu, wajibi ne a kan baligi ya kai kansa zuwa ga wanda ya zubarwa da jinin ko kuma waliyansa domin karɓar haƙƙi.
- ✓ Keta mutunci, kamar zagin mutum ko cin mutuncinsa ko kuma yi masa ƙage, wajibi ne a kan baligi ya nemi yafiyarsa a dunƙule ba tare da bayyan masa dalilin neman yafiyar ba. Ko kuma yaje cikin mutanen da ya aibata shi ya wanke shi kuma ya nema masa gafarar Allah.

**وَلاَ يَحِلُّ لَهُ أَنْ يُؤَخِّرَ التَّوْبَةَ، وَلاَ يَقُولُ: حَتَّى يَهْدِيَنِي اللهُّ فَإِنَّهُ مِنْ عَلاَمَاتِ الشَّقَاءِ وَالْخِذْلاَنِ وَطَمْسِ الْبَصِيرَةِ**

*"Ba ya halatta a kan baligi ya jinkirta Tuba kuma kar yace, har sai Allah ya shirye ni, domin yin haka na daga alamar rashin rabon Lahira da taɓewa da kuma toshewar basira"*

- ✓ Daga bayanin Malam za mu fuskanci wajibi ne ga baligi ya gaggauta Tuba a duk lokacin da ya aikata wani aiki na saɓo.
- ✓ Ƙauracewa ayyukan saɓo ba sa yankewa mutuƙar Tuba bai yanke ba. Tuba kuwa ba ya yankewa har sai rana ta fito daga mafaɗarta.

- ✓ Hadisin ma'aiki ya bayyana haka a fili in da yake cewa: "Lallai Allah yana karɓar tuban bawa mutuƙar ransa bai je gargara ba"[1]
- ✓ Gaggauta Tuba wajibi ne duk wanda ya jinkirta shi ya zama mai laifi, domin jinkirin ƙarin laifi ne.[2]
- ✓ Kada ya kafa hujja da cewa shiriya ta Allah ce, kamar yadda Mushirikai suka kafa hujja[3]

**وَيَجِبُ عَلَيْهِ حِفْظُ لِسَانِهِ مِنَ الْفَحْشَاءِ وَالْمُنْكَرِ، وَالْكَلَامِ الْقَبِيحِ، وَأَيْمَانِ الطَّلَاقِ، وَانْتِهَارِ الْمُسْلِمِ وَإِهَانَتِهِ، وَسَبِّهِ وَتَخْوِيفِهِ فِي غَيْرِ حَقٍّ شَرْعِيٍّ.**

*"Wajibi ne a kan baligi ya kiyaye harshensa daga alfasha da kuma abin ƙi, da mummunan zance da kuma rantsuwar saki, da kyarar musulmi, da kuma wulaƙanta shi, da zaginsa, da kuma tsorata shi ba tare da haƙƙi shari'a ba"*

- ✓ Wajibi ne a kan baligi ya kiyaye harshensa daga waɗannan cututtuka da suka gabata. A Ƙur'ani kamar yadda yake cikin Suratul Ahzab aya ta 70-71 da kuma Suratu Ƙaf aya ta 18 da Suratun Nisa'i aya ta 114, 148 da Suratul Hujurati aya ta 6 da suratul Hajji aya ta 30 duk sun bayyana hatsarin sakin harshe da kuma kiyaye shi.
- ✓ Haka kuma Hadisan Annabi sun bayyana hatsari da kuma illolin sakin harshe, daga cikinsu: "Aljanna ta yi daɗi ga wanda ya mallaki harshensa…"[4]
- ✓ Abdullahi ɗan Amru ɗan As ya ce, Ya Manzon Allah! Wannne musulmi ne yafi kowa? Sai Manzon Allah ya ce: "Shi ne wanda Musulmai suka kuɓuta daga sharrin harsensa da hannunsa"[5]

---

[1] Abu Isa Muhammad bn Isa At-Tirmizi, Sunanut Tirmizi (3537)
[2] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", shafi na (21)
[3] Suratul Zukhruf (20), Suratul An'am (148)
[4] Aɗ-Ɗabariniyyu "Al-Ausaɗ da As-Sagir"
[5] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim", (40)

- ✓ Malik ɗan Dinar ya ce: “Idan ka ji alamun zuciyarka ta bushe, Sa’annan ga Kasala, ga kuma tawayar Arziki; kasani ka yi Magana cikin abin da ba zai amfaneka ba”[1]
- ✓ Ba ya halatta ga baligi ya furta mummunan zance da yi wa mutane zunɗe da aibatasu da kuma cin zarafinsu.
- ✓ Wajibi ne a kan baligi ya kiyaye harshensa daga rantsuwar saki domin ita rantsuwa tana daga cikin jinsin ibada, don haka ba ya halatta a yi rantsuwa sai da abin da Allah ya halatta a yi rantsuwa da shi. Ba a rantsuwa da Saki, haka ba a rantsuwa da Annabi ko Ka’aba, ko rayuwar wani da kuma makamantansu.
- ✓ Ita rantsuwa ba ta halatta sai ga Allah kaɗai, ko kuma wani suna daga cikin sunayensa ko siffa daga cikin siffofinsa.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: “Duk wanda zai yi rantsuwa to ya rantse da Allah ko ya yi shiru”.[2]
- ✓ Haka a wani Hadisin Ma’aiki ya ce: “Duk wanda ya rantse da wanin Allah haƙiƙa ya yi shirka” wa ni lafazin “Ya kafirta”.[3]
- ✓ Zance yana rabuwa zuwa gida biyar a bisa mahangar Addini
    - Wajibi: Kamar furta Kalmar shahada, Umarni da kyakkyawa da kuma hani da mummuna.
    - Haramun: Kamar Gulma, Annamimanci
    - Mustahabbi: Kamar Zikiri da Istigfari
    - Makaruhi: Kamar hira bayan sallar Asuba da kuma Sallar Isaha’i
    - Mubahi: Kamar rera waƙar da babu cutarwa a cikinta kuma babu amfani.

[1] Al-Mardasiy “Umdatul bayan”, shafi na 7
[2] Muhammad ibn Isma’il al-Bukhari “Sahih al-Bukhari”, (6108)
[3] Ahmad ɗan Hanbal “Musandu Ahmad”, (329)

**وَيَجِبُ عَلَيْهِ حِفْظُ بَصَرِهِ عَنِ النَّظَرِ إِلَى الْحَرَامِ،**

*" Wajibi ne a kan baligi ya kiyaye ganinsa daga kallon haramun"*

- ✓ Wato wajibi ne a kan baligi ya kiyayye idanuwansa daga kallon dukkan wani dangi na abubuwan haramun, kamar kallon Macen da ta haramta ya kalleta, da kyakkyawan saurayi ta fuskar kallo irin na sha'wa da jin daɗi. Haka kuma haramun ne kallon jaridu da Talabijin da Kuma Wayar hannu ko Na'ura mai ƙwaƙwalwa wanda suke ɗauke da hotuna ko kuma bidiyo na batsa.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana cewa:
  - "(Ya kai Annabi) Ka gaya wa muminai maza da runtse ganinsu kuma su kiyaye farjinsu, hakan shi ne mafi tsarki a gare su…"[1]
  - "(Ya kai Annabi) Ka gaya wa muminai mata da su runtse ganinsu kuma su kiyaye farjinsu…"[2]
  - "Lallai ne Ji da gani da zuciya dukkaninsu ababan tambaya ne (ranar gobe Kiyama)"[3]
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:
  - "Na haneku da zama a gefen hanyoyi" sai Sahabbai suka ce: Babu makawa sai mun zauna fa?. Sai Annabi ya ce: "In ya zama dole sai kun zauna, to, ku ba wa hanya haƙƙinta" sai suka ce: Mene ne haƙƙin hanya ya kai Ma'aikin Allah? Sai y ace "Runtse gnni da kamewa daga cutarwa da umarni da kyakkyawa da kuma hani da mummuna"[4]

---

[1] Suratun Nur, aya ta 30
[2] Suratun Nur, aya ta 31
[3] Suratul Isra'I, aya ta 36
[4] Abu Dawud Sulaiman ɗan al-Ash'ath "Sunan abi Dawud", (4815)

- "Shi kallo wata kibiya mai guba daga kibiyoyin Iblis, wanda ya bar shi don tsoron Allah; zan canza masa garɗin Imani da zai ji shi a cikin ƙoƙon zuciyarsa"a[1]
- Sayyiduna Ali ya kasance yana cewa: "Duk wanda bai iya mallakar idanuwansa ba; Zuciyarsa ba ta da wata ƙima"
- Zannun al-Misri ya ce; "Runtse ido katanga ce ta afkawa sha'awa"

**وَلاَ يَحِلُّ لَهُ أَنْ يَنْظُرَ إِلَى مُسْلِمٍ بِنَظْرَةٍ تُؤْذِيهِ إِلاَّ أَنْ يَكُونَ فَاسِقًا فَيَجِبُ هِجْرَانُهُ**

*"Haka kuma bai halatta ya yi wa Musulmi kallon da zai cutar da shi ba, sai dai in fasiƙi ne, to wannan wajibi ne a ƙaurace masa"*

- ✓ Haramun ne a kan baligi ya yi wa ɗan'uwansa musulmi kallon raini, wulaƙantawa da kuma cutarwa kamar yadda maƙiya Allah suke yi wa muminai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: "Kafirai sun kusa su cutar da kai da kallonsu yayin da suka ji ƙur'ani, suna cewa lallai shi mahaulaci!"
- ✓ Shi wanda yake saɓon Allah (Fasiƙi) wajibi ne a ƙaurace masa in ba za a iya hana shi saɓon ba da hannu ko da baki.
- ✓ Mai bayyana saɓo wanda ba ya jin kunyar bayyanawa wajibi ne a ƙaurace masa domin ya zama izina ga masu irin halinsa.
- ✓ Matuƙar musulmi zai iya tsawatarwa fasiƙi; bai halatta ya ƙaurace masa ba.[2]

[1] Aɗ-Ɗabaraniy "Al-Kabir", (10363)

[2] Aminuddini Abubakar "Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat", Shafi na 158

وَيَجِبُ عَلَيْهِ حِفْظُ جَمِيعِ جَوَارِحِهِ مَا اسْتَطَاعَ

*"Wajibi ne a kan baligi ya kiyaye dukkan gaɓɓansa gwagwardon iko"*

- ✓ Malam ya game Magana ta in da ya bayyana kiyaye gaɓobi daga saɓo ta hanyar amfani da su wajen ayyukan ɗa'a da kuma kiyayesu daga faɗawa dukkan ayyukan saɓo.[1]
- ✓ Wani daga cikin magabata yana cewa "duk wanda ya kiyaye dokokin Allah a cikin ƙoƙon zuciyarsa da tunaninsa; Allah zai kiyaye shi a cikin gaɓoɓinsa"[2]
- ✓ Wato ya kiyaye harshensa daga ƙarya da gulma da munafurci da sauransu domin harshe shi ne mafi girman hatsar a kan sauran gaɓɓai.
- ✓ Ya runtse ganinsa daga kallon abubuwan da suke haramun ne.
- ✓ Ya kiyaye kunnuwansa daga jin gulma ko zantukan na ƙarya da zancen batsa da makamantansu.
- ✓ Ya kiyaye hannayensa daga karɓa ko kuma ɗiban haram.
- ✓ Ya kiyaye ƙafafunsa daga zuwa guraran ɓarna da ayyukan laifi.
- ✓ Ya kiyaye cikinsa daga cin haramun.
- ✓ Ya kiyaye farjinsa daga zina da luwaɗi.
- ✓ Kiyaye dukkan gaɓoɓi na daga cikin kamalar addinin bawa.

وَأَنْ يُحِبَّ للهِ وَيُبْغِضَ لَهُ وَيَرْضَى لَهُ وَيَغْضَبَ لَهُ

*"Kuma ya so abu don Allah, kuma ya yi ƙiyaya don Allah, ya yi fushi don Allah kuma ya yarda don Allah"*

- ✓ Imanin Baligi ba ya cika har sai ya yi soyayya da kuma ƙiyayya don Allah.

[1] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", Shafi na (29)

[2] Ibnul Jauzi "Sifatus Safwa", 4/366

- ✓ Haƙiƙanin soyayya don Allah shi ne, kaso mutum ba don wani abu da za ka amfana da shi ba a duniya, sai kawai don abin da ya shafi gyara Lahira da kuma neman yardar Allah.
- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Duk wanda ya yi kyauta don Allah, ya hana don Allah, ya yi soyayya saboda Allah, ya yi ƙiyayya saboda Allah, ya aurar saboda Allah; haƙiƙa Imaninsa ya cika"[1]
- ✓ Daga cikin maganganun magabata da suke tsantsar soyayya saboda Allah shi ne abin da Sayyidina Umar ya faɗa akan Umair. Umair ɗan Wahab yazo Madina da niyyar kashe Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi amma sai ya musulunta. Umar Allah ya ƙara masa yarda sai yake cewa wanda suke zauna da shi: "Umair yazo garin Madina wallahi gwara Alade da shi a zuciyata sannan ya muslunta sai na ji nafi ƙaunarsa fiye da yayana"[2]
- ✓ Fa'idojin soyayya don Allah:
  - Samun jin garɗin Imani.
  - Shigar bawa inuwar Allah a ranar Lahira.
  - Samun soyayyar Allah.
  - Samun nutsuwar zuciya.
- ✓ Kamar wanda yake son malaminsa saboda shi ne yake koyan yadda zai bautawa  Allah a wurinsa.
- ✓ Haka kuma kana ƙyamatar mutum ba don komai ba sai don yana saɓon Allah ko kuma kana ƙyatamar wanda Allah yake ƙyamatarsa ta hanyar ƙaurace masa ko kuma daina kula shi.
- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance fushinsa ba ya bayyana har sai an keta alfarmar Ubangiji.[3]

---

[1] Abu Isa Muhammad ibn Isa at-Tirmizi "Sunan at-Tirmizi" (2458)
[2] Imam az-Zahbi "Siyar al-A'alamun Nubala'i" (1/364)
[3] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari", (6786)

- ✓ Akwai bambanci tsakanin ƙiyayya da kuma rashin haɗuwar jini. Wani lokacin za ka samu mutum da baka ƙinsa, amma kuma baka jituwa da shi, irin wannan ɗabi'a ce ta halayyar ɗan Adam.

وَيَأْمُرَ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَى عَنِ الْمُنْكَرِ

*"Ya yi umarni da kyakkywan aiki kuma da ya yi hani da mummuna"*

- ✓ Umarni da kyakkyawan aiki, da kuma hani da mummuna shi ne mafi muhimmancin abin da shar'a ta wajabtawa Baligi kuma da shi ne al'umma take gyaruwa ta samu kyakkyawar rayuwa.
- ✓ Saboda haka ne Allah ya aiko Manzanni, ba don haka ba da jahilci zai yaɗu, ayyukan ɓarna za su yawaita, zalunci zai yawaita, bayin Allah za su halaka.
- ✓ Umartar mutane da abin da shari'a ta umarce su da shi, da kuma hana su abin da shari'a ta hane su da shi, shi ne abin da ake nufi da Umarni da kyakkyawa da kuma hani da mummuna.
- ✓ Umarni da kyakkyawa da kuma hani da mummuna wajibi da wasu suna iya ɗaukewa wasu.
- ✓ Sharaɗan gyara mummunan aiki:
  - Abin ƙin ya zama cikin ababan da aka haramta ne a shari'a.
  - Kar a garin canza mummuna kuma a haifar da mafi muni. Kamar garin hana shan giya a kai ga kisan kai.
  - Mummunan ya zama a bayyane yake, ba a bin diddigin mutum don neman laifinsa.
- ✓ Siffofin wanda zai yi umarni da kyakkyawan aiki da hani da mummuna:
  - Ya zama musulmi kuma mai cikakken ilimi
  - Ya zama mai tsantseni.
  - Ya zama mai kyawawan ɗabi'u.

وَيَحْرُمُ عَلَيْهِ الْكَذِبُ

*"Karya tana haramta a gare shi"*

- ✓ Karya na nufin faɗar akasin labari.
- ✓ Tana ɗaya daga cikin manya-manyan zunubai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya aibata maƙaryata a wurare mabambanta a cikin Kur'ani, daga ciki, Faɗinsa Maɗaukakin sarki:
  - "Haƙiƙa Allah ba ya shiryar da wanda yake maɓarnaci ne kuma mai yawan ƙarya"[1]
  - "Ranar Kiyama za ka ga waɗanda suka yi wa Allah ƙarya fuskarsu ta yi baƙiƙƙirin"[2]
- ✓ A gurare da dama Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana bayyana illolin ƙarya, daga ciki faɗinsa:
  - "…Lallai ƙarya tana shiryarwa izuwa ga fajirci, kuma fajirci yana shiryarwa zuwa ga wuta. Mutum ba zai gushe ba yana ƙarya har an rubuta shi tataccen maƙaryaci a wurin Allah"[3]
  - "Abubuwa huɗu duk wanda ya kasance a cikinsu, haƙiƙa ya zama tataccen munafiki…daga cikinsu akwai wanda in zai yi zance sai ya yi ƙarya…"[4]
- ✓ Rabe-raben ƙarya
  - Tana zama wajibi kamar in yinta zai kuɓutar da mutum daga halaka ko kuma hana wani zalinci.
  - Tana zama haramun kamar yin ta lokacin wasa ko kuma raha.
  - Tana zama "Mustahabbi" lokacin da za a sasanta tsakanin musulmin da suke rigima ko kyautata rayuwar ma'aurata ko kuma yin ta a lokacin da ake yaƙi don ɓatar da maƙiya Allah.

---

[1] Suratu Gafir, aya ta 28
[2] Suratu zuma, aya ta 60
[3] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari", (2607)
[4] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim", (58)

## وَالْغِيبَةُ

*"Da Gulma"*

- ✓ Gulma na nufin ka ambaci ɗan uwanka musulmi da bin da yake ƙyamata a bayan idonsa wanda da zai ji abin da ka faɗa da ransa ya ɓaci.
- ✓ Gulma haramun ce a cikin Kur'ani da Hadisi da kuma Ijma'in malamai.
- ✓ Haramun ne sauraran gulma, wajibi ne a faɗakar da wanda aka ji yana gulma, in kuma ba za a iya hanashi ba; wajibi ne a ƙyamaci abin a zuci kuma abar majalisin.
- ✓ Duk mai gulma ya sani cewa yana jawowa kansa fushin Allah ne da kuma azabarsa. Kuma ana ɗebe masa ladan ayyukansa ana bawa wanda yake gulmar tasa.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: "kar ɗayanku ya yi gulmar ɗayanku…"[1]
- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce "Kada sashinku ya yi gulmar sashi, ku zama yan uwa abokan juna"[2]
- ✓ Aliyu ɗan Hussaini ya kasance yana cewa: "Na haneku da yin gulma domin ita abincin Karnukaa ce"
- ✓ Gulma tana halatta a gurare kamar haka:
    - Wajen shugaba domin kawar da zalincinsa a kan talakawa ko kuma jawowa talakawa wani amfani.
    - Wajen bayar da sheda a kan mutum domin bayyana halayensa ga wanda zai ƙulla kasuwanci ko auratayya ko kuma wata mu'amala ta Shari'a in an buƙaci hakan.
    - Haka, wajen bayanin wanda yake bayyana saɓo don a ƙaurace masa amma in yana aikata saɓon a ɓoye; bai halatta a bayyana ba.

---

[1] Suratul Hujurati, aya ta 12

[2] Abu Isa Muhammad ibn Isa at-Tirmizi "Sunan at-Tirmizi" (1935)

- Wajen siffanta wanda ba za a gane shi ba sai da wannan siffar kamar Makaho ko Kuturu da makamantansu mutuƙar ba a ƙudurce ƙasƙantar da su ba.

## وَالنَّمِيمَةُ

*"Da yin annamimanci"*

- ✓ Ɗaukar zance daga guri zuwa wani gurin daban da niyyar ɓata tsakani shi ne Annamimanci.
- ✓ Tona asirin wata magana, ko wani sirri da wani ya mintar da kai shi ma Annamimanci ne.
- ✓ Shi yasa wani mai hikima yake cewa: "Kada ka rinƙa kai-komo da zance tsakanin masoya biyu na ɓatanci, hakan na kaiwa ga raba tsakaninsu ko kuma haifar da ƙiyayya"[1]
- ✓ Irin wannan ɗabi'a a ce a Musulunci kuma haramun ce a cikin Kur'ani da Sunna da kuma Ijma'in Mmalamai.
- ✓ Cikin suratu Kalam aya ta 10-11 da Suratul Humaza aya ta 1 da kuma suratul Masad aya ta 4-5 Allah Maɗaukakin sarki ya yi mana bayanin illar annamimanci a cikinsu.
- ✓ Annabi Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: "Annamimi ba zai shiga Aljanna ba"
- ✓ Hanyoyin kuɓuta daga Annamimanci:
    - Karyata wanda ya kawo gulma domin shi fasiƙi ne ba a karɓar shedarsa.
    - Ka hana shi ta hanyar yi masa nasiha.
    - Ka kyamace shi saboda ya saɓawa Allah.
    - Kada ka yi mummunan zato a kan wanda aka kawo maka Annamimancinsa.

[1] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", Shafi na (41)

- Kar ya bi diddigin ɗan'uwansa kana bin da aka faɗa a kansa.
- Kar ya ɗorar da maganar da Annamimi ya gaya masa.

## وَالْكِبْرُ وَالْعُجْبُ

*"Ɗa girman kai da kuma da jijji da kai"*

- ✓ Ma'anarsa: Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce "Girman kai shi ne ƙin karɓar gaskiya da kuma wulaƙanta mutane.
- ✓ Ayoyi da yawa da Hadisai da kuma kalaman magabata sun yi bayanai a kan illolin girman kai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya ce: "Haƙiƙa waɗanda suke yin girman kai game da bautata da sannu za su shiga jahannama a wulaƙance"[1]
- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Ba zai shiga Aljanna ba duk wanda ya kasance akwai kwatankwacin ƙwayar koma na girman kai a zuciyarsa…"[2]
- ✓ Sayyidina Abubakar Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Kar ɗayanku ya wulaƙanta wani cikin Musulmi; ƙarami cikin musulmi babba ne a wurin Allah Maɗaukakin sarki"[3]
- ✓ Muhammad ɗan Hussaini ɗan Ali ya ce: "Girman kai bai taɓa shiga zuciyar wani ba face sai ya samu tawaya a cikin hankalinsa, gwargwadon yawansa ko ƙanƙantarsa"[4]
- ✓ Sababan girman kai:
    - Girman kai da ji kafi kowa sanadiyyar wani ilim da kake da shi ko kuma wani aikin Ibada da kake yi.
    - Girmama kai saboda dangi ko ƙarfi ko dukiya ko kuma kyawu ko yawan mabiya.
- ✓ Hanyoyin magance giraman kai:

---

[1] Suratul Ghafir, aya ta 60
[2] Muslim bn Hajjaj "Sahihu Muslim, babun haramta girman kai da kuma bayaninsa", (91)
[3] Aminuddini Abubakar "Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat", Shafi na 185
[4] Hassan Ayyub "As-Sulukul Ijtima'i", shafi na 50

- Ka yi nazari a kan asalin halittarka.
- Ka zama mai koyi da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.
- Ka shagaltu da yi wa kanka hisabi.

## وَالرِّيَاءُ

*"Ɗa yi don a gani (riya)"*

- ✓ Na nufin aikata wata ibada don mutane su gani.
- ✓ Irin wannan ɗabi'ar haramun ce a kan baligi bisa koyarwar Kur'ani da Hadisai da kuma Ijima'in Malamai
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya tsorata da mutane dangane da illar da take cikin riya kama yadda yazo a cikin suratun Nisa'i aya ta 142 da Suratul Ma'un aya ta 4-7 da kuma Suratul Baƙara 264.
- ✓ Annabi tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi y ace: "Haƙiƙa mafi girman abin da nafi ji muku tsoro shi ne ƙaramar shirka:" Sai Sahabbai suka ce: Mecece ƙaramar shirka? Sai Annabi ya ce: "Ita ce riya"[1]
- ✓ Wani Hadisi daban mai tsoratarwa, Ma'aiki ya yi bayani dangane da yadda Riya take lalata aikin bawa da kuma yadda take kai shi zuwa ga wuta in da ya ce *"Haƙiƙa farkon waɗanda za a yankewa hukunci a ranar ƙiyama sune:*

  *Wanda ya yi shahada, za a zo da shi gaban Ubangiji, sai ya yi masa bayanin baiwar da ya ba shi, bawa sai ya tabbar da haka. Ubangii sai ya ce masa "me ka aikata da wannan baiwar da na yi maka" Sai ya ce: Na yi yaƙi domin ɗaukaka kalmarka har na yi shada. Ubangiji sai ya ce masa: "Karya kake, Ka yi yaƙi ne domin a ce kai jarumi ne, kuma an faɗa" Ubangiji sai ya yi umarni a tura shi wuta ta fuskarsa.*

---

[1] Ahmad ɗan Hanbali "Musnad Ahmad", (23680)

*Sai kuma wanda Allah ya ba shi Ilimi, ya koyar da shi kuma ya karanta Kur'ani, bayan an zo da shi, sai ubangiji ya bayyana masa irin baiwar da ya yi masa. Shi kuma ya tabbatar da hakan. Sai Ubangiji ya ce masa: "Me ka yi da ita?" Sai ya ce: Na koyi ilimi kuma na koyar da shi kuma na karanta Kur'an saboda kai. Ubangiji sai ya ce: "Karya kake, ka koyi Ilimi ne don a ce kai Malami ne. Ka karanta Kur'ani don a ce kai makaranci ne kuma an faɗa" Ubangiji sai ya yi umarni a tura shi wuta ta fuskarsa.*

*Sai kuma wanda Allah ya yalwata masa cikin arikinsa, ya ba shi dangogin dukiya gabaɗayanta. Sai a zo da shi gaban Ubangiji, sai ya yi masa bayanin baiwar da ya yi masa, sai ya tabbatar da ita. Sai Ubangiji ya ce: "Me ka aikata da ita" Sai ya ce: babu wata hanya da kake so a ciyar da dukiya face sai da na ciyar da ita ta wannan hanyar. Sai Ubangiji ya ce masa "Karya kake yi, kawai ka ciyar ne domin a ce kai mai kyauta ne kuma an faɗa" Ubangiji sai ya yi umarni a tura shi wuta ta fuskarsa.*[1]

*Sai Ma'aiki ya bugi gwiwar Abu Huraira ya ce masa: "Waɗannan mutane guda uku su ne farkon waɗanda za a kunna wuta da su"*[2]

- ✓ Sayyadina Aliyu Allah ya ƙara masa yadda ya ce: Mai riya yana da alamomi guda uku:
  - Kasala a lokacin ibada a yayin da yake shi kaɗai.
  - Yin ibada cikin walwala da nishaɗi in yana cikin Jama'a.
  - Yana ƙara kyautata ibadarsa idan ya samu yabon mutane. Haka yana daina shi idan an zarge shi.
- ✓ Fudailu ɗan Iyad ya ce: Barin aikata wani aiki na ibada saobda mutane; Riya ce. Aikata wani aiki saboda mutane; shirkace. Iklasi shi ne Allah ya yaye maka cututtukan guda biyu.

---

[1] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (1905).

[2] Abu Isa Muhammad ibn Isa at-Tirmizi "Sunan at-Tirmizi" (2383)

- ✓ Abubuwan da suke jawowa a afka cikin Riya:
  - Son yabo.
  - Gudun zargi
  - Kwaɗayin abin hannun mutane
- ✓ Ba da labarin wani aiki na alheri da ka aikata domin mutane su yaba maka kuma su girmamaka.

## وَالسُّمْعَةُ

*"Da jiyarwa"*

- ✓ Jiyarwa na nufin baligi ya aikata wani aiki saboda Allah sa'annan daga baya yazo yana gayawa mutane domin neman wata girmamawa daga gare su.
- ✓ Irin wannan ɗabi'ar haramun ce a kan baligi kuma tana sabbaba kunyata a ranar Kiyama.
- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Duk wanda ya jiyar Allah zai kunyata shi ranar ƙiyama…"[1]
- ✓ Idan ya kasance yana ibadar a ɓoye sai Allah ya bayyanata ga wani, sanadiyyar haka sai ya ji daɗi, wannan ba riya ba ce kuma ba jiyarwa ba ne. Haka wanda aka yaba masa sanadiyyar wani aikin alheri da ya aikata.
- ✓ An tambayi Ma'aiki dangane da wani mutum da yake aikin alheri, sai mutane suke yaba masa akai? Sai Ma'aikin Allah y ace musu: "Wannan albishir ne na gaggawa ga mumini" (kafin babban albishir a ranar ƙiyama).

## وَالْحَسَدُ

*"Da Hassada"*

- ✓ Hassada na nufin burin gushewar wata ni'ima daga wani ba tare da dalili na shari'a ba.

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (6499)

- ✓ Irin wannan ɗabi’ar Haramun ce a kan baligi bisa koyarwar Kur’ani da Hadisai da kuma Ijima’in Malamai.
- ✓ Ita Hassada sifa ce daga cikin siffofin kafirai da munafukai da masu raunin Imani.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya tsorata da mutane dangane da illar da take cikin Hassada kamar yadda yazo a cikin suratun Nasi aya ta 1-5 da Suratu Ali-Imrana aya ta 120 da kuma Suratul Baƙara 109.
- ✓ Annabi tsira da Aminci Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Kar ku yi gaba a tsakaninku, kar ku yi Hassada a tsakaninku, kar ku juyawa Yan'uwanku baya. Kuma zama bayin Allah Yan uwan juna. Baya halatta ga musulmi ya ƙauracewa ɗan'uwansa sama da kwana uku”[1]
- ✓ Muhammad ɗan Sirin ya ce: “Ban taɓa yi wa wani hassada ba a kan abin duniya. In ɗan'aljanna ne ta ya ya zan yi masa hassada domin, Aljanna zai shiga. In kuwa ɗan'wuta ne ta ya ya zan yi masa hassada da wani abin duniya bayan makomarsa wuta zai tafi”[2]
- ✓ Hassada ko dai ta zama cikin abin duniya kamar dukiya ko wani matsayi ko karɓuwa a cikin mutane ko kyawun halitta da sauransu.
- ✓ Akwai wani nau’i da ya yi kama da hassada, amma kuma ba hassada ba ce. Wato burin samun wata ni’ima da wani yake da it aba tare da burin gushewar ta wancan ba, ana kiran irin wannan da “Gibɗa”.
- ✓ Sannan akwai “Munafasa” wato bawa ya yi ta aiki don ya taradda wani da yake gabansa, ko kuma ya wuce shi cikin wasu ayyuka na alheri. Irin wannan Allah ya kwaɗaitar a kansa cikin suratul Muɗaffifina, aya ta 26.

[1] Muhammad ibn Isma’il al-Bukhari “Sahih al-Bukhari” (401)
[2] Ibnu Kudama “Minhajul Kasidina”, shafi na (185)

## وَالْبُغْضُ

*"Da Kiyayya"*

- ✓ Kiyayya na nufin ka tsani ɗan'uwanka muslmi ba tare da dalili na shari'a ba. Wajibi ne a kan baligi ya zama mai kuɓutaccen ƙirji dangane da ɗan'uwansa muslmi.
- ✓ Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyan cewa su muminai yan'uwa ne[1], kamar yadda a wani gurin ya bayyana cewa su muminai masu ƙanƙan da kai ne ga muminai kuma masu nuna isa ga kafirai ne[2]
- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Ana buɗe ƙofofin Aljanna ranar Litinin da Alhamis, ana gafartwa kowana bawa musulmi wanda baya sanyawa Allah kishiya sai dai fa mutumin da yake gaba da ɗan'uwansa, sai a ce ku jinkirta masu har sai sun shirya, ku jinkirta masu har sai sun shirya"[3]

## وَرُؤْيَةُ الْفَضْلِ عَلَى الْغَيْرِ

*"Da kuma ganin fifiko a kan wani"*

- ✓ Haramun ne ga baligi ya rinƙa ji a zuciyarsa yafi sauran mutane domin wannan yana daga cikin nau'h na girman kai da kuma tsarkake kai kuma Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: "Kar ku tsarkake kawunanku…"[4]
- ✓ Imamu Shafi'i yana cewa: "Duk wanda ya kai kansa wani matsayi sama da nasa sai Allah zai rago shi zuwa matsayinsa"[5]
- ✓ Sheikh Jilani yana cewa: "Duk wanda ya ba wa kansa wata tsarkaka; shi ba tsarkakke bane"[6]

---

[1] Suratul Hujurati, aya ta 10
[2] Suratul Ma'ida, aya ta 54
[3] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (2565).
[4] Suratun Najmi, aya ta 32
[5] Muhammad Ahmad ar-Rashid "Al-Awa'iƙ", shafi na 48
[6] Shehu Abdulƙadir Jilani "Fat'hur Rabbani", shafi na 39

- ✓ Wajibi ne a kan Mumini ya rinƙa kallon kansa ƙasa da waninsa musamman a al'amuran lahira kamar ilimi da Jihadi da himma da ciyarwa don Allah da yawan Ibada.
- ✓ Wajibi na Mumini ya rinƙa kallon kansa a matsayin wanda ya gaja cikin dukkan al'amuran Ibada, haƙiƙa Allah ya siffanta masu yi masa irin ɗabi'un da suka gabata da cewa: "Su ne waɗanda suke aikata abin da aka ce su aikata amma zuciyarsu tana raurawa cewa su izuwa ga Ubangijinsu masu komawa"[1]

## وَالْهَمْزُ وَاللَّمْزُ

*"Da zunɗe da kuma yafuce izgili"*

- ✓ Haramu ne a kan baligi ya rinƙa aibata mutane ko ya ci mutncinsu a gabansu ko a bayan idonsu.
- ✓ Haka, haramun ne a kan baligi ya aibata mutane ta hanyar amfani da hannunsa ko harshensa ko idanunsa.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: "Azaba ta tabbata ga dukkan mai zunɗe da yafuce"[2]
- ✓ Zunɗe da yafuce suna daga cikin siffofin munafukai kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana hakan a cikin Suratut Tauba, aya ta 79.

## وَالْعَبَثُ

*"Da wasa (mara amfani a duniya da lahira)"*

- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: "Dukkan wani wasa da zai shagaltar da Mumini haramun ne, sai dai

---

[1] Suratul Mu'uminuna, aya ta 60
2 Suratul Humazati. Aya ta 1

guda uku, namiji ya yi wasa da matarsa ko wasan harbi[1] ko wasan guje-guje da Dawaki don koyar da su salon yaƙi"[2]

- ✓ Misalin wasanni da Shari'a ta ƙyamata sun haɗa da:
  - Wasa na Ludo da 'Chess' saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Duk wanda ya yi wasan Ludo haƙiƙa ya saɓi Allah da Manzonsa"[3]
  - Haka, wasan ƙwallon ƙafa
  - Shagala da hanyoyin dandalin sada zumunta kamar Facebook, WhatsApp da sauransu.
  - Haka, rawa da waƙa ز

## وَالسُّخْرِيَةُ

*"Da kuma Izgili"*

- ✓ Wulaƙanta mutane da ƙasƙantar da su da kuma binciko laifukansu da aibukansu domin mutane su yi masu dariya shi ake kira izgili.
- ✓ Ana iya yin izgili ta hanyar Magana ko nune.
- ✓ Duk waɗannan ɗabi'un haramun ne a kan baligi a bisa koyarwar Kur'ani da Hadisai da kuma Ijma'in malamai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya yi hani ga yin izgili ga wasu mutanen akan wasu mutanen, babu mamaki waɗanda ake yi wa izgilin sun fi masu yin izgilin alheri a wurin Allah[4]
- ✓ Izgili na daga cikin ɗabi'ar sheɗan kamar yadda Allah ya umarce shi da ya yi wa Annabi Adamu Sujjada amma ya ƙi, ta hanyar rainawa da kuma ƙasƙanta asalin abin da aka halacci Annabi Adamu da shi.[5]

---

[1] Da Kibiya ko da Mashi ko da Bindiga da makamantansu

[2] Imam Ahmad ɗan Hanbal "Musand Ahmad" (16886)

[3] Imam Ahmad ɗan Hanbal "Musand Ahmad" (19521) da Abu Dawud Sulaiman bn al-Ash'as "Sunan abi Dawud" (4938)

[4] Suratul Hujurati, aya ta 11

[5] Suratul Baƙara, aya ta 70-83

## وَالزِّنَا، وَالنَّظَرُ إِلَى الأَجْنَبِيَّةِ، وَالتَّلَذُّذُ بِكَلاَمِهَا

*"Zina da kallon matar da ta haramta ka kalla da kuma jin daɗin zancenta"*

- ✓ Zina na nufin baligi ya kusanci matar da ba ta halatta a gare shi ba ta hanyar aure ko bauta ba.
- ✓ Zina haramun ce a ciki ƙur'ani da Hadisi da kuma Ijma'in Malamai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana cewa "Kar ku kusanci zina, lallai lamarin da sha'anin ya kasance mummunan laifi ne, kuma mummunan tafarki ne"[1]
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Mai zina ba ya aikata alhalin yana mumini…"
- ✓ Kamar yadda aka harmata zina, haka aka haramta Luwaɗi da Maɗigo da biyan sha'awa ta wasu hanyoyin saboda gamewar faɗinsa Maɗaukakin sarki dan gane da muminai "Kuma su ne waɗanda suke kiyaye farjinsu, sai dai a kan matansu, ko kuma bayinsu, irin waɗannan ba ababan zargi bane. Duk wanda ya nemi (biyan buƙatar sha'awarsa) koma ba ya waɗannan to wannan sune masu ƙetare iyaka "[2]
- ✓ Kallo da Hira da kuma alƙawarin haɗuwa su ne manyan jigo da suke kai baligi ga aikata zina. Don haka shari'a ta haramtawa baligi kallon mace da kuma hira da ita domin jin daɗin maganarta, hakan su ne matakai na afkawa cikin zina.

## وَأَكْلُ أَمْوَالِ النَّاسِ بِغَيْرِ طِيبِ نَفْسٍ

*"Da cin dukiyar mutane ba tare da son ransu ba"*

- ✓ Wannan ya haɗar da cin dukiyar mutane ta hanyar ƙwace, damfara, Caca, zalunci, bokanci, cin hanci da rashawa, tilastawa, kuɗin alfasha gabaɗayansu cin dukiya ne ba tare da haƙƙi ba.

---

[1] Suratul Isar'I, aya ta 32

[2] Suratul Ma'arji, aya ta 29-31

- ✓ Irin waɗannan ɗabi'un haramun ne a kan baligi bisa koyarwar Kur'ani da Hadisai da kuma Ijima'in Malamai.

## وَالأَكْلُ بِالشَّفَاعَةِ أَوْ بِالدِّينِ

*"Da ci da sunan Addini"*

- ✓ Siffantuwa da addini domin karɓar wani abu a hannun mutane ko ƙarawa mutum abin da bai cancanta ba da sunan addini ko kuma rage masa.
- ✓ Imamu Gazali ya ce: "In samu kuɗi ta hanyar kiɗa da waƙa shi yafi mini sauƙi a kan na ci ta hanyar siffantuwa da Addini"
- ✓ Malik ɗan Dinar ya ce: "Na tambayi Hassan, mene ne uƙubar Malami idan ya zama mai son duniya?" sai ya ce: "Mutuwar Zuciya, idan ya ƙaunaci duniya; zai neme ta da ayyukan Lahira, a wannan lokacin albarkar Ilimi sai ta gushe daga gare shi, sai siffarsa kawai"[1]
- ✓ Fudailu ɗan Iyad ya ce: "In nemi duniya da ganga da garaya shi yafi soyuwa a gare ni a kan in neme ta da siffar addini"[2] Haka Bishir al-Hafi ya yi kwatankwancin wannan maganar[3]

## وَالأَكْلُ بِالشَّفَاعَةِ

*"Da ci da ceto"*

- ✓ Samawa mutum mafita a wajen wani shugaba ta hanyar karɓar wani abu daga hannunsa, ko da sun yi yarjejeniyar abin da za a bayar ko ba a yi ba.
- ✓ Ma'aiki tsira da maincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Duk wanda ya samawa wani mafita, sai ya ba shi wata kyauta kuma ya karɓeta; haƙiƙa ya buɗe wata babbar ƙofa daga ciki ƙofofin riba"[4]

---

[1] Ibnul Juazi "At-Tabsira", shafi na 367
[2] Ibnul Jauzi "Sifatus Safwa" 2/562
[3] Ibnu Kudama "Mukhtasaru Minhajil Kasidina", shafi na 214
[4] Abu Dawud Sulaiman bn al-Ash'as "Sunan abi Dawud" (3541)

- ✓ Ci da ceto yana shiga cikin wata kyauta da aka ba wa ma'aikacin da ake biyansa kan wannan aikin. Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata gare shi yana cewa: "Duk wanda muka ba shi wani aiki kuma yanka masa albashi a kan wannan aikin, duk abin da ya karɓa bayan wannan haramun ne"[1]
- ✓ Haƙƙin ne a kan masulmi ya samawa ɗan'uwansa masulmi mafita ba tare da ya karɓi wani abu a wajensa ba kamar yadda Ubangiji Maɗaukakin sarki ya bayyana a cikin suratun Nisa'i aya ta 85.

## وَتَأْخِيرُ الصَّلاَةِ عَنْ أَوْقَاتِهَا

*"Jinkirta Sallah a kan lokacinta"*

- ✓ Barin sallah har lokacinta na laruri ya fita ba tare da uzuri na shari'a ba.
- ✓ Ko shakka babu duk baligin da ya jinkirta Sallah har lokacin ya fita haƙiƙa ya aikata mafi munin saɓo.
- ✓ Duk wanda ya mutu yana mai wasa da Sallah, ba ya kula da lokutanta Allah ya yi masa alƙawarin wani kwari a cikin Jahannama kamar Sa'idu ɗan Musayyib ya faɗa.

## وَلاَ يَحِلُّ لَهُ صُحْبَةُ فاسِقٍ، وَلاَ مُجَالَسَتُهُ لِغَيْرِ ضَرُورَةٍ

*"Ba ya halatta a gare shi: ya yi abota da fasiƙi ko kuma zama da shi sai in da lalura"*

- ✓ Fasiƙanci na nufin bijirewa dokokin Ubangiji ta hanyar aikata abubuwan da ya haramta da kuma hanuwa ga abubuwan da ya halatta.
- ✓ Ba ya halatta ga baligi ya riƙi Fasiƙi a matsayin aboki ko kuma zama da shi sai da wani uzuri, kamar zaman mota, zaman asibiti, kasuwa.
- ✓ Zama da fasiƙi yana jawo naso na ɗabi'unsa.

---

[1] Abu Dawud Sulaiman bn al-Ash'as "Sunan abi Dawud" (2943)

- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Lokacin da zuriyar Isra’ila (Banu Isra'il), suka afka cikin saɓo, malamansu sun tsawatar da su, amma suka ƙi hanuwa. Sai (Malaman) suka cigaba da zama da su, suna ci tare, kuma suna Sha. Sanadiyyar haka Allah ya toshe zukatansu a tsakaninsu kuma ya tsine masu a bisa harshen Annabi Dawud da Isa ɗan Maryam, sakamakon bijirewarsu da kuma ƙetare iyaka”.
- ✓ Ya kuma sake bayyana mana a cikin wani Hadisin daban: “Mutum yana tare da ɗabi’un masoyinsa, ɗayanku ya zaɓi wanda zai yi abota da shi”
- ✓ Abota da nagartattun mutane yana da fa’idoji, daga cikinsu:
    - Ilimi da kuma aiki da shi
    - Taimako wajen yi wa Allah biyayya.
    - Fa’idantuwa da kuma taimakekeniya a rayuwar duniya.
    - Duk soyayyar da ba a ƙullata saboda Allah ba; za ta zama ƙiyayya ranar Kiyama.

**وَلاَ يَطْلُبُ رِضَا الْمَخْلُوقِينَ بِسَخَطِ اَلْخَالِقِ، قَالَ اللهُ سُبْحَانَهُ وَتَعَالَى: {وَاللهُ وَرَسُولُهُ أَحَقُّ أَنْ يُرْضُوهُ إِنْ كَانُوا مُؤْمِنِينَ}. وَقَالَ عَلَيْهِ الصَّلاَةُ وَالسَّلاَمُ: «لاَ طَاعَةَ لِمَخْلُوقٍ فِي مَعْصِيَّةِ الْخَالِقِ».**

*“Kar ya nemi yardar wani abin halitta cikin saɓawa Mahalicci, domin Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: “Allah da Manzonsa su kaɗai suka fi cancanta da a nemi yardarsu in kun kasance ku muminai ne” Manzon Allah ya ce: “ba bu biyayya ga abin halitta cikin saɓa wa mahalicci”””*

- ✓ Wato kar baligi ya nemi yardar wani abin halitta ta hanyar bin son zuciyarsu da kuma buƙatunsu saboda kwaɗayin abin da yake hannunsu cikin al’amarin da yake wajabta fushin Allah.
- ✓ Yana da kyau baligi ya sani, neman yardar mutane bindiga ce a ruwa ba ta saɓuwa.

- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: "Duk wanda ya nemi yardar Allah ta hanyar fusata mutane; Allah zai isar masa ƙiyayyar mutane. Duk wanda ya nemi yardar mutane ta hanyar saɓon Allah; Allah zai bar al'amuransa zuwa ga mutane (Ba zai samu yardar su ba)"[1]

**وَلاَ يَحِلُّ لَهُ أَنْ يَفْعَلَ فِعْلاً حَتَّى يَعْلَمَ حُكْمَ اللهِّ فِيهِ وَيَسْأَلَ الْعُلَمَاءَ وَيَقْتَدِيَ بِالْمُتَّبِعِينَ لِسُنَّةِ مُحَمَّدٍ صَلَّى اللهُّ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ**

*"Ba ya halatta ga baligi ya aikata kowanne irin aiki har sai ya san hukuncin Allah a cikinsa. Kuma ya tambayi Malamai, kuma ya yi koyi ga masu bin Sunnar Annabinmu, mai cetonmu wato waɗanda suke shiryarwa a kan biyayyar Allah kuma suke tsoratarwa a kan bin hanyar Shaiɗan"*

- ✓ Wannan ƙa'ida ce mai girman gaske a cikin addinin Masulunci saboda farkon abin da ya sauka ga Ma'aiki shi ne umarnin karatu.
- ✓ Ilimi a dunƙule a Masulunci yana da babbar falala musamman ilimin sanin Allah da kuma Ma'aiki, da kuma ilimin shari'a.
- ✓ Bisa wannan tubali; wajibi ne ga baligi kar ya furta ko ya aikata wani aiki har sai ya san hukuncin Allah a cikinsa.
- ✓ Masulunci ya bayyana fifikon wanda yake da ili a kan wanda ba shi da shi.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Neman Ilim tilas ne a kan kowane Masulmi"
- ✓ Dole ne a kan baligi ya tambayi malamai (waɗanda suke koyi da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, kuma suke shiryar da mutane zuwa ga biyyaya ga Allah, suke tsawatarwa daga bin shaiɗan da kungiyarsa) a kan abubuwan da suka shige masa duhu.

[1] Abu Isa Muhammad ibn Isa at-Tirmizi "Sunan at-Tirmizi" (2414)

- ✓ Da haka ne baligi zai kyautata aƙidarsa da kuma addininsa, ya rayu a kan tsarin magabata nagari.

وَلاَ يَرْضَى لِنَفْسِهِ مَا رَضِيَهُ الْمُفْلِسُونَ الَّذِينَ ضَاعَتْ أَعْمَارُهُمْ فِي غَيْرِ طَاعَةِ اللهِّ تَعَالَى، فَيَا حَسْرَتَهُمْ وَيَا طُولَ بُكَائِهِمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ،

*"Kuma kar ya amince wa kansa irin abin da mara arziki[1] suka amincewa kansu. Waɗannan su ne waɗanda suka tozartar da rayuwarsu cikin saɓawa Allah. Mamakin asararsu, mamakin tsahon kukansu ranar gobe ƙiyama"*

- ✓ Ba ya halatta ga baligi ya amincewa kansa abin da masu saɓo suka amincewa kansu ba. Domin su gajiyayyu ne a karan-kansu kasancewar suna zunubi ba sa neman gafara. Suna laifuka ba sa tuba. Waɗannan su ne matsiyata a duniya da kuma lahira.
- ✓ Mara arziki shi ne wanda zai zo ranar Alƙiyama da karɓaɓɓiyar Sallah da Azumi da kuma Zakka, amma sai a same shi ya zagi wancan, ya yi wa wani ƙazafi, ya ci dukiyar wani, ya zubar da jini wani, ya daki wancan, sai a ɗebe kyawawan ayyukansa a ba wa waɗanda ya zalunta, idan kyawun ayyukansa suka ƙare; sai a ɗebo mummunan ayyukansu a lafta masa.[2]
- ✓ Mafiya munin asara su ne waɗanda suka yi asarar addininsu. Tabbas kukansu zai tsawaita, naƙin ciki zai mamayesu lokacin fitar ransu. Azaba da ƙunci na Kabari za su abokancesu. Wulaƙanci da Azaba za su haɗu da su ranar Alƙiyama.

---

[1] Waɗanda za a yiwa gwanjon ayyukansu na alheri a ranar ƙiyama
[2] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (15)

نَسْأَلُ اللهَّ أَنْ يُوَفِّقنَا لاِتِّبَاعِ سُنَّةِ نَبِيِّنَا وَشَفِيعِنَا وَسَيِّدِنَا مُحَمَّدٍ صَلَّى اللهَّ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ.

*"Muna roƙon Allah ya datar damu wajen bin Sunnar Annabinmu, mai cetonmu, kuma shugabanmu tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi"*

- ✓ Malam ya kammala wannan bangaran da roƙon dacen Allah, da kuma ko yi da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, domin daga nan dukkan wani hukunce-hukunce na Ibada da kuma Mu'amala suke bayyana.
- ✓ Cikin biyayya da kuma ko yi da Annabi ne aka samu kuɓuta da kuma shiriya, duk wanda ya nemi shirya koma bayan wannan haƙiƙa ya ɓata.

## TSARKI

**اَلطَّهَارَةُ قِسْمَانِ: طَهَارَةُ حَدَثٍ، وَطَهَارَةُ خَبَثٍ، وَلاَ يَصِحُّ الْجَمِيعُ إلاَّ بِالْمَاءِ الطَّاهِرِ الْمُطَهِّرِ، وَهُوَ الَّذِي لَمْ يَتَغَيَّرْ لَوْنُهُ أَوْ طَعْمُهُ أَوْ رَائِحَتُهُ بِمَا يُفَارِقُهُ غَالِبًا كَالزَّيْتِ وَالسَّمْنِ وَالدَّسَمِ كُلِّهِ وَالْوَدَحِ وَالصَّابُونِ وَالْوَسَخِ وَنَحْوِهِ، وَلاَ بَأْسَ بِالتُّرَابِ وَالْحَمْأَةِ وَالسَّبَخَةِ وَالآجُرِّ وَنَحْوِهِ.**

*"Tsarki ya rabu zuwa tsarkin kari da kuma tsarkin dauɗa. Dukkansu ba sa inganta sai da ruwa mai tsarki, kuma mai tsarkakewa, wato shi ne ruwan da launinsa bai canza ba, ko ɗanɗanonsa ko ƙamshinsa da abin da zai rinjaye shi kamar Mai da Kakide da Kitse dukkaninsa, da ruwan dauɗa da Sabulu da Dauɗa da makamancinsa. Babu laifi ga turɓaya da baƙar ƙasa da ƙasar kanwa da jan algaruf da makamncinsa"*

- ✓ Tsarki na nufin gusar da abin da yake haramta Sallah na kari ko najasa ta hanyar amfani da ruwa ko turɓaya ko jima.

- ✓ Ana amfani da ruwa domin kawar da kari da kuma najasa. Ana amfani da turɓaya wajen yin Taimama, jima domin tsarkake fatar matacciyar dabba.
- ✓ An fara gabatar da Magana akan tsarki domin shi (tsarki) sharaɗi ne na ingancin sallah, sharaɗi kuwa abin gabatarwa ne kafin Sallah.
- ✓ Tsarki wajibi ne a cikin Kur'ani da Sunna da kuma Ijma'in malamai.
- ✓ Allaha Maɗaukakin sarki yana cewa:
  - "Kuma in kun kasance kuna halin Janaba; ku yi tsarki"[1]
  - "Lallai Ubangiji yana son masu yawan tuba, kuma yana son masu yawan tsarkaka"[2]
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:
  - "Tsarki shi ne mabuɗin Sallah…"[3]
  - "Allah ba ya karɓar sallar ɗayanku idan ya yi kari har sai ya sake alwala"[4]
  - "Tsarki ɓangare ne na Imani"[5]
- ✓ Tsarki yana rabuwa zuwa:
  - Tsaarki na ɓoye: wato tsarkakuwa daga shirka da kuma dukkanin dangin saɓo, tare da cututtukan zuciya ta hanyar tuba na gaskiya.
  - Tsarki na bayyane: ko dai ya zama ƙaramin kari (Fitsari, bayan gida, Tusa, Maziyyi, Wadiyyi, yawun Kare) wanda alwala zata iya gusar da shi ko kuma ya zama babban kari wanda sai an yi wanka (Kamar Janaba, Al'ada, Biƙi).
- ✓ Tsarki wajibi ne a kan dukkan wanda Sallah ta wajaba a kansa bisa wasu daga cikin sharuɗa masu zuwa:
  - Masulunci,

---

[1] Suratul Ma'ida, aya ta 6
[2] Suratul Baƙara, aya ta 222
[3] Abu Isa Muhammad ibn Isa at-Tirmizi "Sunan at-Tirmizi" (3)
[4] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (6954)
[5] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (534)

- Balaga,
- Hankali,
- Ɗaukewar jinni al'ada ko na biƙi,
- Shigar lokacin Sallah.

✓ Tsarki ba ya inganta sai da ruwa mai tsarki kuma mai tsarkakewa, sai dai in an rasa ruwa a irin wannan yanayin sai Taimama ta wakilci ruwan.

✓ Ruwa mai tsarki kuma mai tsarkakewa shi ne ruwan da yake da tsarki a kansa kuma yake tsarkake waninsa. Wato sakakken ruwan da bai canza daga asalinsa ba, kamar ruwan Kogi ko na Korama ko na Rijiya ko Idon ruwa ko Ruwan sama da sauransu.

✓ Ruwa yana jirkita sanadiyyar cakuɗarsa da abu mai tsarki kamar Mai ko ruwan tatar Koko irin wannan ruwa ne mai tsarki, amma ba ya tsarkakewa, za a iya amfani da shi a ayyukan yau da kullum amma ba za a yi amfani da shi a ayyukan Ibada ba.

✓ Idan ruwa ya jirkita da abin da yake gudana a kansa, kamar ruwan teku (da yake da ɗanɗanon gishir ko kanwa), ko kuma abin da ya haifu a cikin ruwan (kamar gansakuka), ko kuma ya jirkita a kan ƙasar da yake gudana, (Kamar jar ƙasa ko farar ƙasa mai kama da ruwan madara ko kuma baƙar ƙasa) irin wannan ruwan babu komai za a yi amfani da shi a ayyukan yau da kullum da kuma na ibada.

✓ Ruwan da ya jirkita da Najasa (Fitsari, bayan gida, Jini); shi ma najasa ne, ba ya halatta a yi amfani da shi a wajen ayyukan yau da kullum ko kuma ayyukan ibada.

✓ Idan ruwan bai jirkita ba sanadiyyar cakuɗuwarsa da Najasarba; babu laifi za a iya amfani da shi a cikin ayyukan yau da kullum da kuma ayyyukan Ibada (Idan ba a samu waninsa ba).

**فَصْلٌ: إِذَا تَعَيَّنَتِ النَّجَاسَةُ غُسِلَ مَحَلُّهَا، فَإِنِ الْتَبَسَتْ غُسِلَ الثَّوْبُ كُلُّهُ. وَمَنْ شَكَّ فِي إِصَابَةِ النَّجَاسَةِ نَضَحَ، وَإِنْ أَصَابَهُ شَيْءٌ شَكَّ فِي نَجَاسَتِهِ فَلاَ نَضْحَ عَلَيْهِ**

*"Idan najasa ta bayyana sai a wanke gurbinta. Idan ba a gane haƙiƙanin in da ta taɓa ba; sai a wanke tufa gabaɗaya. Wanda ya yi kokwantan samuwar najasa; sai ya yi yayyafi. Idan wani abu ya taɓa tufafinsa sai yake kokwantan najasa ne ko ba najasa ba ne; babu komai a kansa"*

- ✓ Idan najasa ta samu tufafi a bigiren da aka gani wajibi ne a wanke iyaka gurin in najasar ba ta daga cikin waɗanda aka yi rangwame a kansu.
- ✓ Najasar da aka yi rangwame a kanta ita ce: Kwata, ruwan da ya kwanta a hanya, caɓi, jini ɗan kaɗan (wanda bai wuce faɗin ƙwandala ba), mai yoyon fitsari da sauransu.
- ✓ Idan najasar da aka yi rangwame a kanta ta taɓa jiki ko tufafi, ba a gusar da ita kuma ba a wanketa.
- ✓ Najasar da ba a yi rangwame a kanta ba idan ta bayyana wajibi ne a gusar da ita. Idan ba a tabbatar da gurin da najasar ta shafa ba wajibi ne a wanke tufar gabaɗaya.
- ✓ Idan Najasa ta samu tufafi kuma gusar da ita ya yi wahala har lokaci ya rage abin da bai fi a sallaci raka'a ɗaya ba; wajibi ne Ka yi sallarka da najasar, barin sallar saɓo ne babba.
- ✓ Idan gurbin najasar kuwa bai bayyana ba tare da yaƙinin samuwar najasar; wajibi ne a wanke tufafi gabaɗaya, in har akwai wadataccen lokaci.
- ✓ Wanda ya yi fitsari bayan ya yi fitsarin sai kokwanto ya kama shi, shin fitsari ne ya ɗiga a tufafinsa ko kuma ruwan tsarki ne? irin wannan zai yi yayyafi ne a jikin tufafinsa, in kuwa ya bar yayyafin bai yi ba; zai sake Sallarsa.
- ✓ Shi yayyafa ruwa a gurbin Najasar da ake shakka a kanta yana sanyawa zuciya nutsuwa, yana kore shaiɗan kuma yana yanke wasuwasi.

وَمَنْ تَذَكَّرَ اَلنَّجَاسَةَ وَهُوَ فِي الصَّلاَةِ قطَعَ إلاَّ أنْ يَخَافَ خُرُوجَ الْوَقْتِ. وَمَنْ صَلَّى بِهَا نَاسِيًا وَتَذَكَّرَ بَعْدَ السَّلاَمِ أعَادَ فِي الْوَقْتِ.

*"Wanda ya tuna wata najasa alhalin yana Sallah; sai ya yanke sallar sai dai in ya ji tsoron fitar lokaci. Wanda ya yi sallah da najasa a bisa mantuwa kuma ya tuna bayan ya yi sallama; sai ya sake Sallar in lokacinta bai fita ba"*

- ✓ Idan mai sallah ya yi kokonton samuwar najasa a jikin tufafinsa; zai yi yayyafi a gurin da ya yi kokwanton samuwarsa. Idan abu ya taɓa tufafin baligi sai yake tunanin najasa ce ko ba najasa b ace; babu komai a kansa.
- ✓ Idan ka fara Sallah sa'annan ka tuna kana da najasa a jikinka; sai ka yanke sallar.
- ✓ Idan ka yi sallar da ita kana mai mantuwa baka tuna ba sai bayan sallama; ka sake sallar in lokacin bai fita ba.
- ✓ Lokacin sallah yana da matuƙar muhimmanci ga masallaci, shi yasa aka yi rangwame da ya kamala sallarsa ga wanda ya tuna najasa yana cikin sallah kuma ya tsoraci fitar lokaci in ya ce zai yanke ya gusar da najasar.

## FARILLAN ALWALA

**فَرَائِضُ الْوُضُوءِ سَبْعٌ: اَلنِّيَّةُ، وَغَسْلُ الْوَجْهِ، وَغَسْلُ الْيَدَيْنِ إِلَى الْمِرْفَقَيْنِ، وَمَسْحُ الرَّأسِ، وَغَسْلُ الرِّجْلَيْنِ إِلَى الْكَعْبَيْنِ، وَالدَّلْكُ، وَالْفَوْرُ.**

*"Farillan Alwala guda bakwai ne: Niyya da Wanke fuska da Wanke hannaye zuwa gwiwar hannu da shafar kai, da wanke ƙafafuwa izuwa idon sawu, da cuccuɗa gaɓoɓi, da kuma gaggautawa"*

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani a kan tsarki da yadda ya rabu sai kuma ya ƙulla fasali a kan farillan alwala.
- ✓ Farilla ita ce abin da babu makawa sai mutum ya aikata.
- ✓ Alwala na nufin wanke wasu gaɓoɓi, da kuma shafar wasu da niyyar ɗauke kari.
- ✓ Farillan guda bakwai ne a bisa mazahabin Imamu Malik, huɗu daga cikunsu (Wanke fuska da wanke hannaye zuwa gwiwar hannu da shafar kai da kuma wanke ƙafafuwa) duk malaman Fiƙhu sun yarda da su, domin nassin Alƙur'ani su ya ambata kai-tsaye a cikin Suratul Ma'ida aya ta 6. Ragowar ukun (Niyya da Cuccuɗawa da kuma gaggautawa) kuma an yi saɓani a kansu.
- ✓ Alwala wajibi ce a Kur'ani da Hadisai da kuma Ijma'in malamai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki yana faɗa cikin littafinsa: "Ya ku waɗanda suka yi Imai! Idan za ku yi Sallah to ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa gwiwar hannu kuma ku shafi kunnuwanku da Kafafunku zuwa idon sahu…."[1]
- ✓ Mai'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Allah ba ya karɓar sallar ɗayanku idan ya yi kari har sai ya sake alwala"[2]
- ✓ Alwala tana da falaloli masu yawa daga cikinsu:
  - Allah yana shafewa mai Alwala zunubansa.
  - Alwala tana ɗaukaka darajojin bawa a ranar Kiyama.

---

[1] Suratul Ma'ida, aya ta 6
[2] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (135)

- Alwala tana sanya hasken fuska da kuma na ƙafafuwa da hannaye ranar Alƙiyama.

✓ Sharuɗan alwala:
- Hankali
- Balaga
- Masulunci
- Daukewar jinin al'ada da na biƙi.
- Shigar lokaci daukewar kari
- Samun wadataccen ruwa da kuma ikon amfani da shi.
- Shigar lokaci ga wanda zai yi taimama.

✓ NIYYA na nufin ƙudurce wani abu a zuciya, ba lallai sai an furta ba. Niyya wajiba ce saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: "Kaɗai dai ladan ayyuka suna tabbata ne da niyyar da aka aikata su"[1]

✓ WANKE FUSKA: Daga farkon goshi zuwa ƙarshen muƙamiƙi a tsaye, faɗinta daga kunnen dama zuwa kunnen hagu. Wanke fuska farilla ne saboda faɗinsa Maɗaukakin Sarki a cikin Ma'ida, aya ta 6: "…Kuma ku wanke fuskokinku…"

✓ WANKE HANNAYE IZUWA GWIWAR HANNU: wato daga farkon yan'yatsu zuwa gwiwar hannu. Allah Maɗaukakin Sarki a cikin Ma'ida, aya ta 6 yana cewa: "…Ku wanke hannayenku zuwa gwiwar hannu…"

✓ SHAFAR KAI: Yana nufin shafa gashin kai da ruwa daga farkon matsirar gashin goshi zuwa ƙarshen ƙeya. Shafar kai farilla ne, saboda faɗinsa Maɗaukakin sarki a cikin Ma'ida, aya ta 6: "… kuma ku shafi kawukanku…"

✓ WANKE KAFAFU ZUWA IDON SAWU: Wato wanke ƙafafuwa gabaɗaya har zuwa farkon ƙauri. Ita ma farilla ce saboda faɗinsa Maɗaukain sarki a cikin Ma'ida, aya ta 6: "…Kuma ku wanke ƙafafunku"

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (54)

- ✓ Wajibi ne a kan mai alwala ya bibiyi digadigansa sosai, domin ya tabbatar ko'ina ruwa ya taɓa saboda yazo cikin faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Azabar wuta ta tabbata ga diga-digai"[1]
- ✓ CUCCUƊAWA: Ana nufin wanke gaɓoɓin alwala da kyau.
- ✓ GAGGAUTAWA: Ana nufin fara Alwala har gamawa ba tare da yankewa ba.

## SUNNONIN ALWALA

**غَسْلُ الْيَدَيْنِ إِلَى الْكُوعَيْنِ عِنْدَ الشُّرُوعِ، وَالْمَضْمَضَةُ، وَالِاسْتِنْشَاقُ، وَالِاسْتِنْثَارُ، وَرَدُّ مَسْحِ الرَّأْسِ وَمَسْحُ اَلْأُذُنَيْنِ وَتَجْدِيدُ الْمَاءِ لَهُمَا، وَالتَّرْتِيبُ بَيْنَ الْفَرَائِضِ.**

*"Wanke tafin hannu zuwa wuyan hannu lokacin fara Alwala, da Kuskurar baki, da shaƙar ruwa, da facewa, da dawo da shafar kai, da shafar fatun kunnuwa, da sabunta ruwa a garesu, da kuma Jeranta farillai"*

- ✓ Ma'anar Sunna a gurin Malaman Fiƙhu shin ne aikin da Ma'aiki ya dawwama a kansa tare da dalilan da suke nuna ba farilla ba ne ba.
- ✓ Wanke tafin hannu yana daga cikin sunna musamman idan mutum ya tashi daga barci saboda faɗin ma'aiki da yake cewa: "Idan ɗayanku ya farka daga barci kar ya sanya ya dulmiya hannunsa a cikin masaki har sai ya wanke sau uku domin bai san a ina hannayensa suka kwana ba"
- ✓ Kuskurar baki na nufin guntsar ruwa da kuskurar baki da shi, a kamfata uku.
- ✓ Zuba ruwa a hanci ta hanyar amfani da iska mai ƙarfi wajen shaƙar, sai dai in kana azumi, sai ka shaƙa a hankali.
- ✓ Fitar da ruwan daga cikin hanci ta hanyar amfani da iska mai ƙarfi shi ake kira da facewa.
- ✓ Dawo da hannye daga ƙeya zuwa farkon goshi, na daga cikin sunnonin alwala.

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (60)

- ✓ Sanya yanyatsun nuni a cikin ƙofar kunne da jujjuyasu tare da tsetstsefe su, ciki da wajen fatun kunnuwa shi ake da kira da shafar fatun kunne.
- ✓ Sake taɓa ruwa domin shafar kunne.
- ✓ Yana daga cikin sunnar alwala a jeranta farilla kamar yadda suka zo a cikin ayar Alwala da kuma koyarwar ma'aiki.

**وَمَنْ نَسِيَ فَرْضًا مِنْ أَعْضَائِهِ فَإِنْ تَذَكَّرَهُ بِالْقُرْبِ فَعَلَهُ وَمَا بَعْدَهُ، وَإِنْ طَالَ فَعَلَهُ وَحْدَهُ وَأَعَادَ مَا صَلَّى قَبْلَهُ.**

*"Wanda ya manta wata farilla a cikin gaɓoɓin alwala, in ya tuna a kusa sai ya wanketa da abin da ya biyo bayanta. Idan kuma ya tsawaita sai ya wanke gaɓar ita kaɗai sa'annan ya sake Sallah"*

- ✓ Wanda ya manta wanke wata gaɓa da take farilla ce daga cikin gaɓoɓin alwala idan ya tuna kafin ragowar gaɓoɓin su bushe, sai ya wanketa kuma an so ya wanke gaɓoɓin da suka biyo bayanta, domin jerantawa yana daga cikin sunnonin alwala.
- ✓ In kuwa mantuwar ta yi tsayi, har gaɓobi suka bushe; sai ya wanke gaɓar ita kaɗai da niyyar cika alwalarsa ba sai ya zo da abin da yake gaba ba, kuma zai sake sallar da ya yi, domin alwalarsa ba ingatacciya ba ce kamar yadda Khalil yake cewa: "Duk wanda ya bar wata farilla; zai zo da ita da kuma abin da ya sallata"[1]

**وَإِنْ تَرَكَ سُنَّةً فَعَلَهَا وَلاَ يُعِيدُ الصَّلاَةَ**

*"Idan ya bar wata Sunna zai aikata ta, amma ba zai sake sallah ba"*

- ✓ Wanda ya bar wata Sunna zai zo da ita ne kawai, ko da kuwa ya kammala alwalarsa kuma gaɓoɓinsa sun bushe, kuma ba zai sake sallarsa ba domin Sallarsa ingantacciya ce[2]
- ✓ Ana gyara Sunnar da aka bari ne saboda sallolin da za su zo a gaba.

---

[1] Khalilu bn Ishaƙ al-Maliki "Mukhtasarul Khalil", shafi na (20)
[2] Imamu Malik ɗan Anas "Al-Mudawwanatul Kubra", 1/95

وَمَنْ نَسِيَ لُمْعَةً غَسَلَهَا وَحْدَهَا بِنِيَّةٍ وَإِنْ صَلَّى قَبْلَ ذَلِكَ أَعَادَ.

*"Wanda ya manta wata lam'a; zai wanketa ita kaɗai tare da niyya, in kuwa ya yi Sallah kafin lokacin sai ya sake"*

- ✓ Wanda ya wanke wata gaɓa daga cikin gaɓoɓin Alwala amma kuma ruwa bai game wani guri ɗan kaɗan ba, ko mai yawa; za a wanke wannan gurin shi kaɗai tare da niyya.
- ✓ Ana sake sallar da aka bar lam'a a gaɓoɓin farilla, domin sallar bata yiwu ba[1]

وَمَنْ تَذَكَّرَ الْمَضْمَضَةَ وَالِاسْتِنْشَاقَ بَعْدَ أَنْ شَرَعَ فِي الْوَجْهِ فَلاَ يَرْجِعُ إِلَيْهِمَا حَتَّى يُتِمَّ وُضُوءَهُ

*"Wanda ya manta kuskurar baki da kuma shaƙa ruwa a hanci har ya fara wanke fuska sannan ya tuna; ba zai dawo gare su ba har sai ya kamala alwalarsa"*

- ✓ Wanda ya fara wanke gaɓar da take farilla ce ba zai dawo zuwa ga abin da yake sunna ba ne.

## MUSTAHABBAN ALWALA

التَّسْمِيَةُ وَالسِّوَاكُ وَالزَّائِدُ عَلَى الْغَسْلَةِ الأولَى فِي الْوَجْهِ وَالْيَدَيْنِ، وَالْبُدَاءَةُ بِمُقَدِّمِ الرَّأسِ، وَتَرْتِيبُ السُّنَنِ وَقِلَّةُ الْمَاءِ عَلَى الْعُضْوِ، وَتَقْدِيمُ الْيُمْنَى عَلَى الْيُسْرَى. وَيَجِبُ تَخْلِيلُ أَصَابِعِ الرِّجْلَيْنِ، وَيَجِبُ تَخْلِيلُ اللِّحْيَةِ الْخَفِيفَةِ فِي الْوُضُوءِ دُونَ الْكَثِيفَةِ، وَيَجِبُ تَخْلِيلُهَا فِي الْغُسْلِ وَلَوْ كَانَتْ كَثِيفَةً.

*"Mustahabbai: Bisimillah da yin asuwaki, da ƙarin wanke fuska da hannu a kan na farko, da Fara wanke fuska ta goshi da Jeranta sunnoni da Karanta ruwa akan gaɓɓan alwala da Fara wanke ɓangaran dama kafin na hagu da*

---

[1] Muhammad bn Muhammad al-Maliki "Mawahibul Jalil", 1/225

*Tsattsefe yatsun ƙafa da Tsattsefe gemun da ba shi da yawa a lokacin alwala, da kuma mai yawa a lokacin wanka"*

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani a kan sunnoni alwala sai ya shiga bayanai a kan abubuwan da ake so mai alwala ya aikata.
- ✓ Malam bai kawo adadin  Mustabban alwala ba saboda saɓanin Malamai a kan adadin, kowa da yadda ya ƙididdige su.
- ✓ Mustahabbi na nufin wani aikin da yake bai kai farilla ko Sunna ba amma kuma aikata shi akwai lada.
- ✓ Mustahabbi shi ne abin da Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya aikata sau ɗaya ko sau biyu ko kuma wani abu da ya yi umarni amma ba a rawaito ya aikata ba.[1]
- ✓ Yin Bismillah lokacin fara alwala saboda Hadisin Ma'aiki da yake cewa: "…Babu cikakken ladan alwala ga wanda bai ambaci sunan Allah ba (a yayin fara alwala)"
- ✓ Yin Aswaki wato cuccuɗa haƙori da wani ita ce ko yan yatsu ko kuma "brush". Yana da kyau ya fara Asuwaki kafin kuskurar baki saboda faɗinsa tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi: "Ba don kar na tsanantawa al'ummta ba; da na umarce da yin asuwaki yayin kowace alwala"
- ✓ Karin wanke fuska da hannu a kan na farko wato bayan wanki na farko ƙaro na da na uku na daga cikin ababan da ake so a alwala.
- ✓ Fara wanke fuska ta goshi ka faro ta ƙarshen matsirar gashi, wato sama goshi zuwa ƙasa.
- ✓ Jeranta sunnoni yana daga cikin abubuwan da ake so a alwala a jeranta Sunnoni kamar yadda suka zo a cikin ayar alwala da kuma koyarwar Ma'aiki.

---

[1] Abu Muhammad Badruddini Muhammad "Al-Bahrul Muhiɗu", 1/284

- ✓ Karanta ruwa a kan gaɓoɓin alwala yin amfani da mafi ƙarancin ruwan da zai ishi mutum wanke gaɓɓan alwala.
- ✓ Fara wanke ɓangaran dama kafin na hagu kasancewar Ma'aiki yana burgeshi fara yin komai da dama.
- ✓ Tsattsefe yatsun ƙafa wato sanya yan yatsu da kuma cuccuɗa tsakankanin yan yatsun ƙafa.
- ✓ Tsefe gemun da ba shi da yawa a lokacin alwala, da kuma mai yawa a lokacin wanka wato wanda ba shi da yawan gashi a haɓarsa abin so ne ya cuccuɗa gemunsa.

## ABUƁUWAN DA SUKE WARWARE ALWALA

**نَوَاقِضُ الْوُضُوءِ أَحْدَاثٌ وَأَسْبَابٌ: فَالأَحْدَاثُ: الْبَوْلُ وَالْغَائِطُ وَالرِّيحُ وَالْمَذْيُ وَالْوَدْيُ.**

*"Abubuwan da suke warware alwala akwai karrai da sababai: Karrai: Fitsari da bayan gida daTusa da Maziyyi da kuma Wadiyyi"*

- ✓ Wasu abubuwane idan suka faru ga wanda yake da Alwala to alwalarsa ta warware.
- ✓ Abubuwan da suke warware alwala sun kasu gida biyu:
- ✓ Karrai (abubuwan da suke fitowa ta ɗayan hanyoyi biyu, ko dai ta gaba ko kuma ta baya) da kuma sababai (abubuwan da ba daga jikin mutum suke fitowa ba amma kuma samuwar ɗaya daga cikinsu yana warware alwala).
- ✓ Karrai sune kamar haka: Fitsari, Bayan gida, Tusa, Maziyyi, Wadiyyi
    - Fitsari da bayan gida suna wajabtawa baligi tsarki kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana a cikin Suratul Ma'ida, aya ta 6.

- Wani mutum daga “Hadaramaut” ya tambayi Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda), mene ne karrai? Sai ya ce: “iskar da take fita daga duburar mutum”[1]
- Wadiyyi da kuma Maziyyi ana yi masu tsarki ne kamar yadda Ma’aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya bayyana.
- Wadiyyi ruwa ne fari mai kauri da yake fitowa bayan kammala fitsari. Hukuncinsa kamar na fitsari ne, ba a wanke farji gabaɗayansa, kaɗai dai ana wanke in da ya fita ne kuma ba tare da ƙulla niyya ba.

*“Wajibi ne ya wanke gabansa gabaɗayansa saboda maziyyi, amma ba zai wanke marainansa ba”*

- ✓ Malam ya yi wata Magana wadda za ta iya haifar da tambaya kamar haka, shin wajibi ne wanke gabansa duka saboda fitar maziyyi ko kuma iyaka gurbin da maziyyin kaɗai ya taɓa za a wanke?
- ✓ Malamai sun yi saɓani akan hakan amma Malam mai Ahlari ya zaɓi wankewa gabaɗaya.

**وَالأَسْبَابُ: النَّوْمُ الثَّقِيلُ وَالإِغْمَاءُ وَالسُّكْرُ وَالْجُنُونُ**

*“Sababai su ne barci mai nauyi, da Shiɓan jiri(ko suma), da maye,da hauka”*

- ✓ Barci mai nauyi shi ne barcin da mutum zai iya yin tusa ba tare da ya sani ba saboda Hadisin Sayyidina Ali (Allah ya ƙara masa yadda) ya ce: Manzon Allah ya ce: “Ido shi ne maƙulli na tusa, duk wanda ya yi barci ya sake alwala”[2]
- ✓ Barci yana rabuwa zuwa:
  - Barci mai tsayi mai nauyi, irin wannan yana warware Alwala.
  - Gajere mai nauyi, shi ma yana warware Alwala.
  - Gajere mara nauyi, ba ya warware Alwala.

[1] Aminuddini Abubakar “Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat”, Shafi na 252
[2] Usman bn Sa’id ad-Darimi “Sunan ad-Darimi” 1/184

- Mai tsaho mara nauyi, an so a sake Alwala.

✓ Shiɓan jiri ko farfaɗiya wata cuta ce da take samuwa a cikin ƙoƙon kai ta hanyar ɗaukewar hankali. Imamu Malik ya kasance yana cewa: "Duk wanda farfaɗiya ko shiɓan jiri ya same shi; wajibi ne ya sake alwala"[1]

✓ Maye da hauka suna da cikin abubuwan da suke warware alwala kasancewarsu suna gusar da hankali. Malamai sun haɗu akan wajibcin sake alwala ga duk wanda ya haɗu da abubuwan da suka gabata.

وَالْقُبْلَةُ، وَلَمْسُ الْمَرْأَةِ إِنْ قَصدَ اللَّذَّةَ أَوْ وَجَدَهَا

*"Da Sumbata da shafar mace da nufin jin daɗi ko kuma samun jin daɗin ba tare da ya nufata ba"*

✓ Rungumar Mace da kuma tsotsar kuncinta ko kuma bakinta da niyyar jin daɗi na daga cikin abubuwan da suke warware alwala.

✓ Haka, wanda ya shafi jikin mace da nufin jin daɗi shi ma alwalarsa ta karye. Ya samu biyan buƙata ko bai samu ba.

✓ Shafar mace yana rabuwa zuwa:
  - Baligi idan ya yi nufin jin daɗi sanadiyyar shafar mace; Alwalarsa ta karye.
  - In kuma ya shafeta ba tare da niyyar jin daɗi ba amma ya samu jin daɗin; Alwalarsa ta warware.
  - Idan ya shafi Mace da nufin jin daɗi amma kuma bai samu ba; zai sake alwala.
  - Idan ya shafeta ba da nufin jin daɗin ba kuma bai samu ba; babu alwala a kansa.

وَمَسُّ الذَّكَرِ بِبَاطِنِ الْكَفِّ أَوْ بِبَاطِنِ الأَصَابِعِ

*"Da Shafar gaba da tafin hannu ko yan yatsu"*

---

[1] Salihu bn Abdus-Sami'I al-Abi "Hidatul Muta'abbidi as-Saliki", shafi na 18

- ✓ Duk wanda ya shafi farjinsa da cikin tafin hannunsa ko da cikin yan yatsunsa; alwalarsa ta warware. Saboda faɗinsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: "Idan ɗayanku ya shafi gabansa da tafin hannunsa babu wata sitira; lallai wajibi ne a kansa ya sake alwala"[1]
  Haka Ma'aiki ya faɗa a wani Hadisin "Duk wanda ya shafi farjinsa kar ya sake ya yi Sallah har sai ya sake Alwala"[2]

**وَمَنْ شَكَّ فِي حَدَثٍ وَجَبَ عَلَيْهِ الْوُضُوءُ إلاَّ أَنْ يَكُونَ مُوَسْوَسًا فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ**

*"Wanda ya yi kokonta cikin samuwar kari; Alwala ta wajaba a kansa, sai dai in mai yawan kokonto ne babu komai a kansa"*

- ✓ Shakka cikin samuwar Kari na daga cikin abubuwa da suke wajabta sake Alwala sai dai in kokwanto ya Auri mutum (Mutum mai yawana Shakka) to babu komai akansa.

**وَيَجِبُ عَلَيْهِ غَسْلُ الذَّكَرِ كُلِّهِ مِنَ الْمَذْيِ، وَلاَ يَغْسِلُ الأُنْثَيَيْنِ. وَالْمَذْيُ هُوَ الْمَاءُ الْخَارِجُ عِنْدَ الشَّهْوَةِ الصُّغْرَى بِتَفَكُّرٍ أَوْ نَظَرٍ أَوْ غَيْرِهِ.**

*"Yana wajaba a kansa ya wanke gabansa gabaɗaya saboda fitar Maziyyi amma ba zai wanke marainansa ba. Maziyyi wani ruwa ne da yake fitowa yayin ƙaramar sha'awa ta hanyar tunani ko kallo ko waninsu"*

- ✓ Wajibi ne a wanke farji gabaɗayansa saboda fitar Maziyyi.
- ✓ Maziyyi wani tsainkakken ruwa ne, fari mai santsi da yake fitowa yayin ƙaramar sha'awa, ko kuma tuntuntuni ko waninsu.
- ✓ Ba a wanke maraina sakamakon fitar Maziyyi.
- ✓ Wajibi ne yin niyya yayin wankewar.

---

[1] Abul Kasim Sulaiman ib Ahmad "Al'Mu'ujamul Ausad", (1850)
[2] Abu Dawud Sulaiman ibn al-Ash'ath "Sunan abi Dawud" (181)

**لاَ يَحِلُّ لِغَيْرِ الْمُتَوَضِّئِ صَلاَةٌ وَلاَ طَوَافٌ**

*"Abubuwan da basu halatta ba ga wanda ba shi da Alwala: Sallah da Ɗawafi"*

- ✓ Sallah kowace iri ba ta halatta ga wanda ba shi da Alwala. Aya ta 6 cikin suratul Ma'ida ta tabbatar da haka.
- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Allah baya karɓar Sallah ba tare da Alwala ba…"
- ✓ Ɗawafi Ibada ce da Allah ya shar'anta ga mai aikin Hajji ko Umra. Ba ta halatta a gabatar da ita ba tare da Alwala ba, saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "ɗawafi kamar Sallah ce, sai dai Allah ya halatta magana a cikinsa. Duk wanda zai furta wata Magana ya tabbatar ta alheri ce"

**لاَ يَحِلُّ لِغَيْرِ الْمُتَوَضِّئِ صَلاَةٌ وَلاَ طَوَافٌ وَلاَ مَسُّ نُسْخَةِ الْقُرْآنِ الْعَظِيمِ وَلاَ جِلْدِهَا، لاَ بِيَدِهِ وَلاَ بِعُودٍ وَنَحْوِهِ إِلاَّ الْجُزْءَ مِنْهَا الْمُتَعَلَّمَ فِيهِ، وَلاَ مَسُّ لَوْحِ الْقُرْآنِ الْعَظِيمِ عَلَى غَيْرِ الْوُضُوءِ إِلاَّ لِمُتَعَلِّمٍ فِيهِ أَوْ مُعَلِّمٍ يُصَحِّحُهُ وَالصَّبِيُّ فِي مَسِّ الْقُرْآنِ كَالْكَبِيرِ, وَالإِثْمُ عَلَى مُنَاوِلِهِ لَهُ،**

*"Bai halatta ya shafi Al-Kur'ani mai girma ba ko gafakarsa da hannunsa ko da sanda ko makamancinsa sai dai juzi'i, shi ma sai ga ɗalibi. Bai halatta ya sahfi allon Kur'ani b aba tare da Alwala ba sai ga ɗalibin Kur'ani ko Malamin da yake koyar da shi don zai inganta shi. Yaro dangane da shafar Kur'ani kamar babba ne wajen zunubi sai dai zunubin yana hawa kan wanda ya saka shi"*

- ✓ Ba ya dacewa ga wanda ba shi da Alwala ya taɓa Kur'ani.
- ✓ Babu laifi ga malamin da yake koyar da shi.
- ✓ Haka, babu laifi a kan ɗalibin da yake koyon Kur'ani.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi y ace: "Kar ka shafi Kur'ani sai kana mai tsarki"

- ✓ Ba ya kamata ga yaro ya taɓa Alƙu'ani ba tare da Alwala ba. In kuwa ya taɓa; zunubunsa na kan wanda ya saka shi ko kuma yana kallonsa bai hana shi ba.

**وَمَنْ صَلَّى بِغَيْرِ وُضُوءٍ عَامِدًا فَهُوَ كَافِرٌ وَالْعِيَاذُ بِاللهِّ**

*"Wanda ya yi gangancin yin Sallah ba tare da Alwala ba; tabbas ya kafurta. Allah ya tsare mu"*

- ✓ Tsarki wajibi ne a Sallah kamar yadda Kur'ani da Hadisai da kuma Ijam'in Malamai ya nuna.
- ✓ Bisa waɗannan dalilan duk wanda ya yi sallah ba tare da Alwala ba; lalle ya halatta abin da Allah ya haramta.
- ✓ Duk wanda ya aikata haka kuwa, tabbas ya kafirta.

## WANKA DA HUKUNCE-HUKUNCENSA

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani a kan ƙaramin tsarki, yanzu kuma zai yi bayani dangane da babban tsarki da kuma abubuwan da suke wajabta wanka.
- ✓ Wanka na nufin game jiki da ruwa da cuccuɗawa tare da niyyar ɗauke babban kari domin yin ibada.

**يَجِبُ الْغُسْلُ مِنْ ثَلاَثَةِ أَشْيَاءَ: اَلْجَنَابَةِ وَالْحَيْضِ وَالنِّفَاسِ**

*"Wanka yana wajaba saboda abubuwa uku: Janaba da Haila da kuma biƙi"*

- ✓ Wanka wajibi ne a kan baligi da ayoyin Kur'ani da Hadisai da kuma ijma'in malamai.
- ✓ Allah Maɗaukakin sarki ya yi maganar wankan jnaba a cikin suratul Ma'ida aya ta 6, kamar yadda aya ta 222 a cikin suratul Baƙara ta yi Magana akan hukuncin wankan jinin al'ada.
- ✓ Janaba wata sifa ce da take hana baligi yin Ibadar da aka sharɗanta mata yin babban tsarki kamar Sallah da ɗawafi da sauransu.

**فَالْجَنَابَةُ قِسْمَانِ: أَحَدُهُمَا خُرُوجُ الْمَنِيِّ بِلَذَّةٍ مُعْتَادَةٍ فِي نَوْمٍ أَوْ يَقَظَةٍ بِجِمَاعٍ أَوْ غَيْرِهِ. وَالثَّانِي: مَغِيبُ الْحَشَفَةِ فِي الْفَرْجِ**

*"Ita janaba ta kasu gida biyu: Fitar Maniyyi a bisa jin daɗi na al'ada a cikin barci ko a farke ko ta hanyar saduwa ko waninsa da kuma ɓoyuwar gaba a cikin farji"*

- ✓ Maniyyi wani farin ruwa ne mai kauri, wanda yake ingizar juna da yake fita lokacin babbar sha'awa.
- ✓ Fitar maniyyi a lokacin mafarki da wanda ya sadu da iyalinsa da wanda ya kalli wata mace har maniyyi ya fito, da kuma wanda ya yi amfani da kowace irin hanya ta jin daɗi ya fitar da shi irin haka shi yake wajabta wanka.
- ✓ Idan kuwa ya fita ba tare da jin daɗi ba kamar wanda kunama ta harbe shi sai maniyyi ya fito, ko ya yi amfani da ruwa mai zafi sosai ko mai sanyi sosai sanadiyyar haka maniyyi ya fita irin wannan babu wanka a kan sa, alwala kaɗai ta wadatar.[1]
- ✓ Ɓacewar kan kaciya cikin farji yana wajabta wanka ko da kuwa maniyyi bai fita ba. Saboda Hadisin Nana A'isha (Allah ya ƙara mata yadda) take cewa: Manzona Allah ya ce: "Idan mutum ya zauna a kan turakun mace guda huɗu kuma ya wahalar da ita; wanka ya wajana ko kuwa Maniyyi bai fita ba"
- ✓ Annabi tsira da amincin Alla su tabbata a gare shi yana cewa: "Idan kaciya ta haɗu da kaciya, kuma kan kaciya ya ɓuya a cikin farji wanka ya wajaba"

**وَمَنْ رَأَى فِي مَنَامِهِ كَأَنَّهُ يُجَامِعُ وَلَمْ يَخْرُجْ مِنْهُ مَنِيٌّ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ، وَمَنْ وَجَدَ فِي ثَوْبِهِ مَنِيًّا يَابِسًا لاَ يَدْرِي مَتَى أَصَابَهُ اغْتَسَلَ وَأَعَادَ مَا صَلَّى مِنْ آخِرِ نَوْمَةٍ نَامَهَا فِيهِ**

*"Duk wanda ya yi mafarki yana saduwa da mace amma babu wani abu da ya fita daga gabansa; babu komai a kansa. Wanda yaga busasshen Maniyyi a*

[1] Muhammad bn Muhammad as-Shanƙiɗi "Manhul Ali fi sharhi kitabul akhdari", shafi na 153

*tufansa amma bai san yaushe ya same shi ba; ya yi wanka kuma ya sake sallar da ya yi bayan ƙarshen barcinsa"*

- ✓ Wanda ya yi mafarki ba ya fita daga ɗaya da cikin halaye masu zuwa:
  - Wanda yana barci ya yi mafarki kamar yana yin Jima'i kuma ya farka yaga maniyyi a jikinsa; wajibi ne ya yi wanka.
  - Wanda yana barci ya yi mafarki kamar yana yin Jima'i kuma ya farka bai ga maniyyi ya fita daga jikinsa ba; babu wanka akansa.
  - Wanda ya maniyyi ya fita a cikin barci ba tare da ya yi mafarki ba; wajibi ne ya yi wanka.

## FARILLAN WANKA

**فَرَائِضُ الْغُسْلِ: النِّيَّةُ عِنْدَ الشُّرُوعِ وَالْفَوْرُ وَالدَّلْكُ وَالْعُمُومُ.**

*"Farillan wanka: Niyya yayin fara wankan, da gaggautawa da cuccuɗawa, da kuma game jiki da ruwa"*

Niyya yayin fara wankan,

- ✓ Kudurcewar zuciya wajen kawar da babban kari.
- ✓ Gurbin niyya a zuci yake, ba a bayyanawa da baka.
- ✓ Ana yin niyya ne domin bambance ayyukan ibada daga na al'ada.

Gaggautawa

- ✓ Ta hanyar kammala wankan a zama ɗaya ba tare da yankewa ba.
- ✓ Wasu malaman suka ce, hakan Sunna ce ba Farilla ba.

Cuccuɗawa

- ✓ Shafa ruwa a jiki tare da tabbatar da cewa ruwan ya game dukkan gaɓɓai.

Game jiki da ruwa

- ✓ Tabbatar da ruwa ya sadu da dukkan jiki.

## SUNNONIN WANKA

**غَسْلُ الْيَدَيْنِ إِلَى الْكُوعَيْنِ كَالْوُضُوءِ، وَالْمَضْمَضَةُ وَالاِسْتِنْشَاقُ وَالاِسْتِنْثَارُ، وَغَسْلُ صِمَاخِ الأُذُنِ وَهِيَ الثُّقْبَةُ الدَّاخِلَةُ فِي الرَّأْسِ. وَأَمَّا صَحْفَةُ الأُذُنِ فَيَجِبُ غَسْلُ ظَاهِرِهَا وَبَاطِنِهَا**

*"Wanke hannaye zuwa idon hannu kamar alwala da Kuskurar baki da Shaƙar ruwa da fyacewa, da kuma wanke fatun kunnuwa. Ita ce ƙofar da take shiga cikin Kai. Amma fatun kunnuwa wajibi ne shafar ciki da wajensu"*

- ✓ Malam ya kammala Sunnonin wanka da na Alwala. Wannan kuwa abu ne da babu ƙura ko kaɗan a kai saboda Hadisin Maimuna[1] da ta karɓo daga Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi, wanda idan zai yi wanka yana yin alwala irin ta sallah.

## MUSTAHABBAN WANKA

**الْبِدَايَةُ بِغَسْلِ النَّجَاسَةِ ثُمَّ الذَّكَرِ فَيَنْوِي عِنْدَهُ، ثُمَّ أَعْضَاءِ الْوُضُوءِ مَرَّةً مَرَّةً، ثُمَّ أَعْلَى جَسَدِهِ، وَتَثْلِيثُ غُسْلِ الرَّأْسِ، وَتَقْدِيمُ شِقِّ جَسَدِهِ الأَيْمَنِ، وَتَقْلِيلُ الْمَاءِ عَلَى الأَعْضَاءِ.**

*"Farawa da wanke najasa, sannan wanke gabansa tare da ƙulla niyya, wanke gaɓoɓin alwala sau ɗaiɗai. Ya wanko daga kansa zuwa ƙasa. Ya wanke kansa sau uku. Ya gabatar da wanke ɓarinsa na dama da kuma Karanta ruwa akan gaɓoɓi"*

- ✓ Fara gusar da Najasa tare da niyyar ɗauke babban kari na daga cikin mustahabban wanka.
- ✓ Sannan ya wanke farjinsa ta yadda ba zai buƙaci sake taɓa shi don kar alwalarsa ta warware.

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (276)

- ✓ Idan gurin yanka akwai ƙasa babu laifi ya jinkirta wanke ƙafarsa, ya ja gefe kaɗan sai ya wanke ƙafafunsa a ƙarshen wankansa.
- ✓ An so a tsattsefe gashin kai, idan yana da yawa domin ya tabbatar ruwa ya isa zuwa ga asalin fatar kansa.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana fara wanke tsagin kansa na dama sannan na hagu sannan ya ɗebi ruwa ya wanko tsakiyar kansa[1].
- ✓ Karanta ruwa yayin wanka yana daga cikin ladabi. Annabi tsira da amincin Allah ya kasance yana wanka da kwano guda da ƙari kaɗan. Yana alwala da babban kofin ruwa[2].

**وَمَنْ نَسِيَ لُمْعَةً أَوْ عُضْوًا مِنْ غُسْلِهِ بَادَرَ إِلَى غَسْلِهِ حِينَ تَذَكُّرِهِ وَلَوْ بَعْدَ شَهْرٍ، وَإِنْ أَخَّرَهُ بَعْدَ ذِكْرِهِ بَطَلَ غُسْلُهُ فَإِنْ كَانَ فِي أَعْضَاءِ الْوُضُوءِ وَصَادَفَهُ غَسْلُ الْوُضُوءِ أَجْزَأَهُ.**

*"Wanda duk ya manta wata lam'a ko gaɓa cikin wankansa; ya yi gaggawar wanketa da zarar ya tuna, ko da kuwa bayan wata guda ne, ya sake sallar da ya yi kafin shi. Idan ya jinkirta bayan tunawarsa wankansa ya ɓaci. Idan ya kasance a gaɓoɓin alwala ne sai ya haɗa da alwala; Ya isar masa"*

- ✓ Bayani ya gabata cewa game jiki da ruwan na daga cikin farillan wanka, a bisa haka, duk wanda ya bar lam'a ko wata gaɓa daga cikin gaɓoɓin wanka da gangan wankansa ya ɓaci.
- ✓ In kuwa bisa mantuwa ne; wajibi ne ya gaggauta wanke gurin da ya bari tare da ƙulla niyya.
- ✓ In ka jinkirta wankewa bayan ka tuna; wankan ya ɓaci. Dole a sake wankan gabaɗaya, da kuma sake salloli.
- ✓ In kuwa ya kasance cikin gaɓɓan Alwala sai ya sadar da shi da wanka wanka; wankan ya isar masa.

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (258)
[2] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (201)

- ✓ Abin da aka barin farilla shi ne wajabta sake wanka amma in ya kasance yana cikin sunnoni ko mustahabbai sai wanke shi saboda sallar gaba amma ba za a sake wanka ba.

لاَ يَحِلُّ لِلْجُنُبِ دُخُولُ الْمَسْجِدِ، وَلاَ قِرَاءَةُ الْقُرْآنِ إِلاَّ الآيَةَ وَنَحْوَهَا لِلتَّعَوُّذِ وَنَحْوِهِ.

*"Ba ya halatta ga mai janaba shiga masallaci ko karatun Kur'ani sai dai aya ɗaya ko makamancinta don neman tsari"*

- ✓ Baya halatta ga mai janaba ya shiga massalci don zama a ciki dai in da wani ƙwaƙƙwaran uzuri ko kuma wucewa zai yi saboda faɗinsa Maɗaukakin Sarki a cikin suratun Nisa'i aya ta 43.
- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Ba ya halatta shiga Masallaci ga mai janaba ko mai al'ada"[1]
- ✓ Sayyidina ali yake cewa: "Naga Ma'aiki ya yi Alwala sannan ya karanta wani abu daga Alƙur'ani sannan ya ce, haka ne lamarin da sha'anin ga wanda ba mai janaba ba"
- ✓ Imamul Bukhari da Imamuɗ Ɗabari da Ibnul Manzur da ibnu Hazam duk sun tafi akan halaccin karanta Alƙur'ani ga mai janaba; saboda Hadisin Nana A'isha da take cewa: "Annabi ya kasance yana ambaton Allah a cikin kowanne hali"[2]
- ✓ Abdullahi ɗan Ubay kasance yana karanta ayoyin da ya saba karantawa alhalin yana da janaba[3]

وَلاَ يَجُوزُ لِمَنْ لاَ يَقْدِرُ عَلَى الْمَاءِ الْبَارِدِ أَنْ يَأْتِيَ زَوْجَتَهُ حَتَّى يُعِدَّ الآلَةَ إِلاَّ أَنْ يَحْتَلِمَ، فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ

*"Ba ya halatta ga wanda ba zai iya amfani da ruwa mai sanyi ba ya kusanci iyalansa, sai dai in ya tanadi ruwa mai ɗumi amma in mafarki ya yi; babu komai a kansa"*

---

[1] Abu Dawud Sulaiman ibn al-Ash'ath "Sunan abi Dawud" (232)
[2] Muslim ɗan Hajjaj "Sahihu Muslim" (373)
[3] Muhammad Nasiruddin al-Albani "Irwa'ul galil", shafi na (244-245)

- ✓ Idan amfani da ruwan sanyi zai kai mutum ga halaka kuma bai samu na'urar da zai ɗumama ruwan ba; ba ya halatta ya sadu da iyalinsa domin hakan zai tilasta masa yin taimama. Ita kuwa taimama rangwame ce a shari'a ga mai uzuri, saduwa da iyali kuwa ba uzuri ba ne.
- ✓ Amma wanda ya yi mafarki; babu laifi ya yi taimama in yaji tsoron amfani da ruwa mai sanyi saboda samuwar rashin lafiya. Mafarki abu ne da yake zuwa ba tare da zaɓin mutum ba.

Tsokaci

- ✓ Wanka yana da siffa ta kamala da kuma siffa ta isarwa.
- ✓ Siffa ta isarwa shi ne game jiki da ruwa tare da niyya ta hanyar shiga kogi ko amfani da "shower" ko kuma kwararar ruwan daga bokiti ko buta kai tsaye tare da cuccuɗawa.
- ✓ Siffar kamala kuwa:
  - Sanya masakin a ɓangaran dama in ya zama buɗaɗɗe ne.
  - Ya ambaci sunan Allah.
  - Ya yi amfani da bigire mai tsarki.
  - Ya wanke tafukan hannunsa sau uku kafin ya sanya su a cikin masakin wankansa.
  - Sannan ya gusar da ƙazantar da take farjinsa da cinyoyinsa.
  - Ya ƙudurce ɗauke babban kari.
  - Ya sanya yan yatsunsa ya cuccuɗa kansa ta yadda ruwa zai ratsa ya kai ga asalin fatar kansa sau uku.
  - Ya gabatar da wanke ɓangaransa na dama sannan na hagu.

TAIMAMA

- ✓ Bayan ya kamala bayaninsa a kan tsarki na ruwa, kai tsaye sai ya shiga bayani a kan tsarki na ƙasa.
- ✓ Taimama ibada ce da ake amfani da ƙasa wajen shafar fuska da hannaye da niyyar halatta Sallah.
- ✓ An shar’anta yin taimama ne a lokacin da mutum ya kai matuƙa wajen neman ruwa amma bai samu ba. Ko kuma akwai ruwan amma ba zai iya amfani da shi ba saboda rashin lafiya ko kuma ƙaruwarta, ko kuma ruwan ba zai ishe shi ya yi amfani da shi ba kuma ya yi Ibada.
- ✓ Taimama wajibi ce a cikin Kur’ani da Hadisai da kuma Ijma’in Malamai.
- ✓ Allah Maɗaukakin Sarki ya halatta yin ta cikin suratun Nisa’i aya ta 43.
- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana cewa: “An sanya mini ƙasa gabaɗayanta wurin Sallah, da kuma tsarki, duk in da Sallah ta riski ɗaya daga cikin al’ummata a wurin abin tsarkinsa yake”
- ✓ Abu Zar Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Annabi yana cewa “Haƙiƙa ƙasa mai tsarki ce, kuma gurin tsarkin masulmi ce, ko da kuwa bai samu ruwa ba tsahon shekara goma…”
- ✓ Malamai sun haɗu gabaɗayansu a kan Taimama tana wakiltar Alwala da kuma wanka a cikin halin hali na musamman.
- ✓ Ita taimama rangwame ce aka yiwa masulmi da ya yi amfani da ƙasa wajen yin tsarki idan larurar hakan ta bijiro.
- ✓ Hakan yana daga cikin hikimar Ubangiji ta hanyar sanya ibadar taimama daga ƙasar da ɗan'adam yake kai-komo a kanta wacce ita ce asalin halittarsa.

وَيَتَيَمَّمُ الْمُسَافِرُ فِي غَيْرِ مَعْصِيَةٍ، وَالْمَرِيضُ لِفَرِيضَةٍ أَوْ نَافِلَةٍ

*“Kuma matafiyi zai yi taimama, a cikin tafiya da ba ta saɓon Allah bace. Kuma mara lafiya in zai yi Sallar farilla ko Nafila”*

- ✓ Tafiya ko rashin lafiya su ne sabuban da aka halattawa baligi yin taimama.

- ✓ Matafiyi zai yi taimama idan ya rasa ruwa, saboda Hadisin Imrana ɗan Hussaini, yake cewa mun kasance muna tare da Ma'aiki a halin tafiya, mutane suka yi Sallah, sai ga wani mutum a gefe bai yi Sallah tare da Jama'a ba. Sai Ma'aiki ya ce masa: "Me ya hanaka ka yi Sallah"? Sai ya ce masa: "Janaba ce ta sameni kuma babu ruwa". Sai Ma'aiki yace: "Ka yi amfani da ƙasa don za ta isar maka"[1]
- ✓ Haka mara lafiya in ba zai iya amfani da ruwa ba a halatta masa yin taimama saboda Hadisin Jabir da y ace: Muna cikin wata tafiya, sai Dutse ya faɗowa ɗayanmu ya fasa masa kai, kuma ya yi mafarki (bayan ya yi barci). Sai ya tambayi abokansa shin zan iya yin taimama. Sai suka ce, ba za ka yi ba, saboda za ka iya amfani da ruwa. Suka saka shi ya yi wanka sanadiyyar haka ya rasu. Bayan mun dawo sai muka ambata wa Ma'aiki abin da ya faru, sai ya ce: "Kaiconsu! Sun kashe (ɗan'uwansu), me yasa ba za su tambaya in basu sani ba domin maganin jahilci shi ne tambaya. Ya isar masa ya yi taimama, gurin da ya samu rauni kuma ya ɗaureshi da wani kyalle, sai ya yi shafa akai, ya wanke ragowar jikinsa"[2]

**وَيَتَيَمَّمُ الْحَاضِرُ الصَّحِيحُ لِلْفَرَائِضِ إِذَا خَافَ خُرُوجَ وَقْتِهَا. وَلاَ يَتَيَمَّمُ الْحَاضِرُ الصَّحِيحُ لِنَافِلَةٍ وَلاَ جُمُعَةٍ وَلاَ جِنَازَةٍ إِلاَّ إِذَا تَعَيَّنَتْ عَلَيْهِ الْجَنَازَةُ.**

*"Haka, wanda yake lafiyayye kuma mazaunin gida, zai iya yin taimama in ya tsoraci fitar lokaci. Wanda yake lafiyayye kuma mazaunin gida, ba zai yi taimama ba saboda sallar nafila ko Juma'a ko jana'iza (sai dai in ta wajaba a kansa)"*

Tsoron fitar lokaci ga wanda ya yanke ƙauna daga samun ruwa ba; Taimama tana halatta a gare shi.

---

[1] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (348)

[2] Abu Dawud Sulaiman ibn al-Ash'ath "Sunan abi Dawud" (232)

# FARILLAN TAIMAMA

**النِّيَّةُ وَالصَّعِيدُ الطَّاهِرُ، وَمَسْحُ الْوَجْهِ وَمَسْحُ الْيَدَيْنِ إِلَى الْكُوعَيْنِ، وَضَرْبَةُ الأَرْضِ الأُولَى وَالْفَوْرُ، وَدُخُولُ الْوَقْتِ وَاتِّصَالُهُ بِالصَّلاَةِ.**

*"Niyya da ƙasa mai tsarki da shafar fuska da shafar hannaye izuwa idon hannu da kuma bugun ƙasa na farko da gaggautawa da Sshigar lokaci da kuma Sadar da Taimamar da Sallah"*

Niyya

- ✓ Himmatuwar zuciya wajen halatta sallah ga wanda bai samu ruwa ba ko ba akwai ruwan amma ba zai iya amfani da shi ba sakamakon rashin lafiya ko hunturu.
- ✓ Ba zai yi niyyar ɗauke kari da taimama ba domin Taimama ba ta ɗauke kari kaɗai dai tana halatta sallah ne ya yin buƙata domin waklilyar alwala ce ko wanka.

Kasa mai tsarki

- ✓ Dukkan bigiran da ya bayyana a bayan ƙasa kuma ya kuɓuta daga samuwar najasa a wurin saboda faɗinsa Maɗaukakin Sarki a cikin suratun Nisa'i aya ta 43.

Shafar fuska da Shafar hannaye zuwa idon hannu, da kuma bugun ƙasa na farko

- ✓ Wajibi ne mai taimama ya shafi fuskarsa gabaɗaya daga sama zuwa ƙarshen muƙamiƙi da geffan kunnuwansa, saboda faɗin Allah a cikin suratun Nisa'i aya ta 43.
- ✓ Haka Hadisin Ammar (Allah ya ƙara masa yadda) da yake cewa Janaba ta same shi amma bai samu ruwa ba, sai ya yi birgima a cikin ƙasa, ya yi Salla. Daga ya bawa Ma'aiki labarin abin da ya aikata. Ma'aiki sai y ace masa: "Da ka aikata da ya wadatar maka, Ma'aiki ya daki da hannayensa ya hure su, ya shafi fuskarsa da hannayensa"

Gaggautawa

- ✓ Gabatar da ita lokaci guda ba tare da yankewa ba.

Shigar lokaci

- ✓ Ba a yin taimama sai lokacin sallar da za a gabatar ya shiga.

Sadar da taimamar da Sallah

- ✓ Wajibi ne ana kamala taimama a shiga Sallah kai tsaye.

وَالصَّعِيدُ هُوَ التُّرَابُ وَالطُّوبُ، وَالْحَجَرُ، وَالثَّلْجُ وَالْخَضْخَاضُ وَنَحْوُ ذَلِكَ

*"Ƙasa mai tsarki: ya haɗa da tubali da dutse da ƙanƙara da faƙo da makamantansu"*

- ✓ Duk waɗannan ana amfani da su wajen yin taimama saboda faɗinsa Maɗaukakin sarki cikin sutarun Nisa'I aya ta 4. Da kuma Hidisn Abu Umama da ya gabata.

وَلاَ يَجُوزُ بِالْجِصِّ اَلْمَطْبُوخ وَالْحَصِيرِ وَالْخَشَبِ وَالْحَشِيش وَنَحْوِهِ،

*"Ba ya halatta a yi taimama da dafaffan siminti, da tabaramar kaba, da katako da ciyawa da makamantansu"*

- ✓ Duk abin da ɗan'adam ya sarrafasu daga haƙiƙaninsu ba a amfani da su wajen taimama kamar 'Tiles' da ire-irensu.

وَرُخِّصَ لِلْمَرِيضِ فِي حَائِطِ الْحَجَرِ وَالطُّوبِ إِنْ لَمْ يَجِدْ مُنَاوِلاً غَيْرَه.

*"An yi rangwame ga mara lafiya wajen taɓa bango ko tubali in bai samu mai kawo masa ƙasar da zai taimama ba"*

- ✓ Mara lafiya da ba zai iya tashi ba, kuma bai samu wanda zai kawo masa ƙasar da zai yi taimama; an yi masa rangwame da ya taɓa gini da aka yi da ƙasa, da dutse mutuƙar ba a yaɓe su da siminti ba.

## SUNNONIN TAIMAMA

تَجْدِيدُ الصَّعِيدِ لِيَدَيْهِ وَمَسْحُ مَا بَيْنَ الْكُوعَيْنِ وَالْمِرْفَقَيْنِ، وَالتَّرْتِيبُ.

*"Sabunta taɓa ƙasa da hannaye. Shafar abin da yake tsakanin idon hannu da gwiwar hannu, da jerantawa"*

Dukkan abubuwan da suka gabata suna daga cikin sunnonin taimama.

## MUSTAHABAN TAIMAMA

التَّسْمِيَةُ وَتَقْدِيمُ الْيُمْنَى عَلَى الْيُسْرَى وَتَقْدِيمُ ظَاهِرِ الذِّرَاعِ عَلَى بَاطِنِهِ وَمُقَدَّمِهِ عَلَى مُؤَخَّرِهِ

*"Faɗin Bismillah, zai gabatar da dama kafin hagu, zai gabatar da bayan zira'i kafin cikinsa, da kuma farkonsa kafin ƙarshensa"*

- ✓ Faɗin "Bismillahi" an shar'antata cikin dukkanin ibadu.
- ✓ Gabatar da dama a kan hagu saboda Hadisin Nana Aisha Allah ya ƙara mata yarda da ya gabata.

وَنَوَاقِضُهُ كَالْوُضُوءِ

*"Abubuwan da suke warware taimama: Duk abubuwan da suke warware alwala su ne dai abubuwan da suke warware taimama"*

- ✓ Kasancewar taimama tana wakiltar alwala; shi ya sa duk abin da yake lalata alwala shi yake lalata taimama.
- ✓ Samuwar ruwa yana warware taimama.
- ✓ Samun ikon amfani da ruwa bayan rashinsa (ko saboda rashin lafiya ko Hunturu)
- ✓ Wasu mutane biyu sun yi tafiya, sai lokacin sallahi ya riske su, amma ba su da ruwa. Sai suka yi taimama suka yi Sallah. Daga baya suka samu ruwa a cikin lokaci. Ɗayansu ya sake Alwala da Sallah, ɗayan kuma bai sake ba. Bayan sun iso sai suka faɗa wa mMa'aiki abin da ya faru, shi

kuma sai y ace ga wanda bai sake sallar ba: “Ka da ce da Sunna kuma Sallarka ta yi”. Ya cewa wanda ya sake: “Kana da lada biyu”.

**وَلاَ تُصَلَّى فَرِيضَتَانِ بِتَيَمُّمٍ وَاحِدٍ**

*“Ba a yin sallar farilla guda biyu da taimama ɗaya”*

- ✓ Saboda ba a taɓa samu Ma’aiki ya haɗa tsakanin salloli da taimama ɗaya ba saɓanin alwala.
- ✓ Sayyadina Ali yana cewa: “Wajibi ne sake taimama ga kowace Sallah”.
- ✓ Haka ɗan Abbas Allah ya ƙara masa yarda yake cewa “Yana daga cikin Sunna ba a yin Sallah fiye da ɗaya da taimama ɗaya, in za ka gabatar da Sallah; ka sake taimama”

**وَمَنْ تَيَمَّمَ لِفَرِيضَةٍ جَازَ لَهُ النَّوَافِلُ بَعْدَهَا**

*“Duk wanda ya yi taimama don gabatar da Sallar farilla; ya halatta ya yi Sallar nafila bayanta”*

- ✓ Da sharaɗin sadar da nafilar da farilla (ba tare da rarrabe tsakaninsu da kowana irin aiki ba), kuma da sharaɗin rashin fitar lokaci tare da ƙulla niyya a kan yin sallar nafila bayan ta farilla.

**وَمَسُّ الْمُصْحَفِ، وَالطَّوَافُ وَالتِّلاَوَةُ إِنْ نَوَى ذَلِكَ وَاتَّصَلَتْ بِالصَّلاَةِ وَلَمْ يَخْرُجِ الْوَقْتُ، وَجَازَ بِتَيَمُّمِ النَّافِلَةِ كُلُّ مَا ذُكِرَ إِلاَّ الْفَرِيضَةَ**

*“Haka ya halatta ya ɗauki Kur’ani, ya yi ɗawafi, kuma ya karanta Ku’rani in ya yi niyyar haka kuma ya sadar da ita da sallah ,mutuƙar lokaci bai fita ba. Ya halatta in mutum ya yi taimama don yin nafila ya aikata duk abubuwan da suka gabata ban da sallar farilla.”*

- ✓ Wato zai yi niyyar yin taimama don gabatar da sallar farilla tare da niyyar yin nafila a bayanta da ɗawafi da kuma karatun Alƙur'ani sai dai

wannan maganar mafi yawa daga cikin malaman da suka yi ƙarin bayani a kan littafin ahlari sun raunanata[1].

- ✓ Babu laifi a yi taimama don yin kowace irin sallah ko da kuwa lokacinta bai shiga ba.
- ✓ Haka, za ka iya sallar farilla sama da ɗaya, da taimama matuƙar dalilin da ya sa aka yi taimamar bai gushe ba. Wannan shi ne ra'ayi mafi ƙarfi a wannan babin In sha Allah.

**وَمَنْ صَلَّى الْعِشَاءَ بِتَيَمُّمٍ قَامَ لِلشَّفْعِ وَالْوَتْرِ بَعْدَهَا مِنْ غَيْرِ تَأْخِيرٍ**

*"Wanda ya yi sallar isha'i da taimama; (take) zai miƙe don kawo shafa'i da wutiri ba tare da jinkir ba"*

- ✓ Wato yin hakan ya halatta ba tare da jinkiri ba ta hanyar yin hira ko wani aikin daban.

**وَمَنْ تَيَمَّمَ مِنْ جَنَابَةٍ فَلاَ بُدَّ مِنْ نِيَّتِهَا.**

*"Wanda ya yi taimama saboda janabar da ta same shi; dole ya yi mata niyya"*

- ✓ Wato niyyar halattawa kansa gabatar da Sallah saboda dukkan ayyuka suna inganta ne da niyyoyinsu. Amma ba zai yi niyyar ɗauke karin gabaɗaya ba, kasancewar taimama ba ta ɗauke kari gabaɗayansa.

Tsokaci:

- ✓ Duk wanda ya rasa ruwa ko turɓayar da zai yi taimama; ya yi sallarsa a haka. Babu wani a'ibu a kansa balle ramuwa.
- ✓ Irin wannan halin ana samun kaine a cikin wasu gidajen gyaran hali ko halin tafiya a mota ko jirgin sama ko na ruwa da sauaransu.
- ✓ Duk da Imamuna Malik yana ganin wanda ya tsinci kansa a irin wannan halin; ba zai yi sallar ba kuma babu ramuwa a kansa.

---

[1] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", Shafi na (129)

AL’ADA

- Wani jini ne da yake fita daga al’aurar mace da kuma mahaifa da kansa, ga wacce take baliga ba tare da wata rashin lafiya ko kuma haihuwa ba.
- Allah ya sanya fitar al’ada ga mace ya zama alamar kuɓutar mahaifa daga juna biyu.
- Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce dangane da jinni al’ada: “Wani abu ne da Allah ya rubuta shi akan yaya mata cikin dangin Annabi Adamu.”
- Jinin da ya fita ba tare da rashin lafiya ba shi ake kira jinin al’ada.
- Jinin da ya fita a halin rashin lafiya shi ake kira jinin “Istihadha”, kamar yadda Ma’aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Kaɗai dai wannan fizgar jijiya ce, ba al’ada ba”
- Jinin da ya fita sanadiyyar haihuwa shi ake kira jinin biƙi.

وَالنِّسَاءُ مُبْتَدَأَةٌ وَمُعْتَادَةٌ وَحَامِلٌ

*“Mata iri uku ne: Akwai wacce yanzu ta fara, akwai wacce ta saba, akwai kuma mai juna biyu”*

- Danagane da wacce ta fara yanzu; ba ta da sanannan kwanaki na yawan al’adarta, hukuncinta ya dogara da yadda ta samu kanta, idan taga fatsi-fatsi ko kuma ƙasa-ƙasa a ƙarshen kwanakinta alama ce ta ɗaukewar al’ada (Ya danganta da yadda kwanakinta suka kasance).
- Wacce ta saba da yin al’ada, kuma tana da masaniya a kan lokacin zuwan jinin da lokacin ɗaukewarsa da kuma adadin kwanakin da take yi.

وَأَكْثَرُ الْحَيْضِ لِلْمُبْتَدِأَةِ خَمْسَةَ عَشَرَ يَوْمًا. وَلِلْمُعْتَادَةِ عَادَتُهَا. فَإِنْ تَمَادَى بِهَا الدَّمُ زَادَتْ ثَلاَثَةَ أَيَّامٍ مَا لَمْ تُجَاوِزْ خَمْسَةَ عَشَرَ يَوْمًا

*“Mafi yawan kwanakin al’ada ga wacce ta fara kwana sha biyar ne. (Wacce ta saba kuwa, tafi kowa sanin gwargwadon kwanakin al'adarta). In jinni ya*

*zarce mata a kan al'adar da ta sani ta ƙara kwana uku a kai, mutuƙar bai wuce kwana 15"*

- ✓ Wacce kuwa ta kasance ta daɗe tana yi ta san adadin kwanakinta. Mafi yawansa kwana goma sha biyar ne, ba ya ƙaruwa fiye da haka.
- ✓ Idan jini al'ada ya cigaba da zuba ga wacce ta san kwanakin al'adarta; sai ta ƙara kwanaki uku mutuƙar in ta ƙara kwanakin ba za su wuce kwana goma sha biyar ba.
- ✓ Idan Mace tana da ikon rabewa tsakanin jini al'ada da kuma jinin cuta; ba ta da buƙatar lissafin kwanaki. Za ta bar Sallah lokacin da jini yazo sa'annan ta cigaba da ibadunta idan ta tabbatar ya ɗauke kamar yadda Imamu Malik ya bayyana.[1]
- ✓ Misali: Macen da take kwana Takwas a al'adarta sai jini ya zarce mata; za ta ƙara kwana uku ya zama kwana 11, idan ya cigaba da zuba bayan cikar kwana 11 sai ta yi wanka ta cigaba da duk abin da aka hanata na ibada domin ragowar ya zama jinin cuta.

  A wata mai zuwa kwanakin al'adarta za su zama kwana Sha ɗaya, idan jini ya cigaba da zuba sai ta ƙara kwana Uku ya zama kwana Sha huɗu, in ya wuce kwana Sha huɗu, sai ta yi wanka ta cigaba da abubuwan da aka hanata na ibada idan tana cikin jinni, abin da ya ƙaru a kan kwana Sha huɗu ya zama jinin cuta.

  A wata mai zuwa al'adarta ta koma kwana Sha huɗu, idan jini ya cigaba da zuba sai ta ƙara kwana ɗaya ya zama kwana Sha Biyar. Idan ya cigaba da zuba bayan kwana Sha Biyar, sai ta yi wanka ta cigaba da duk abin da aka hanata na ibada domin ragowar ya zama jinin cuta.

[1] Ibnu Abudl-Bar "At-Tamhid", 16/76

Tsokaci: Duk yadda jini ya kai da yi wa mace wasa ba ya haura kwana Sha Biyar, duk abin da ya ƙaru a kan kwana Sha Biyar, ya zama jinin cuta, ba a ƙirga shi a matsayin jinin al'ada da zai hana Ibada.[1]

- ✓ In jinin ya wuce kwana gGoma sha biyar ya zama jinn cuta.

وَلِلْحَامِلِ بَعْدَ ثَلاَثَةِ أَشْهُرٍخَمْسَةَ عَشَرَ يَوْمًا وَنَحْوُهَا، وَبَعْدَ سِتَّةِ أَشْهُرٍ عِشْرُونَ وَنَحْوُهَا، فَإِنْ تَقَطَّعَ الدَّمُ لَفَّقَتْ أَيَّامَهُ حَتَّى تُكَمِّلَ عَادَتَهَا.

*"Mai ciki kuwa bayan wata uku, kwana Goma sha biyar ne ko makamancin haka. Bayan wata shida kuwa, kwana Ashirin ne da makamancinsa. Idan jini ya yanke mata, sai ta haɗa lissafin kwanakin har ya cika al'adarta da ta sani"*

- ✓ Idan jinin al'ada ya zo wa mai juna biyu (hakan yana da wuyar faruwa) za ta bar dukkanin ibadu, har sai jinin tsaya sannan ta yi wanka ta cigaba da ibadunta.
- ✓ Mai ciki idan jinin al'ada ya zo mata tana da halaye kamar haka:
    - Idan a watanni Ukun farko jinin al'adar ya zo mata, za ta ƙara kwana Goma sha biyar ko kwana Ashirin, daga nan in jinin ya cigaba da zuba ya zama jinin cuta. Za ta yi wanka kuma ta cigaba da dukkan dangogin ibada.
    - Idan Jinin al'ada yazo mata bayan juna biyun ya ƙetare wata uku har zuwa lokacin da za ta haihu; kwanakinsa zai zama kwana Talatin ne ko kuma kwana Ashirin, kamar yadda Malam Khalil ya bayyana a cikin Muktasar.
    - Idan kuwa jinin al'ada yazo bayan samun juna biyu da wata ɗaya ko wata biyu; za ta ƙara kwana uku a kan al'adarta da ta saba kafin samun cikin.

---

[1] Abdus Sami'I al-Abi "Hidayatul Mutabbidis Salik" shafi na (60). Abdun Nabiy Galib "Fiƙhul Mar'atul Muslima", shafi na (19-20)

- ✓ Wadda jini yake mata wasa (Wato misali; taga jini kwana biyu a cikon kwana na uku ya ɗauke sannan ya dawo a kwana na Huɗu) za ta ɗaura a kan lissafin kwanaki biyun da suka gabata har ya kai kwana Goma sha biyar.
- ✓ Wacce jini yake mata wasa duk lokacin da alamomin tsarki suka bayyana; za ta yi wanka ta cigaba da ibada.
- ✓ Tsarki yana da alamomi guda biyu
    - Bushewa: wato Mace ta sanya ƙyalle a cikin farjinta, ta fitar da shi a bushe ba tare da wani alamar jini ba.
    - Fari-fari: Wato wani ruwa ne fari mai kamar gasara da yake fitowa daga farjin Mace a lokacin da ta gama al'ada.

Abin lura Bayan waɗancan alamomin biyu sun bayyana ko mai Mace ta gani (Kamar fatsi-fatsi) ba ya daga cikin al'ada kamar yadda Ummu Aɗiya ta ce: "Bamu kasance muna ƙirga fatsi-fatsi bayan tsarki a matsayin wani abu ba"

- ✓ Yana da kyau a kwanakin ƙarshe na al'adar mace ta rinƙa duba kanta a ƙarshen dare kafin hudowar Alfijir, in ta samu tsarki, sai ta yi wanka ta yi Sallar Magriba da Isha'i.
- ✓ Haka, ta duba kafin faɗuwar rana, in ta samu tsarki, ta yi wanka ta yi sallar Azahar da La'asar.
- ✓ Haka, ta duba bayan Alfijir kafin hudowar rana, in ta samu tsarki za ta yi Sallar Asuba.

**وَلاَ يَحِلُّ لِلْحَائِضِ صَلاَةٌ وَلاَ صَوْمٌ وَلاَ طَوَافٌ وَلاَ مَسُّ مُصْحَفٍ وَلاَ دُخُولُ مَسْجِدٍ. وَعَلَيْهَا قضَاءُ الصَّوْمِ دُونَ الصَّلاَةِ، وَقِرَاءَتُهَا جَائِزَةٌ،**

*"Ba ya halatta ga mai al'ada ta yi Sallah ko azumi, ko ɗawafi, ko ɗaukar Kur'ani ko shiga Masallaci. Wajibi ne ta rama azumin da ta sha a watan Ramadan. Babu laifi za ta iya karanta Alƙur'ani"*

- ✓ Macen da take halin Al'ada ko biƙi ba ya halatta a gare ta ta yi sallah, kamar yadda yake cikin Hadisin Faɗimatu yar Abi Hubaish, ta kasance tana da cutar zubar jini, sai Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare she ya ce mata: "Idan jinin al'ada ya kasance baƙi ne ana gane shi, in ya kasance haka, to ki bar Sallah. Idan wani daban ya zo, ki yi alwala ki yi sallah"[1]
- ✓ Azumi yana haramta ga mai al'ada da kuma mai jinin biƙi, saboda Hadisin Abu Sa'idul Khuduri: Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi lokacin da yake cewa wasu taron mata: "… Shin idan ɗayarku tana al'ada ba tana barin Sallah da azumi ba"? Suka ce: Haka ne. Ma'aiki ya ce: "Wannan na daga cikin tawayar addininta"[2]
- ✓ Haka ɗawafi ba ya halatta ga mai al'da ko biƙi saboda Hadisin Nana Aisha Allah ya ƙara mata yadda da Ma'aiki yake ce mata: "Ki aikata duk abin da mai aikin Hajj yake aikatawa amma ban da ɗawafi har sai kin yi tsarki"[3]
- ✓ Dangane da shafar Alƙur'ani kuwa Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: "Kar wanda ya shafe shi, sai mai tsarki"[4]
- ✓ Shiga Masallaci kuwa Allah Maɗaukakin Sarki ya haramta shi ga mai Janaba, haka ma Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kamar yadda ya gabata.
- ✓ Wajibi ne ga mai al'ada ta rama azumin wata Ramadan idan ta yi tsarki.

---

[1] Abu Dawud Sulaiman ibn al-Ash'ath "Sunan abi Dawud" (282)

[2] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (2658)
[3] Muhammad ibn Isma'il al-Bukhari "Sahih al-Bukhari" (305)
[4] Suratul Waƙi'ah, aya ta 79

**وَلاَ يَحِلُّ لِزَوْجِهَا فَرْجُهَا وَلاَ مَا بَيْنَ سُرَّتِهَا وَرُكْبَتَيْهَا حَتَّى تَغْتَسِلَ.**

*"Ba ya halatta ga mijinta ya sadu da ita. Haka abin da yake tsakanin gwiwarta da cibiyarta har sai ta yi wanka"*

- ✓ Malamai gabaɗayansu sun haɗu akan shafar farjin mace mai al'ada ko da kuwa da yatsa ne ba ya halatta.
- ✓ Haka, mafi rinjayen malamai sun haɗu a kan ba ya halatta a gare shi daga cibiyarta zuwa gwiwarta saboda faɗinsa Maɗaukakin Sarki a cikin Suratul Baƙara aya ta 222.
- ✓ Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya cewa Abdullahi ɗan Sa'ad lokacin da ya tamabaye shi ina ne yake halatta a gare shi ga matarsa lokacin da take al'ada: "Saman cibiyarta"
- ✓ Babu laifi a sumbanci mai al'ada ko a rungumeta ko kuma shafi jikinta kamar yadda Hadisin Nana Aisha Allah ya ƙara mata yarda ya bayyana.

JININ BIKI

**وَالنِّفَاسُ كَالْحَيْضِ فِي مَنْعِهِ، وَأَكْثَرُهُ سِتُّونَ يَوْمًا، فَإِذَا انْقَطَعَ الدَّمُ قَبْلَهَا وَلَوْ فِي يَوْمِ الْوِلاَدَةِ، اغْتَسَلَتْ وَصَلَّتْ فَإِذَا عَاوَدَهَا الدَّمُ فَإِنْ كَانَ بَيْنَهُمَا خَمْسَةَ عَشَرَ يَوْمًا فَأَكْثَرَ كَانَ الثَّانِي حَيْضًا، وَإِلاَّ ضُمَّ إِلَى الأَوَّلِ وَكَانَ مِنْ تَمَامِ اَلنِّفَاسُ**

*"Shi jinni biƙi, kamar jinin al'ada be yake cikin hane-hanensa. Mafi yawan kwanakinsa kwana Sittin ne. Idan jinin ya yanke kafin kwana Sittin, ko da ranar da ta haihu ne; za ta yi wanka kuma ta yi Sallah. Idan jinin ya dawo mata, in ya kasance tsakanin yankewar da dawowar ya kai kwana Sha Biyar, ko sama da haka; wannan jinin da ya dawo na al'ada ne. in kuwa bai kai kwana Sha Biyar ba; sai ta haɗa lissafinta da na farko. Sai ya zama yana daga cikar jinin biƙi"*

- ✓ Shi ne jinin da yake fita bayan haihuwa.
- ✓ Hukuncinsa kamar hukuncin jinin al'ada ne, yana haramta duk abin da jinin al'ada yake haramtawa.

- ✓ Jinin biƙi ba shi da mafi ƙaranci, amma mafi yawansa kwana Sittin ne.
- ✓ In ya ɗauke a ranar da mace ta haihu; za ta yi wanka, ta yi Sallah kuma mijinta ya sadu da ita.
- ✓ Idan jinin ya dawo mata bayan kwana Sha Biyar ko sama da haka; ana ƙirga shi a matsayin jinin al'ada.
- ✓ Idan kuwa ƙasa da kwana Sha Biyar ne; ana ƙirga shi a matsayin jinin biƙi, sai ta haɗa lissafinsa da na baya.

## LOKUTAN SALLAH

- ✓ Abin da ake nufi da lokaci  a Shari'a; shi ne lokacin da aka warewa kowacce ibada.
- ✓ Sanin lokutan Sallah wajibi ne a kan baligi.
- ✓ Sanin lokutan Sallah farilla ce da wani yake ɗaukewa wani.
- ✓ Ba ya halatta baligi ya fara Sallah har sai tabbatar da shigar lokacinta kamar yadda Allah maɗaukakin Sarki ya faɗa cikin Suratun Nisa'i, aya ta 103.
- ✓ Kur'ani ya yi nuni zuwa ga lokutan Sallah cikin faɗinsa Maɗaukakin Sarki a Sutaul Isra'i, aya ta 78.
- ✓ Mala'ika Jibrilu ya sanar da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a cikin Hadisin Jabir.

### اَلْوَقْتُ الْمُخْتَارُ لِلظُّهْرِ مِنْ زَوَالِ الشَّمْسِ إِلَى آخَرَ الْقَامَةِ

*"Lokaci na zaɓi ga sallar Azahar: Gushewar Rana daga tsakiyar sama zuwa ƙarshen tsayin inuwa"*

- ✓ Mafificin lokacin da aka fi so a gabatar da sallar Azahar shi ne daga gushewar ranar daga tsakiya sama zuwa ƙarshen tsahon inuwa.
- ✓ Ana son jinkirta sallar Azahar lokacin tsananin zafi, saboda tsananin zafi na rage khushu'i saboda faɗinsa Ma'aiki: "Ku sanyaya lokacin sallar Azahar yayin tsananin zafi, haƙiƙa tsananin zafi yana daga numfashin Jahannama"

- ✓ Haka, ana gaggautata a lokacin da ba na zafi ba, saboda Hadisin Anas ɗan Malik Allah ya ƙara masa yarda yake cewa: "Ma'aiki ya kasance yana gaggauta sallah lokacin tsananin sanyi…"

وَالْمُخْتَارُ لِلْعَصْرِ مِنْ الْقَامَةِ إِلَى الاِصْفِرَارِ

*"Zaɓaɓɓen lokaci na sallar La'asar: (shi ne) Farkon ƙarshen tsayin inuwa zuwa rawayar rana"*

- ✓ Mafificin lokacin da aka fi so a gabatar da sallar La'asar yana farawa daga ƙarshen tsawon inuwa zuwa ninkuwarta saboda Hadisin Abdullahi ɗan Umar wanda Annabi yake cewa: "Lokacin sallar la'asar mutuƙar rana ba ta rawaya-rawaya ba"

وَضَرُورِيُّهُمَا إِلَى الْغُرُوبِ

*"Laluransu zuwa faɗuwar rana"*

- ✓ Lokacin da ba shi ne mafi soyuwa ba a sallaci Azahar ko La'asar yana tiƙewa zuwa farkon lokacin magriba (wato lokacin da rana ta fara jajata).

وَالْمُخْتَارُ لِلْمَغْرِبِ: قَدْرُ مَا تُصَلَّى فِيهِ بَعْدَ شُرُوطِهَا

*"Zaɓaɓɓan lokaci na sallar Magriba (shi ne), gwargadon lokacin da aka sallace ta bayan shigarta"*

- ✓ Mafificin lokacin da aka fi so a gabatar da sallar Magriba yana farawa ne daga faɗuwar rana zuwa lokacin da aka kammalata tare da dukkan sharuɗanta na tsarki da suturce al'aura, fuskantar alƙibla da sauransu.

وَالْمُخْتَارُ لِلْعِشَاءِ مِنْ مَغِيبِ الشَّفَقِ إِلَى ثُلُثِ اللَّيْلِ الأَوَّلِ

*"Zaɓaɓɓan lokaci na sallar Isha'i: (shi ne) bayan ɓuyar jajatar rana zuwa ɗaya bisa uku na dare"*

- ✓ Lokaci mafi soyuwa ga sallar Isha'i yana faraway ne daga ɓuyan fatsi-fatsi zuwa ɗaya bisa ukun dare

**وَضَرُورِيُّهُمَا إِلَى طُلُوعِ اَلْفَجْرِ**

*"Lalurunsu zuwa hudowar Alfijir"*

- ✓ Mafificin lokacin da aka fi so a gabatar da sallar Magriba ko Isha'i yana faraway ne daga farkon ɗaya bisa ukun dare izuwa hudowar Alfijir.

**وَالْمُخْتَارُ لِلصُّبْحِ مِنَ الْفَجْرِ إِلَى الإِسْفَارِ الأَعْلَى**

*"Zaɓaɓɓan lokaci na Sallar Asuba (shi ne) daga hudowar Alfijir zuwa wayewar gari, kafin hudowar rana"*

- ✓ Mafificin lokacin da aka fi so a gabatar da sallar Asubahi yana farawa ne daga hudowar Alfijir na gaskiya zuwa gari ya fara haske.

**وَضَرُورِيُّهُ إِلَى طُلُوعِ الشَّمْسِ**

*"Larurorinta: daga wayewar gari zuwa hudowar rana"*

- ✓ Lokacin da ba shi ne mafi soyuwa ba a sallaci Asubahi ba; daga lokacin da gari ya yi haske zuwa ga hudowar rana.

**وَالْقَضَاءُ فِي الْجَمِيعِ مَا وَرَاءَ ذَلِكَ.**

*"Ana yin ramuwa ne a cikin lokacin da ba wannan ba"*

- ✓ Ana rama sallah ne kaɗai in ba a gabatar da ita ba a lokaci mafi soyuwa ko kuma lokacin da ba shi ne mafi soyuwa ba (Lokacin Lalurori)
- ✓ Ana rama sallar Azahar ko La'asar idan aka yi sakaci har rana ta faɗi. Haka, ana rama sallar Magirba da Isha'i idan Alfijir ya keto. Kamar yadda ana rama sallar Asubahi idan rana ta keto.

**وَمَنْ أَخَّرَ الصَّلاَةَ حَتَّى خَرَجَ وَقْتُهَا فَعَلَيْهِ ذَنْبٌ عَظِيمٌ إِلاَّ أَنْ يَكُونَ نَاسِيًا أَوْ نَائِمًا**

*"Duk wanda ya jinkirta Sallah har lokacinta ya fita; tabbas ya ɗauki zunubi mai girma sai dai in mantawa ya yi ko kuma ya yi barci"*

- ✓ Duk wanda ya yi wa sallar riƙon sakainar kashi har lokacinta ya fita tabbas ya ɗauki zunubi mai girma. Tabbas ya cancanci fushin Allah, sai dai wanda yake da uzuri.

**وَلاَ تُصَلَّى نَافِلَةٌ بَعْدَ صَلاَةِ الصُّبْحِ إِلَى ارْتِفَاعِ الشَّمْسِ، وَبَعْدَ صَلاَةِ الْعَصْرِ إِلَى صَلاَةِ الْمَغْرِبِ، وَبَعْدَ طُلُوعِ الْفَجْرِ إِلاَّ الْوِرْدَ لِنَائِمٍ عَنْهُ وَعِنْدَ جُلُوسِ إِمَامِ الْجُمُعَةِ عَلَى الْمِنْبَرِ، وَبَعْدَ الْجُمْعَةِ حَتَّى يَخْرُجَ مِنَ الْمَسْجِدِ**

*"Ba a yin sallar nafila bayan sallar Asuba har sai rana ta hudo. Haka bayan sallar La'asar har sai rana ta faɗi. Haka bayan hudowar Alfijir, sai dai sallar da mutum ya saba yi, barci ya hana bai gabatar da ita ba. Haka lokacin da Limamin Juma'a yake zama a kan mumbari. Haka bayan sallar juma'a har sai mutum ya bar masallaci"*

- ✓ Hani dangane da yin sallar Nafila a wasu lokuta hani ne ko dai na Haramci ko na Karhanci.
- ✓ Hani na haramci shi ne ba a Sallah daidai lokacin da rana take hudowa ko kuma take faɗuwa.
- ✓ Hanin yin sallar Nafila bayan idar da sallar Asubahi kai-tsaye hani ne na karhanci.
- ✓ Ya halatta a yi sallar Jana'iza bayan idar da sallar Asubahi kai-tsaye.
- ✓ Haka, babu laifi don yin sujjadar karatun Kur'ani.
- ✓ Sallar nafila bayan La'asar da bayan hudowar Alfijir kafin Sallar Asubahi (Sai dai ina Salloli biyu ne Alfijir ko Shafa'i da wutiri ga wanda barci ya rinjaye shi bai gabatar dasu ba), da bayan rana ta faɗi kafin gabatar da sallar Magriba da kuma sallar nafila lokacin da Liman ya hau mumbari kafin ya fara huɗuba duk hani ne na karhanci.
- ✓ Sallar nafila haramunce idan Liman ya fara Khuɗuba, ga mutumin da yake cikin masallaci.

# SHARAƊAN SALLAH

- ✓ Bayan malam ya kammala bayani a kan hukunce-hukuncen tsarki sai ya ci gaba da bayani a kan Sallah domin ita ce mafi girman rukunan Masulunci bayan Kalmar shahada.
- ✓ Sallah wajibi ce a kan kowana baligi, kamar yadda nassin Kur'ani da Hadisi da kuma Ijima'in malamai suka bayyana.
- ✓ Sallah wajibi ce a kan kowanne masulmi ya santa.
- ✓ Duk wanda ya musanta wajibincinta, lallai ya kafirta, za a nemi tubansa sau Uku, idan ya ƙi; shari'a za ta kashe shi a matsayin Kafiri.
- ✓ Wanda ya yadda da wajibcinta amma ya ƙi yinta, lalle shi mai saɓo ne, za a jikirta masa gwargwadon raka'a ɗaya kafin lokacinta na laruri ya fita. Za a cigaba da nanata masa da kuma umartarsa da ya yi Sallah. Idan har lokaci ya fita bai yi sallar ba; shari'a za ta tsayar masa da haddin kisa. Allah ya tsare mu.[1]
- ✓ Sharaɗi shi ne abin da in babu shi babu hukunci, samuwarsa kuma ba shi yake tabbatar da samuwar hukuncin ba. Misali: Tsarki sharaɗi ne na Sallah domin in babu tsarki babu Sallah. Amma kuma za a iya samun tsarki kuma Sallah ta lalace sakamakon barin wani sharaɗin daban ko kuma barin rukuni.
- ✓ Rukuni na nufin turakun ibadar amma sharaɗi na nufin abin da yake wajen turakun ibada amma kuma dole sai da shi sannan rukuni zai inganta.

Sharuɗan Sallah suna rabuwa zuwa:

- ✓ Sharaɗan wajabci wanda suka ƙunshi:
  - Masulunci: Domin Allah ba ya karɓar aikin Kafiri.
  - Balaga: Kasancewar Sallah ba wajibi ba ce a kan yaro har sai ya yi mafarki.
  - Hankali: Sallah ba ta wajaba a kan Mahaukaci.

---

[1] Walidu bnul Fakki "Ittihaful Mubtadi'I fi Sharhi Mukhtasarul Akhdari", Shafi na (150)

- Shigar lokaci: Sallah ba ta inganta har sai lokacinta ya shiga.[1]

✓ Sharuɗan inganci (wanda su ne marubucin ya yi nuni zuwa gare su):

**وَشُرُوطُ الصَّلاَةِ طهَارَةُ الْحَدَثِ وَطهَارَةُ الْخَبَثِ مِنَ الْبَدَنِ وَالثَّوْبِ وَالْمَكَانِ وَسَتْرُ الْعَوْرَةِ وَاسْتِقْبَالُ الْقِبْلَةِ، وَتَرْكُ الْكَلاَمِ وَتَرْكُ الأَفْعَالِ الْكَثِيرَةِ،.**

*"Sharuɗan Sallah: Tsarkaka daga kari da tsarkaka daga najasa (Jiki da Tufa da kuma Bigire) da suturce al'aura da fuskantar alƙibla da barin zance da barin ayyuka masu yawa"*

✓ Tsarkaka daga Kari: wato tsarkaka daga ƙarami da kuma babban kari kamar yadda ya gabata domin Sallah ba ta ingantuwa sai sai da su. Wajibi ne a gusar da dukkan najasa da ruwa mai tsarki ko da waninsa kamar yadda ya gabata. Duk wanda ya yi sallah da najasa ko kuma najasar ta fallatso masa[2]ko da kuwa da a kan kuskure ne da makamantansu Sallah ta ɓaci, idan ya san da faruwarta.

✓ Tsarkaka daga najasa (Jiki da Tufa da kuma Bigire): Wato gusar da najasa daga gangar jikin mutum da kuma tufafinsa wanda ya haɗa da takalminsa da hularsa da rawaninsa. Bigire kuma yana nufin in da gaɓoɓi za su taɓa wajen tsayuwarsa da sujjadarsa da zamansa.

  A takaƙaice, wajibi ne gusar da najasar da ba a yi rangwame a kanta ba daga jikin mutum da tufafinsa da kuma bigiran Ibada.

✓ Suturce al'aura: Da baligi zai shiga Sallah ba tare ya suturce al'aurarsa ba; Sallarsa ɓatacciya ce. Sai dai shar'a ta yi rangwame ga wanda ba shi da tufafi kuma babu inda zai samu.

  Wajibi ne tufafin ya zama mai kauri, ta yadda jiki ba zai bayyana ba, domin tufafin da ake ganin fatar mutum kamar tsirara ne, ba ya halatta Sallah da shi.

---

[1] Aminuddini Abubakar "Sharhun wa Tahlilun li Mukhtasaril Akhdari fil Ibadat", Shafi na 299

[2] Kamar Mace ta goya jaririyarta ta yi mata fitsari a jikinta

Haka, amfani da matsattsun kaya suna shiga cikin abubuwan ƙyamata wanda in ba a kiyaye ba zai iya zama haramun.

Duk wanda ya yi sallah tsirara (yana da ikon samun tufafi) a bisa mantuwa ko ganganci, ko kuma bisa jahilci; sallarsa ta ɓaci, wajibi ne a kansa ya sake ta.

- ✓ Fuskantar Alƙibla: wato fuskantar Ka'aba na ɗaya daga cikin sharuɗan ingancin Sallah. Ko kuma kirdadonta ga waɗanda suka yi nisa da ita sosai, ko kuma a yi amafani da na'ura ta zamani domin tabbatar da in da alƙiblar take.

  Malamai gabaɗayansu sun haɗu akan bai halatta mutum ya yi Sallah ba mutuƙar bai fuskanci Alƙibla ba, sai dai a halin tsoro mai tsanani ko yaƙi ko matifiyi in zai yi sallar Nafila a kan dabbarsa.

  Duk wanda ya juya Alƙibla ba  bisa ganganci ba, kuma yana da ikon fuskantarta; sallarsa ta lalace.

  Wanda ya kauce wa Alƙibla a bisa rashin sani; an so ya sake sallarsa.

- ✓ Barin zance: Duk wata Magana da aka yi a cikin Sallah mutuƙar ba ta gyaran Sallah ba ce, tabbas ta lalata sallah saboda Hadisin Zaidu ɗan Arƙam da yake cewa: "Mun kasance muna magana a ciki sallah har sai da aka saukar da aya ta 238 a cikin baƙara, sai aka umarcemu da mu yi shiru, aka hanemu da yin magana (a cikin sallah)'.
- ✓ Barin ayyuka masu yawa: wato barin jinsin ayyukan da ba na Sallah ba amma an yi afuwa ga aikin ɗan kaɗan.

**وَعَوْرَةُ الرَّجُلِ مَا بَيْنَ السُّرَّةِ وَالرُّكْبَةِ، وَالْمَرْأَةُ كُلُّهَا عَوْرَةٌ مَا عَدَا الْوَجْهَ وَالْكَفَّيْنِ.**

*"Al'aurar namiji ita ce abin da yake tsakanin cibiya zuwa gwiwa. Ita kuwa mace gabaɗaya jikinta al'aura ce, ban da fuska da kuma tafuka"*

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani a kan cewa suturce al'aura sharaɗi ne na ingancin sallah, yanzu zai yi bayanin mecece al'aurar namiji da ta mace.

- ✓ Wajibi ne a kan baligi ya rufe daga cibiyarsa zuwa gwiwarsa idan zai yi sallah, har a wajen Sallah hakan wajibi ne a kansa.
- ✓ Haka, yana wajaba ga Mace ta rufe ko'ina a jikinta in za ta yi Sallah da kuma wajen Sallah ban da fuskarta da kuma tafukanta.
- ✓ Al'aura iri biyu ce, akwai babba (Kamar farji da dubura) wadda take wajabta sake sallah in ta bayyana da kuma ƙarama (abin da yake tsakanin cibiya da gwiwa amma babbar al'aura), wacce aka so ake sallah in ta bayyana.
- ✓ Imamu Malik ya ce: "Idan digadigai ko gashi suka bayyana; za ta sake Sallah mutuƙar lokaci bai fita ba"[1]

**وَتُكْرَهُ الصَّلَاةُ فِي السَّرَاوِيلِ، إِلاَّ إِذَا كَانَ فَوْقَهَا شَيْءٌ،**

*"Makaruhi ne yin Sallah da wando kaɗai, sai dai in mutum ya ɗaura wani abu a kafaɗunsa"*

- ✓ Makaruhi ne ya yi Sallah da wando wanda yake mai shara-shara ko kuma ɗamamme da yake bayyana al'aura sai dai in ya sanya rigar da za ta rufe shi. in kuwa ba haka ba; haramun ne ya yi Sallah a haka.

**وَمَنْ تَنَجَّسَ ثَوْبُهُ وَلَمْ يَجِدْ ثَوْبًا غَيْرَهُ وَلَمْ يَجِدْ مَاءً يَغْسِلُهُ بِهِ أَوْ لَمْ يَكُنْ عِنْدَهُ مَا يَلْبَسُ حَتَّى يَغْسِلَهُ وَخَافَ خُرُوجَ الْوَقْتِ صَلَّى بِنَجَاسَتِهِ، وَلاَ يَحِلُّ تَأْخِيرُ الصَّلاَةِ لِعَدَمِ اَلطَّهَارَةِ، وَمَنْ فَعَلَ ذَلِكَ فَقَدْ عَصَى رَبَّهُ، وَمَنْ لَمْ يَجِدْ مَا يَسْتُرُ بِهِ عَوْرَتَهُ صَلَّى عُرْيَانًا،**

*"Duk wanda tufarsa ta samu najasa kuma bai samu wata tufar ba kuma bai samu ruwan da zai wanketa ba, ko bai samu tufar da zai sanya kafin ya wanke ta ba kuma yana tsoron fitar lokaci; ya yi sallah da najarsa. Bai halatta a jinkirata sallah ba (har lokacinta) ya fita saboda rashin tsarki. Wanda ya aikata haka ya saɓawa Allah. Wanda duk bai samu tufar da zai suturce al'aurarsa ba; ya yi Sallah tsirara"*

---

[1] Suhunun "Al-Mudawwana", shafi na 155

- ✓ Ya gabata cewa wajibi ne baligi ya gusar da najasa daga jiki da tufafi da kuma bigiran Sallah.
- ✓ Samun iko wajen gusar da najasa ta hanyar samun ruwa mai tsarki na daga cikin sharaɗin tsarki.
- ✓ Idan baligi bai samu iko ba, kuma ya ji tsoron fitar lokaci; sai ya yi sallar da najasar, babu komai a kansa In sha Allah.
- ✓ Jinkirta Sallah saboda rashin samun ikon gusar da najasa na daga cikin manya-manyan laifi.
- ✓ Haka duk wanda bai samu ikon suturce al'aurarsa ba; ya yi sallarsa tsirara.

**وَمَنْ أَخْطَأَ الْقِبْلَةَ أَعَادَ فِي الْوَقْتِ،**

*"Wanda ya kuskurewa alƙibla; ya sake sallah in da lokaci ( in lokacin bai fita ba)"*

- ✓ Bayanai sun gabata a kan hakan.

**وَكُلُّ إِعَادَةٍ فِي الْوَقْتِ فَهِيَ فَضِيلَةٌ،**

*"Sake Sallah a lokacinta mustahabbi ne"*

- ✓ Kamar wanda ya kuskure alƙibla, in ya sake sallarsa kafin fitar lokacinta haka aka so, in kuma lokacinta ya fita; babu buƙatar sakewa.

**وَكُلُّ مَا تُعَادُ مِنْهُ الصَّلَاةُ فِي الْوَقْتِ فَلَا تُعَادُ مِنْهُ الْفَائِتَةُ وَالنَّافِلَةُ ✓**

*"Duk sallar da aka ce a sake ta sakamakon wani dalili akan lokaci, ba a saketa in lokacin ya fita, haka ma nafila.*

- ✓ Kamar dai wanda ya yi sallar nafila da tufafi masu najasa saboda ba shi da ikon gusar da ita, toh ba zai sake wannan sallar ba.

## FARILLAN SALLAH

**فَرَائِضُ الصَّلاَةِ: نِيَّةُ الصَّلاَةِ الْمُعَيَّنَةِ، وَتَكْبِيرَةُ الإِحْرَامِ وَالْقِيَامُ لَهَا، وَالْفَاتِحَةُ وَالْقِيَامُ لَهَا، وَالرُّكُوعُ وَالرَّفْعُ مِنْهُ, وَالسُّجُودُ عَلَى الْجَبْهَةِ وَالرَّفْعُ مِنْهُ، وَالاِعْتِدَالُ، وَالطُّمَانِينَةُ، وَالتَّرْتِيبُ بَيْنَ فَرَائِضِهَا، وَالسَّلاَمُ وَجُلُوسُهُ الَّذِي يُقَارِنُهُ**

*"Farillan Sallah (su ne) niyyar Sallar lokacin da kabbarar harama, da kuma tsayuwa dominta da karanta Fatiha, da kuma tsayuwa dominta da ruku'u da kuma ɗagowa daga ruku'u, da Sujjada a kan goshi da kuma ɗagowa daga sujjada da daidaituwa da nustuwa da jeranta tsakanin farllai, da Sallama da zaman ƙarshe"*

- ✓ Farilla ita ce dukkan aikin da shari'a ta nemi Bbaligi ya aikata ta fuskatar tilastawa.
- ✓ Farillan sallah wato abubuwa da suke wajibi ne sai an cika su sannan sallah za ta inganta.

Niyyar Sallar lokacin

- ✓ Wato Masallaci ya ƙudurce a ransa irin sallar da zai gabatar (Azahar ce ko La'asar ko makamantansu).
- ✓ Furtata ba ya daga cikin sharaɗinta domin muhallinta a zuci yake.
- ✓ Furta niyya makaruhi ne sai dai ga wanda yake yawan kokwanto; shi babu laifi a kansa.
- ✓ Niyya ana gwamata ne tare da kabbarar harama, ba ya halatta a raba tsakaninsu.

Kabbarar harama da Tsayuwa domin ta

- ✓ Da ita ne ake shiga cikin sallah kai tsaye.
- ✓ Kabbarar harama tana haramtawa masallaci abubuwan da suka halatta kafin ita kamar ci da sha da kuma zance.
- ✓ Lafazinta "Allahu Akbar" baya halatta ga wanin wannan lafazin.
- ✓ Amma ga wanda yake ba shi da ikon furtata a yadda take (Kamar Bebe ko mai In'ina ko kuma wanda bai iya Larabci ba); sai ya ƙudurce a

zuciyarsa ya shiga sallah, ko kuma ya yi amfani da lafazin da yake da irin na waccan ma'anar.

- ✓ Wato ga wanda yake da iko a kan tsayuwar, da baligi (mai iko akan tsayuwa) zai yi kabbarar sallar farilla a zaune sanna ya miƙe daga baya; lallai sallarsa rusasshiya ce. Amma in nafila ce; babu laifi.

Karanta Fatiha da kuma tsayuwa dominta.

- ✓ Wato ya motsa harshe domin karatun Fatiha.

Wato wajibi ne ga Liman ko mai Sallah shi kaɗai ya karanta Fatiha amma ga wanda ba zai iya ba; ta faɗi a kansa.

Ruku'u da kuma ɗagowa daga ruku'u

- ✓ Shi ne ranƙwafawar mai Sallah har ya kai kusa da gwiwarsa ta yadda zai ɗaura tafukansa a kan ƙoƙon gwiwarsa.
- ✓ Kar ya sunkuyar da kansa ƙasa sosai ko kuma ya ɗaga shi sama sosai.
- ✓ Ya daidaita kansa da gadon bayansa, kamar yadda in aka daura masa Tulu zai zauna.
- ✓ An so Namiji ya ware ƙafafuwansa kaɗan kamar yadda aka so Mace ta haɗe ƙafafuwanta kaɗan.
- ✓ In ya ɗago daga Ruku'i ya tsaya ƙyam, ta yadda kowace gaɓa za ta daidaita gajeran lokaci.
- ✓ Daidaito da nutsuwa bayan ɗagowa daga Ruku'i farilla ne, barin ɗaya daga cikinsu na ɓata Sallah.

Sujjada a kan goshi da kuma ɗagowa daga sujjada

- ✓ Wato ɗaura faɗin goshi akan ƙasa.
- ✓ Goshi shi ne abin da yake tsakanin gira da makwarkwaɗar kai (ƙarshen matsirar gashin kai).
- ✓ Wanda ya yi sujjada a kan hanci kaɗai; sallarsa ta ɓaci amma wanda ya yi sujjada da goshi kaɗai ban da hanci ya aikata makaruhi.
- ✓ Domin haka ne yake rarrabe tsakanin sujjadar farko da ta biyu.
- ✓ Rarrabe tsakanin sujjadar farko da ta biyu wajibi ne.

Daidaituwa

- ✓ Mai Sallah wajibi ne ya daidaitu a tsaye ƙyam, wato kowace gaɓa ta koma in da take ta daidaita, a lokacin ɗagowa daga ruku'u da kuma sujjada.
- ✓ Misali: wajibi ne ga wanda ya ɗago daga ruku'u ya daidaita a tsaye kafin ya tafi sujjada. Haka, wajibi ga wanda ya ɗago daga sujjada ya daidai a zaune kafin ya tashi ko kafin ya koma sujjada ta biyu.

Nutsuwa

- ✓ Tabbatuwar gaɓoɓi a yayin ruku'u ko sujjada ko tsayuwa da zama.

Jeranta tsakanin farillai.

- ✓ Wajibi ne gabatar da Sallah a tsarin da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya koyar.
- ✓ Ana fara gabatar da niyya kafin kabbarar harama. Ana gabatar da kabbarar harama kafin karatun Fatiha kamar dai yadda suka zo a cikin farillan sallah.

Sallama

- ✓ Sallama ana yin ta ne a bayyane bayan gama Tahiyar ƙarshe ta kowacce Sallah ta hanayar faɗin "Assalamu Alaikumwa Wa Rahmatullahi" ko kuma "Assalamu Alaikum" yayin da Liman yake ɗan karkatar da kansa ɓangaran dama.

Zaman ƙarshe.

- ✓ Shi ne zaman da ake yi kafin Sallama.
- ✓ Tsawonsa shi ne gwargwadon ɗan zaman da ake yi domin Tahiyya.

SUNNONIN SALLAH

الإِقامَةُ، وَالسُّورَةُ الَّتِي بَعْدَ الْفَاتِحَةِ، وَالْقِيَامُ لَهَا، وَالسِّرُّ فِيمَا يُسَرُّ فِيهِ، وَالْجَهْرُ فِيمَا يُجْهَرُ فِيهِ، وَسَمِعَ اللهُ لِمَنْ حَمِدَهُ. وَكُلُّ تَكْبِيرَةٍ سُنَّةٌ إِلاَّ الأُولَى وَالتَّشَهُّدَانِ وَالْجُلُوسُ لَهُمَا، وَتَقْدِيمُ الْفَاتِحَةِ عَلَى السُّورَةِ وَالتَّسْلِيمَةُ الثَّانِيَةُ وَالثَّالِثَةُ لِلْمَأْمُومِ، وَالْجَهْرُ بَالتَّسْلِيمَةِ الْوَاجِبَةِ، وَالصَّلاَةُ عَلَى رَسُولِ اللهِ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ، وَالسُّجُودُ عَلَى الأَنْفِ وَالْكَفَّيْنِ وَالرُّكْبَتَيْنِ وَأَطْرَافِ الْقَدَمَيْنِ وَالسُّتْرَةُ لِغَيْرِ الْمَأْمُومِ وَأَقَلُّهَا غِلَظُ رُمْحٍ وَطُولُ ذِرَاعٍ طَاهِرٍ ثَابِتٍ غَيْرِ مُشَوِّشٍ.

*"Sunnonin Sallah: Iƙama da karatun Sura bayan da tsayuwa dominta, da sirranta karatu a wurin da ake sirrantawa da Bayyana karatu a wurin da ake bayyanawa da faɗin Sam'allahu liman Hamidahu da kowacce kabbara Sunna ce ban da ta farko da Karatun Tahiya na farko da na biyu da kuma zama dominsu da Fara karanta kafin Sura da Sallama ta biyu da ta uku ga mai koyi da liman da Bayyana sallamar farilla da Salati ga Ma'aiki (a cikin Tahiyya) da Sujjada a kan hanci da tafuka da gwiwa da tsinin yan yatsun ƙafa, da Sanya sitira ga Liman, mafi ƙarancin girmanta (shi ne) kaurin mashi, tsawon ta shi ne tsintsiyar hannu, ta kasance mai tsarki a tsaye ba zane-zane ko karkata a jikinta.*

- ✓ Bayan Malam ya gama bayani dangane da farillan Sallah sai ya shiga bayani a kan Sunnoni.
- ✓ Daga cikin su akwai ƙarfafa (waɗanda idan aka bar fiye da ɗaya za a yi mata sujjada.)

Iƙama

- ✓ Tana daga cikin Sunnoni masu ƙarfi.
- ✓ Ma'anarta shi ne sanar da shiga Sallah ta hanyar amfani da sanannen lafazi.

- ✓ Ma’aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: “Babu wasu mutane guda uku da ba sa yin kiran sSallah, ba a yin Iƙama a cikinsu face Shaiɗan ya yi rinjaye a kansu…”
- ✓ Iƙama ana ɗayanta lafuzanta sai dai wajen faɗin “Allahu Akbar” ta farko da ta ƙarshe ana faɗinsu sau bi-bi-yu.

Karatun Sura bayan da tsayuwa dominta

- ✓ Na daga cikin Sunnonin masu ƙarfi cikin haƙƙin Liman da kuma mai Sallah shi kaɗai.
- ✓ Ana karanta Sura a raka’o’in biyu na farko a dukkanin Salloli, ban da Asubahi.
- ✓ Idan liman yana karatu a bayyane ba wajibi bane a kan mai bin sallah ya karanta Sura ba sai dai an so haka a karatun ɓoye.
- ✓ Karatun Sura yana inganta ko aya ɗaya aka karanta.
- ✓ Wato tsayuwar da ake yi a lokacin da ake karanta Sura ita ma Sunna ce.

Sirranta karatu a wurin da ake sirrantawa

- ✓ Hakan na daga cikin sunnoni masu ƙarfi kamar karatun ɓoye a sallar Azahar da La’asar da Raka’ar ƙarshe ta Magrib da kuma Raka’o’i biyun ƙarshe na Sallar Isha’i.
- ✓ Malamai sun haɗu akan hakan.
- ✓ Ma’anar ɓoyewa shi ne: yin karatu tare da furta lafuzan ayoyin da ake karantawa ta hanyar mai Sallah ya jiyar da kansa, da kuma wanda ya kusanceka sosai.
- ✓ Amma karatu a cikin zuci ba tare da motsa harshe ba; ba a ƙirga shi a matsayin karatun Sallah, domin wannan tunani ne kawai.

Bayyana karatu a wurin da ake bayyanawa

- ✓ Hakan na daga cikin Sunnoni masu ƙarfi.
- ✓ Bayyana karatu a cikin Sallah kamar ta Asubahi da Raka'o'i biyun farko na sallar Magriba da Isha’i domin Ma’aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana bayyana karatunsu.

- ✓ Mafi ƙarancin bayyanawa shi ne mai Sallah ya jiyar da kansa da waɗanda suke bin sa amma mafi ɗaukakarsa ba shi da iyaka a cikin haƙƙin namiji.
- ✓ Ita kuwa mace za ta jiyar da kanta ne kaɗai, babu buƙatar ta ɗaga muryarta.

Faɗin Sam'allahu liman Hamidahu

- ✓ Shi mai bin Sallah yana faɗin "Rabbana Wa lakal hamdu" bayan Liman ya faɗi "Sam'allahu Liman Hamidahu"
- ✓ Kuma faɗinsa "Sam'allahu liman Hamidahu" yana daga cikin Sunnoni masu ƙarfi

Kowacce kabbara Sunna ce ban da ta farko

- ✓ Yana da cikin Sunna yin dukkanin kabbarori ban da ta farko kuma ana haɗasu tare da aiki kamar Kabbara lokacin ruku'I ko kuma yinta lokacin sujjada da sauran gurabe.
- ✓ Abdullahi ɗan Mas'ud yake cewa: Na ga Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana yin Kabbara a dukkan Ruku'u da tsayuwa da kuma zama.

Karatun tahiya na farko da na biyu, da kuma zama dominsu

- ✓ Karatun tahiyya ta farko da ta biyu suna daga cikin Sunnoni.

Fara karanta  kafin Sura

- ✓ Fara karatun Sura kafin Fatiha, yin hakan ya saɓawa Sunna, mai Sallah zai sake wannan raka'ar in ya ƙullata ko kuma karatun in bai ƙulla raka'a ba.
- ✓ Ba zai yi sujjadar rafkanwa ba cikin abin da yake sananne a gurin malamai.

Sallama ta biyu da ta uku ga mai koyi da liman

- ✓ Yana daga cikin Sunnonin Sallah yin Sallama ta biyu da ta uku ga mai koyi da Liman, wato zai mayar da sallama ga limaminsa da kuma wanda yake ɓangarnsa na hagu in da akwai mutum.

Bayyana sallamar farilla

- ✓ Sunna ce daga cikin Sunnonin Sallah bayyana Sallamar farko ga Liman, wadda ita ce za ta fitar da shi daga cikin Sallah amma ba wajibi bane ga mai bin Sallah ya bayyanta.

Salati ga Ma'aiki (a cikin tahiyya)

- ✓ Yin Salati ga Mai'aiki yana daga cikin Sunna a tahiyar ƙarshe.
- ✓ Sheikh Nasiruddini Al'albani yana cewa: "Ma'aiki ya kasance yana yiwa kansa Salati a tahiyar farko da ta ƙarshe kuma ya shar'anta haka ga al'ummarsa"

Sujjada a kan hanci da tafuka da gwiwa da tsinin yan yatsun ƙafa.

- ✓ Yana da cikin Sunna yin sujjada a kan gaɓoɓi guda bakwai kamar yadda Hadisin Abdullahi ɗan Abbas ya bayyana.

Sanya sitira ga Liman mafi ƙarancin kaurinta kaurin mashi, tsawonta shi ne tsintsiyar hannu, ta kasance mai tsarki a tsaye ba zane-zane ko karkata a jikinta.

- ✓ Ana sanyata ne ga Liman da kuma mai yin Sallah shi kaɗai domin hana ƙetara Sallah.
- ✓ Tana da Sunnar da aka shar'anta kamar yadda yazo a cikin Hadisin Abu Sa'idu Al khudri.
- ✓ Yana daga cikin hikimar sanya Sitira: Tabbatar da Khushu'i ga mai Sallah da kuma hana wani abu ya ɗauki tunaninsa ta hanyar kalle-kalle ko kuma tunane-tunane

MUSTAHABBAN SALLAH

- ✓ Bayan Malam ya kamala bayani a kan Sunnonin Sallah, yanzu kuma zai fara bayani a kan abubuwa da aka so a aikata su a cikin Sallah.

**رَفْعُ الْيَدَيْنِ عِنْدَ الإِحْرَامِ حَتَّى تُقَابِلاَ الأُذُنَيْنِ وَقَوْلُ الْمَأْمُومِ وَالْفَذِّ: رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ، وَالتَّأْمِينُ بَعْدَ الْفَاتِحَةِ لِلْفَذِّ وَالْمَأْمُومِ، وَلاَ يَقُولُهَا الإِمَامُ إِلاَّ فِي قِرَاءَةِ السِّرِّ، وَالتَّسْبِيحُ فِي الرُّكُوعِ وَالدُّعَاءُ فِي السُّجُودِ، وَتَطْوِيلُ الْقِرَاءَةِ فِي الصُّبْحِ وَالظُّهْرِ تَلِيهَا وَتَقْصِيرُهَا فِي الْعَصْرِ وَالْمَغْرِبِ، وَتَوَسُّطُهَا فِي الْعِشَاءِ، وَتَكُونُ السُّورَةُ الأُولَى قَبْلَ الثَّانِيَةِ وَأَطْوَلَ مِنْهَا، وَالْهَيْئَةُ الْمَعْلُومَةُ فِي الرُّكُوعِ وَالسُّجُودِ وَالْجُلُوسِ وَالْقُنُوتِ سِرًّا قَبْلَ الرُّكُوعِ وَبَعْدَ السُّورَةِ فِي ثَانِيَةِ الصُّبْحِ وَيَجُوزُ بَعْدَ الرُّكوعِ وَالدُّعَاءُ بَعْدَ التَّشَهُّدِ الثَّانِي، وَيَكُونُ التَّشَهُّدُ الثَّانِي أَطْوَلَ مِنَ الأَوَّلِ وَالتَّيَامُنُ بِالسَّلاَمِ وَتَحْرِيكُ السَّبَّابَةِ فِي التَّشَهُّدِ**

*"Ɗaga hannu lokacin kabbarar harama, da kusanta su ga kunnawa da faɗin "Rabbana wa Lakal Hamidahu" ga mai bin liman Sallah da kuma wanda yake Sallah shi kaɗai da faɗin "Amin" bayan ga mai Sallah shi kaɗai da wanda yake bin liman. Limami ba ya faɗinta sai a karatun sirri da Yin Tasbihi a cikin Ruku'u da kuma yin Addu'a a cikin Sujjada, da tsawaita karatua a sallar Asubahi da kuma Azahar. Da taƙaitawa a Sallar la'asar da Magriba. Da tsaikawa a Isha'i da Surar farko tafi ta biyu tsayi, da yin Ruku'u da sananniyar siffar Ruku'u da kuma Sujjada, da zama da Karanta al-Kunuti a ɓoye kafin ruku'u bayan karatun Sura a raka'a ta biyu ta Sallar Asuba. Ana iya yi bayan ɗagowa daga ruku'u da Addu'a bayan tahiyar ƙarshe, ana son tsawaitata fiye da ta biyu, da damantaw,a da sallama da karkaɗa ɗan yatsan nuni a tahiya"*

Ɗaga hannu lokacin kabbarar harama da kusanta su ga kunnawa

- ✓ Malamai sun haɗu akan kyawun aikata hakan ga Masallaci.
- ✓ Wa'il ɗan Hujur ya ce: "Ya ga Ma'aiki ya ɗaga hannayensa lokacin da ya yi kabbarar harama, ya kusanto su dab da kunnuwansa"

Faɗin “Rabbana Wa lakal Hamidahu” ga mai bin liman Sallah da kuma wanda yake Sallah shi kaɗai

- ✓ Ma’anar faɗinka “Rabbana Wa lakal Hamdu” shi ne Ya Ubangiji ka amsa mana kuma kai ne mafi cancantar a gode masa.
- ✓ Ana so faɗin hakan ga mai koyi da liman bayan faɗin liman “Sami’allahulliman Hamidahu”

Faɗin “Amin” bayan ga mai Sallah shi kaɗai da wanda yake bin liman. Limami ba ya faɗinta sai a karatun sirri.

- ✓ Liman da mai koyi da shi, da mai Sallah shi kaɗai duk zasu faɗi “Amin” kamar yadda Abdul Barr ya ce faɗin hakan shi ne mafi inganci.

Yin Tasbihi a cikin Ruku’u da kuma yin addu’a a cikin Sujjada

- ✓ Ana so ga mai Sallah ya yi Tasbihi yayin Ruku’u da Sujjada.
- ✓ Ana so ya tsawaitawa da tsananta addu’a a cikin Sujjada.
- ✓ Mafi ƙarancin Tasbihi shi ne faɗin “Subhana Rabbiyal Azim” sau ɗaya a ruku’u da kuma faɗin “Subhana Rabbiyal A’ala” sau ɗaya a sujjada.
- ✓ Ɗan Abbas yana cewa: Ma’aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: “Amma Ruku’u to ku girmama Ubangiji a cikinsa. Ita kuwa Sujjada ku tsananta wajen Addu’a domin akwai kyakkyawan tsammanin Allah zai amsa”

Tsawaita karatua a sallar Asubahi da kuma Azahar. Taƙaitawa a sallar la’asar da Magriba. Tsaikawa a Isha’i.

- ✓ An so Liman ya tsawaita karatun Sura a Sallar Asubahi da kuma Azahar.
- ✓ Ya gajarta karatun a Sallar Magriba da kuma La’asar.
- ✓ Ya tsakaita karatu (Tsakanin tsawaitawa da gajartawa) a Sallar Isha’i.
- ✓ Ma’anar tsawaitawa shi ne Liman ya karanta ɗaya daga cikin surorin da suke tsakanin Suratul Hujurati zuwa suratun Nazi’ati.
- ✓ Ma’anar gajartawa shi ne Liman ya karanta ɗaya daga cikin surorin da suke tsakanin suratush Shamsi zuwa Nasi
- ✓ Ma’anar tsakaitawa shi ne Liman ya karanta ɗaya daga cikin surorin da suke tsakanin “Abasa” zuwa Suratul Balad

- ✓ Ana so Liman ya kula da halin mabiyansa Sallah. Idan suna cikin walwala da nutsuwa sai ya tsaiwata karatu. In suna cikin ƙunci da damuwa sai ya gajarta.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Idan ɗayanku zai yi limanci toh ya sauƙaƙa domin a mabiyansa akwai mai rauni da mai shekaru da mara lafiya".

Surar farko tafi ta biyu tsaho.

- ✓ An so ga Liman ya yi dogon karatu a raka'ar farko, a raka'a ta biyu kuwa ya yi wadda bata kai ta farko ba. Kamar Suratul Alaƙ da kuma Suratul Kadr.
- ✓ An so idan Liman ya karanta Sura, to ya karanta wacce take ƙasa da ita.

yin ruku'u da sananniyar siffar Ruku'u da kuma Sujjada

- ✓ Wato ka tabbatar da hannayenka a kan gwiwarka, ka daidaita bayanka, kar ka yi ƙasa da kanka, ko sama da shi sannan ka kafe tsinin digadiganka.
- ✓ Wato ya sanya goshinsa da hancinsa a kan ƙasa, ya shimfiɗa tafukansa, ya nesanta cikinsa da cinyoyinsa, ya ɗan buɗa damtse.

ZAMA

- ✓ Wato a siffar Sallah shi ne ka shimfiɗa digadiganka na hagu ko ɗaura mazaunanka a kansa, ka kafe ƙafar dama yan yatsunka suna masu kallon alƙibla, ka ɗaura hannayenka a ƙarshen cinyarka.

Karanta Al-ƙunuti a sirrance kafin ruku'u bayan karatun Sura a raka'a ta biyu ta Sallar Asuba. Ana iya yi bayan ɗagowa daga ruku'u.

- ✓ Wato komawa ga Allah da kuma ƙanƙan da kai ta hanyar roƙonsa, tunkuɗe wani sharri ko jawo wani alheri.
- ✓ An so yinta a sallar Asubahi a sirrance kafin ruku'u a raka'a ta ƙarshe a allar Asubahi.

Addu'a bayan tahiyar ƙarshe ana son tsawaitata fiye da ta biyu.

- ✓ An so yin addu'a a tahiyar ƙarshe kafin sallama.
- ✓ An rawaito addu'o'i mabambanta daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

- ✓ Akwai abubuwa guda Huɗu muhimmai da ake neman tsari da su a cikin tahiya kamar haka:
  - Azabar Kabari
  - Azabar Jahannama
  - Fitinar rayuwa da mutuwa
  - Fitinar Dujal

Damantawa da sallama.

An so ga Liman da mai Sallah shi kaɗai da mai bin Sallah ya karkata kansa ɓangaran dama saboda abin da aka rawaito daga Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata gare shi.

Karkaɗa ɗan yatsan nuni a Tahiya.

- ✓ Wato karkaɗa shi hagu da dama.
- ✓ Ma'aiki ya kasance idan ya ɗaga ɗan yatsansa a Tahiya yana karkaɗa shi kuma ya yi addu'a

ABUBUWAN DA BA A SO MAI SALLAH YA AIKATA

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani akan abubuwan da aka so mai Sallah ya aikata, yanzu kuma zai yi bayani akan abubuwan da ba a so mai Sallah ya aikata.
- ✓ Duk abin da zai shagaltar da mai Sallah daga barin Kushu'i ana so ya bar shi kamar tunanin duniya.

**، وَيُكْرَهُ الاِلْتِفَاتُ فِي الصَّلاَةِ، وَتَغْمِيضُ الْعَيْنَيْنِ، وَالْبَسْمَلَةُ وَالتَّعَوُّذُ فِي الْفَرِيضَةِ وَيَجُوزَانِ فِي النَّفْلِ، وَالْوُقُوفُ عَلَى رِجْلٍ وَاحِدَةٍ إِلاَّ أَنْ يَطُولَ قِيَامُهُ، وَاقْتِرَانُ رِجْلَيْهِ وَجَعْلُ دِرْهَمٍ أَوْ غَيْرِهِ فِي فَمِهِ، وَكَذَلِكَ كُلُّ مَا يُشَوِّشُهُ فِي جَيْبِهِ أَوْ كُمِّهِ أَوْ عَلَى ظَهْرِهِ، وَالتَّفَكُّرُ فِي أُمُورِ الدُّنْيَا، وَكُلُّ مَا يَشْغُلُهُ عَنِ الْخُشُوعِ فِي الصَّلاَةِ.**

*"An karhanta waiwaye a cikin Sallah da rufe idanuwa da bayyana Bisimillah da kuma faɗin "A'uzubillahi" a sallar farilla amma suna halatta a Nafila da Tsayuwa akan ƙafa ɗaya sai in tsayuwar ta tsawaita da gwama*

*ƙafafu da Sanya Dirhami ko waninsa a cikin baki. Haka duk abin da zai ɗauke masa hankali a aljihunsa ko hannun rigarsa, ko bayansa da Tunani cikin abubuwan duniya da dukkan abin da zai shagaltar da shi daga samun Khushu'i a cikin Sallah"*

Waiwaye a cikin Sallah

- ✓ An so mai Sallah ya bar waiwaye ba tare da larura ba.
- ✓ Idan mai Sallah ya yi waiwayen da gangar jikinsa ta kaucewa alƙibla sallarsa ta rushe.

RUFE IDANUWA

- ✓ Don kar mai Sallah ya yi tunanin hakan abun buƙata ne ko kuma yin hakan na sanya kushu'i.
- ✓ An so ga wanda yake Sallah a gefen hanya ya runtse idonsa idan ya ji tsoron kallon abin da yake haramun ne.

Bayyana Bisimillah da kuma Faɗin "A'uzubillahi" a Sallar farilla amma suna halatta a Nafila.

- ✓ Imamu Malik ya ce: "Ba a karanta 'Bismillahir Rahmanir Rahim' a sallar farilla a wanda ake karatunta a bayyane ko a ɓoye, haka na riski Malamai a Madina amma a sallar Nafila babu laifi yinta ko barinta"

Tsayuwa a kan ƙafa ɗaya sai in tsayuwar ta tsawaita.

- ✓ Domin hakan wasa ne a cikin Sallah.

Gwama ƙafafu

- ✓ Wato ya gwama ƙafafunsa kamar wanda aka ɗaure ko kuma ya buɗe su da yawa.

Sanya Dirhami ko waninsa a cikin baki. Haka duk abin da zai ɗauke masa hankali a aljihunsa ko hannun rigarsa ko bayansa.

- ✓ Duk wani abu da mutum ya sanya a bakinsa mutuƙar bai hana shi karatun Sallah daidai ba ya zama makaruhi amma akasin Sallah ya ɓaci.
- ✓ Haka in ya ƙulla wani abu a cikin hannun rigarsa ko aljihunsa (Karar waya ko girgiɗinta) ya aikata makaruhi amma in haka ya hana shi cika rukuni daga cikin rukunan Sallah; sallarsa ta ɓaci.

Tunani cikin abubuwan duniya da dukkan abin da zai shagaltar da shi daga samun Khushu’I a cikin Sallah.

- ✓ Tunanin Duniya a cikin abin da ya shafi harkokin Kasuwanci da Siyasa da makamantansu domin haka zai tafiyar da Kushu'i a cikin Sallah.
- ✓ Idan tunanin ya sanya bai san mai ya sallata ba, lalle sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Idan tunanin ya kai shi ga kokonto; sai ya ciko abin da yake kokonton akansa.
- ✓ Duk wanda ya yi tunani akan sha’anin Lahira kamar Wuta da Aljanna ko kuma wani aiki da zai kusantar da shi ga Allah; wannan abin so ne.
- ✓ Faɗakuwa da kuma nazari cikin ayoyin da liman yake karantawa na daga cikin ababan da suke ƙara kushu'i a cikin Sallah.

FASALIN DA ZAI YI MAGANA AKAN KUSHU'I

لِصَّلاَةِ نُورٌ عَظِيمٌ تُشْرِقُ بِهِ قُلُوبُ الْمُصَلِّينَ وَلاَ يَنَالُهُ إِلاَّ الْخَاشِعُونَ

*“Sallah tana da wani haske mai girma, wadda take haska zukatan masallata, babu mai samunsa sai mai Kushu'i a cikin Sallah”*

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani a kan abubuwan da ba a so mai Sallah ya aikata, sai kuma ya shiga bayanin yadda mai Sallah zai samu Kushu'i.
- ✓ Ma’anar Kushu'i shi ne wani yanayi da yake bayyana a zuciya da kuma gangar jikin Masallaci wajen ƙanƙan da kai ga Allah. Haka Kushu'i na nufin bawa ya karkaɗe duniya da duk abin da yake cikinta.
- ✓ Yana da kyau Masallaci ya rinƙa bincikar kushu'insa domin shi ne abu na farko da za a fara ɗaukewa daga zuciyar bayi.
- ✓ Duk ibadar da aka yi ta a cikin Kushu'i tana da fifiko a kan wacce ba a yi ta da Kushu'i ba.
- ✓ Duk Sallar da aka yi ta da Kushu'i tana kankare zunuban da suka gabace ta.
- ✓ Kushu'i sababi ne na samun babban rabo a Duniya da kuma Lahira.

**فَإِذَا أَتَيْتَ إِلَى الصَّلَاةِ فَفَرِّغْ قَلْبَكَ مِنْ الدُّنْيَا وَمَا فِيهَا، وَاشْتَغِلَ بِمُرَاقَبَةِ مَوْلَاكَ الَّذِي تُصَلِّى لِوَجْهِهِ**

*"Idan kazo za ka fara Sallah ka karkaɗe zuciyarka daga Duniya da abin da yake cikinta, ka shagaltu da ganawa da majiɓancin lamarinka wannan da kake Sallah saboda shi"*

- ✓ Tsarkake zuciya daga barin tunane-tunanen duniya da abin da yake cikinta na ƙyale-ƙyale har ya halatto girman Ubangiji a zuciyarsa ta yadda zai samu jin daɗin ganawa da Mahaliccinsa.
- ✓ Ka haikaito a zuciyarka cewa duk abin da kake yi allah yana ganinka, yana tare da kai kuma ka kawar da kai daga dukkan abin da zai nisantaka da Mahaliccinka.

**وَاعْتَقِدْ أَنَّ الصَّلَاةَ خُشُوعٌ وَتَوَاضُعٌ للهِّ سُبْحَانَهُ بِالْقِيَامِ وَالرُّكُوعِ وَالسُّجُودِ وَإِجْلَالٌ وَتَعْظِيمٌ لَهُ بِالتَّكْبِيرِ وَالتَّسْبِيحِ وَالذِّكْرِ. فَحَافِظْ عَلَى صَلَاتِكَ فَإِنَّهَا أَعْظَمُ الْعِبَادَاتِ،**

*"Ka ƙudurce ita Sallah Kushu'i ce da ƙanƙan da kai ga Allah, ta hanyar tsayuwa da Ruku'u da Sujjada, da girmamawa da kuma kambamawa ta hanyar kabbarori da Tasbihi da kuma ambaton Allah. Don haka ka kiyaye dukkan sallolinka domin ita ce mafi girman ibadu"*

- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce wa Mu'awiyatu ɗan Hakan As-Sulamiy: "Lallai wannan Sallar ba ya halatta a a yi zantukan yau-da-kullum a cikinta; kaɗai dai ana yin Tasbihi da Kabbarori da kuma karatun Kur'ani"

**وَلَا تَتْرُكِ الشَّيْطَانَ يَلْعَبُ بِقَلْبِكَ وَيَشْغَلُكَ عَنْ صَلَاتِكَ حَتَّى يَطْمِسَ قَلْبَكَ وَيَحْرِمَكَ مِنْ لَذَّةِ أَنْوَارِ الصَّلَاةِ.**

*"Kar ka bar Shaiɗan ya yi wasa da zuciyarka ya shagaltar da kai daga sallarka don kar Shaiɗan ya yi wasa da zuciyarka ya haramta jin daɗin Sallah da kuma samun haskenta"*

- ✓ Bawa idan zai yi Sallah; ya rinƙa ji ita ce Sallarsa ta ƙarshe, hakan shi yafi kusa da ya ƙara masa Kushu'i a cikin Sallah kuma ya nesanta sheɗan daga wasa da zuciyarsa.
- ✓ Wani mutum yazo wuirn Ma'aiki y ace masa: Ka yi mini wa'azi amma ka taƙaita! Sai Ma'aiki y ace masa: "Idan zaka yi Sallah ka yi sallar mai ban kamata"
- ✓ Haka yazo a cikin hadisin Anas ɗan Malik Allah ya ƙara masa yadda: "Ka rinƙa tuna mutuwa a sallarka, domin bawa idan ya tuna mutuwa a sallarsa shi yafi kusa ya ingantata, ka yi Sallah irin wacce baka tunanin zaka sake yin irinta"

، فَعَلَيْكَ بِدَوَامِ الْخُشُوعِ فِيهَا فَإِنَّهَا تَنْهَى عَنْ الْفَحْشَاءِ وَالْمُنْكَرِ بِسَبَبِ الْخُشُوعِ فِيهَا،
فَاسْتَعِنْ بِاللهِ إِنَّهُ خَيْرُ مُسْتَعَانٍ

*"Don haka wajibi mutuƙar kana Sallah ka dawwama cikin Kushu'i domin ita (Sallah) tana hana bawa zuwarwa munanan ayyuka da kuma ababan ƙyamata. Ka nemi taimakon Allah domin shi ne mafi alherin wanda ake neman taimakonsa"*

- ✓ Yana da kyau Masallaci ya rinƙa lura da kuma zurfafa tunani cikin ma'anonin ayoyin ƙur'ani, ya shagaltar da zuciyarsa da wa'azuka da kuma labarai da suke cikinsa.
- ✓ Hakan, zai sanya zuciya ta yi taushi, Idanu su zubar da hawaye, a samu Kushu'i.
- ✓ Nesantar duk abin da zai hana samun Kushu'i a cikin Sallah kamar Sallah ya yi da mutum yake jin bayan gida ko bawali ko matsananciyar yunwa ko barin wayar hannu a kunne ko kuma zuciyarsa ba a nutse take ba sanadiyar wasu tunane-tunane.
- ✓ Haka Sallah lokacin da akawo abinci, ko kuma ya yi sallar a gurin da wani abu zai ja hankalinsa (Kamar gurin da yake da zane-zane ko hotuna, ka barin sautin talabijin ko radiyo a buɗe) duk suna daga cikin abubuwan da suke kore Kushu'i daga zuciyar Masallaci.

## BAYANI AKAN HALAYEN TSAYUWA DA KUMA DOGARO A CIKIN SALLAH

**فَصْلٌ: لِلصَّلاَةِ الْمَفْرُوضَةِ سَبْعَةُ أَحْوَالٍ مُرَتَّبَةٍ تُؤَدَّى عَلَيْهَا أَرْبَعَةٌ مِنْهَا عَلَى الْوُجُوبِ، وَثَلاَثَةٌ عَلَى الاِسْتِحْبَابِ، أَوَّلُهَا الْقِيَامُ بِغَيْرِ اسْتِنَادٍ ثُمَّ الْقِيَامُ بِاسْتِنَادٍ، ثُمَّ الْجُلُوسُ بِغَيْرِ اسْتِنَادٍ، ثُمَّ الْجُلُوسُ بِاسْتِنَادٍ، فَالتَّرْتِيبُ بَيْنَ هَذِهِ الأَرْبَعَةِ عَلَى الْوُجُوبِ إِذَا قَدَرَ عَلَى حَالَةٍ مِنْهَا وَصَلَّى بِحَالَةٍ دُونَهَا بَطَلَتْ صَلاَتُهُ، وَالثَّلاَثَةُ الَّتِي عَلَى الاِسْتِحْبَابِ هِيَ: أَنْ يُصَلِّيَ الْعَاجِزُ عَنْ هَذِهِ الثَّلاَثَةِ الْمَذْكُورَةِ عَلَى جَنْبِهِ الأَيْمَنِ، ثُمَّ عَلَى الأَيْسَرِ ثُمَّ عَلَى ظَهْرِهِ، فَإِنْ خَالَفَ فِي الثَّلاَثَةِ لَمْ تَبْطُلْ صَلاَتُهُ**

*"Sallar farilla tana da halaye guda bakwai da ake gabatar da ita, huɗu daga ciki ta wajibi ne, uku daga ciki mustabbi ne.*

Halayen da suke wajibi:

- Tsayuwa ba tare da dogaro ba.
- Tsayuwa da dogaro
- Zama ba tare da dogaro ba.
- Zama da dogaro.

Jeranta tsakanin waɗannan guda huɗun wajibi ne, idan Masallaci yana da ikon yin Sallah a ɗaya daga cikin halaye hɗun da suka gabata sai ya yi a akasinsu; sallarsa ta ɓaci"

- ✓ Cikin wannan fasalin Malam ya yi bayani dangane da halayen sallar mara lafiya tun daga yadda zai tsaya da yadda zai zauna da kuma yadda zai jingina.
- ✓ Wajibi ne Baligi ya yi Sallah cikin kowana hali ya samu kansa mutuƙar da hankali a tattare da shi.
- ✓ In ya kasa kawota a wani halin zai sallaceta a wani halin da zai iya, babu in da Sallah take faɗuwa akansa.
- ✓ Imrana ɗan Husain ya cewa Ma'aiki ayan da cutar Basir, sai ya tambayi Ma'aiki akan yadda zai yi Sallah? Sai y ace masa: "Ka yi Sallah a tsaye, in ba zaka iya b aka yi a zaune, in ba zaka iya ba ka yi ba kwance"

- ✓ Halin da aka fi so Masallaci ya yi Sallah shi ne tsayuwa cikakkiya, a halin rashin lafiya zai je hali na biyu (wato tsayuwa tare da dogaro). An karhanata jingina a jikin amai janaba ko kuma mai al'ada idan ya samu waninsu. Idan ya jingina a jikinsu; ya sake sallarsa akan lokaci.
- ✓ Idan hali na biyu ya ta'azzara toh yaje hali na uku (Wato zama ba tare da dogaro ba). Idan yana da iko akan hali na uku amma ya tafi ya yi Sallah a hali na huɗu; sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Idan ya kasa yin Sallah a cikin halaye ukun da suka gabata; sai ya yi Sallah a hali na huɗu (wato zama tare da dogaro) a jikin Gado ko Gini ko Kujera da makamantansu.

*"Halayen da suke na Mustahabbi: Wanda ba zai iya Sallah a hakayen da suka gabata ba; ya yi a kwiɓinsa na dama sannan na hagu sannan a rigingine. Idan ya saɓa jeranta wannan halayen uku sallarsa bata ɓaci ba"*

- ✓ Gajiyayye idan ba zai iya tsayuwa ba kuma ba zai iya zama ba babu laifi akansa ya yi sallarsa a rigiingine a ɓangaransa na dama yana mai fuskatntar alƙibla.
- ✓ Ya yi nuni da kansa, idan ba zai iya bay a yi da idanunsa, idan ba zai iya ba ya yi da yan yatsu.
- ✓ Idan ba zai iya yi da kwiɓinsa na dam aba; ya yi a kwiɓinsa na hagu.
- ✓ Idan ba zai iyayi a cikin halaye biyu da suka gabata ba; ya yi Sallah a rigingine ƙafafunsa na kallon aƙibla.

## SIFFOFIN DOGORON DA BAYA ƁATA SALLAH

**وَالاِسْتِنَادُ الَّذِي تَبْطُلُ بِهِ صَلاَةُ الْقَادِرِ عَلَى تَرْكِهِ هُوَ الَّذِي يَسْقُطُ بِسُقُوطِهِ، وَإِنْ كَانَ لاَ يَسْقُطُ بِسُقُوطِهِ فَهُوَ مَكْرُوهٌ**

*"Dogaron da sallar mai iko akan barinsa take ɓaci da shi, shi ne idan abin da Masallaci in ya dogara da shi ya faɗi shima zai faɗi, wannan shi yake ɓata Sallah. Amma idan mai Salah ba zai faɗi da faɗuwar abin da ya dogara da shi ba; wannan makaruhi ne"*

- ✓ Wato idan mai ikon yin Sallah ba tare da ya dogara da wani abu bay a yi Sallah tare da dogaro kamar kututture ko Katanga ko kujera ko tebur da makamntansu sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Idan ba zai faɗi da faɗuwar abin da ya dogara da shi ba wannan Makaruhi ne, sallarsa bata ɓaci ba.

**، وَأَمَّا النَّافِلَةُ فَيَجُوزُ لِلْقَادِرِ عَلَى الْقِيَامِ أَنْ يُصَلِّيَهَا جَالِسًا، وَلَهُ نِصْفُ أَجْرِ الْقَائِمِ.**

Malam Akhdari ya ce: “Amma wanda yake da iko ya yi sallar Nafila a tsaye sai ya yi ta a zaune sallarsa ta yi amma zai samu rabin ladan wanda ya yi a tsaye”

- ✓ Ita sallar Nafila tana halatta abubuwan da basa halatta a sallar farilla, kamar Sallah a zaune ga wanda yake da ikon yinta a tsaye.
- ✓ Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana cewa: “Wanda ya yi Sallah a zaune yana da rabin ladan wanda yayi a tsaye”
- ✓ Amma wanda aka yiwa rangwame sanadiyyar wani uzuri; yana da cikakken lada irin na wanda ya yi a tsaye kamar yadda Ma’aiki yake cewa: “Idan bawa yana rashin rashin lafiya ko kuma yana halin tafiya za a rubuta masa ladan abubuwan da yake gabatarwa na ibada kafin uzurin”

**وَيَجُوزُ أَنْ يَدْخُلَهَا جَالِسًا وَيَقُومَ بَعْدَ ذَلِكَ أَوْ يَدْخُلَهَا قَائِمًا وَيَجْلِسَ بَعْدَ ذَلِكَ إِلاَّ أَنْ يَدْخُلَهَا بِنِيَّةِ الْقِيَامِ فِيهَا فَيَمْتَنِعَ جُلُوسُهُ بَعْدَ ذَلِكَ**

*“Ya halatta ya fareta a tsaye sa’annan ya kammalata a zaune. Haka, ya halatta ya fareta a zaune ya kammalata a tsaye sai dai in ya shiga da niyyar zai kammalata a tsaye toh bai halatta ya zauna ba.*

- ✓ Wannan shi ne bambanci tsakanin sallar farilla da kuma ta nafila.

## FASALI

- ✓ Bayan Malam ya kammala bayani dangane da halayen da mara lafiya zai yi Sallah, a wannan fasalin kuma zai yi bayani ne dangane da wanda Sallah ta kubce masa sanadiyyar rashin lafiya ko kuma halin tafiya.

يَجِبُ قَضَاءُ مَا فِي الذِمَّةِ مِنْ الصَّلَوَاتِ وَلاَ يَحِلُّ التَّفْرِيطُ فِيهَا

*"Wajibi ne rama sallar da ta kufce bai halatta a jinkirtata ba"*

- ✓ Malam sai ya ce "Sallar da ta kufce" ba wacce aka barta ba da ganganci saboda kyautatawa mumini zato.
- ✓ Mumini baya barin Sallah da ganganci sai dai za ta iya kuɓuce masa bisa larura.
- ✓ Wajibi ne akan Baligi ya rama sallar da ya bari lokacinta (a bisa mantuwa ko da ganganci) ya fita ko da kuwa sallolin da ya bari kaɗan ne ko kuma da yawa, a halin zaman gida ya bar su ko kuwa a halin tafiya.
- ✓ Duk sallar da aka bar ta sanadiyyar gushewar hankali ko Al'ada ko kuma Biƙi; ba a ramata.
- ✓ Ita ramuwa ana yinta ne cikin kowana irin lokaci (Misali Sallar Azahar za a iya yin ramuwar a lokacin sallar Magirba).
- ✓ Baya halatta ga mai ramuwa ya jinkirta rama Sallah, ana so ya gabatar da ita duk lokacin da ya tuna kuma cikin gaggawa.

وَمَنْ صَلَّى كُلَّ يَوْمٍ خَمْسَةَ أَيَّامٍ فَلَيْسَ بِمُفَرِّطٍ

*"Wanda kullum ya rama sallar kwana biyar bai zama mai sakaci ba"*

- ✓ Wato ga wanda ya bar salloli da yawa.
- ✓ Amma mafi rinjaye shi ne ya rama abin da ya sawwaƙa ba tare da ya takura kansa ba ko kuma ya ƙuntata har kar neman abincinsa ba.
- ✓ Allah ne masani.

***وَيَقْضِيهَا عَلَى نَحْوِ مَا فَاتَتْهُ إِنْ كَانَتْ حَضَرِيَّةً قَضَاهَا حَضَرِيَّةً، وَإِنْ كَانَتْ سَفَرِيَّةً قَضَاهَا سَفَرِيَّةً سَوَاءٌ كَانَ حِينَ الْقَضَاءِ فِي حَضَرٍ أَوْ سَفَرٍ***

*"Zai ramata ne a irin yanayin data kufce masa, in a sallar zaman gidace ya rama ta a tsarin sallar zaman gida, in kuma a halin tafiya ne sai ya ramata a*

*yanayin sallar matafiyi, zai yi ramuwar ne ko a halin tafiya yake ko a halin zaman gida"*

- ✓ Lokacin da Sallah ta kubcewa baligi shi ne abin lura.
- ✓ Duk wanda Sallah ta kuɓuce masa a halin zaman gida; zama ramata cikakkiya.
- ✓ Wanda kuwa ta kubce masa a halin tafiya; zai ramata ne a taƙaicenta (Kasaru), ko kuwa yana zaune ne gida.
- ✓ Imamuna Malik (Allah ya ƙara masa yadda) ya ce: "Wanda ya bar Sallah da ganganci ko da mantuwa a halin tafiya sa'annan ya dawo wajen iyalansa, idan da ragowar lokacin sallar bai fit aba; zai kawota cikakkiya. In kuwa lokacin ya fita; zai ramata a taƙaice (Kasaru) domin zai ramata ne kamar yadda ta kuɓuce masa. Malik y ace: Wannan shi ne abin da na samu mutanen Madina akai"

**وَالتَّرْتِيبُ بَيْنَ الْحَاضِرَتَيْنِ وَبَيْنَ يَسِيرِ الْفَوَائِتِ مَعَ الْحَاضِرَةِ وَاجِبٌ مَعَ الذِّكْرِ، وَالْيَسِيرُ أَرْبَعُ صَلَوَاتٍ فَأَدْنَى، وَمَنْ كَانَتْ عَلَيْهِ أَرْبَعُ صَلَوَاتٍ فَأَقَلُّ صَلاَّهَا قَبْلَ الْحَاضِرَةِ وَلَوْ خَرَجَ وَقْتُهَا**

*"Jeranta tsakanin salloli guda biyu yayin zaman gida da mafi ƙarancin sallar da ta kubce da wadda za'a sallace ta a lokacin; wajibine yayin da aka tuna. Mafi ƙarancin salloli kuwa shi ne salloli huɗu zuwa ƙasa. Wanda ake binsa salloli hudu ko abinda bai kai haka ba zai fara sallatar sallar da take gabansa ko da lokacin ta zai fita"*

- ✓ Wajibi ne a jeranta sallollin ramuwa kamar tsakanin Azahar da la'asar ko kuma Magriba da Isha'I.
- ✓ Duk wanda bai jeranta tsakanin sallolin ramuwa ba da ganganci kuma da yalwataccen lokaci sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Zahirin abin da yake cikin bayanin Malam shi ne kamar yadda yazo a ikin Mudawwana "Duk wanda ya kasance ana binsa bashin salloli guda huɗu ko ƙasa; zai fara gabatar da wadda ake binsa bashin kafin ta lokacin ko da kuwa lokacinta zai fita"

- ✓ Abdullahi ɗan Mas’ud ya ce: “Lokacin da Mushirikai suka shagaltar damu daga barin salloli a lokacin yaƙin Gwalalo har dare ya raba, Annabi ya umarci Bilal ya yi kiran Sallah sannan aka yi Iƙama aka sallaci Azahar sannan aka sake Iƙama aka sallaci La’asar sannan aka sake Iƙama aka sallaci magriba sannan aka sake Iƙama aka sallaci Isha’i”

**، وَيَجُوزُ الْقضَاءُ فِي كُلِّ وَقْتٍ**

*“Ya halarta ramuwar sallar cikin kowane lokaci”*

- ✓ Wato lokacin dare ko kuwa na rana.
- ✓ Yana da kyau a nisanci lokutan hani kamar lokacin hudowar Rana da lokacin garjin Rana da lokacin faɗuwarta.

**. وَلاَ يَتَنَقَّلُ مَنْ عَلَيْهِ الْقضَاءُ وَلاَ يُصَلِّي الضُّحَى وَلاَ قِيَامَ رَمَضَانَ وَلاَ يَجُوزُ لَهُ إلاَّ الشَّفْعُ وَالْوَتْرُ وَالْفَجْرُ وَالْعِيدَانِ وَالْخُسُوفُ وَالاِسْتِسْقَاءُ،**

*“Wanda salloli suke kansa na ramuwa bayayin sallar nafila ko sallar walaha ko sallar asham sai dai shafa'I da wutri da raka'atanil fijr da sallar idi na ƙaramar Sallah da babbar Sallah da sallar kisfewar rana da wata da sallar roƙon ruwa”*

Baya halatta ga wanda ake binsa sallolin ramuwa ya shagaltu da sallolin nafila.

**وَيَجُوزُ لِمَنْ عَلَيْهِمُ الْقضَاءُ أَنْ يُصَلُّوا جَمَاعَةً إِذَا اسْتَوَتْ صَلاَتُهُمْ**

*“Yana halarta ga wanɗanda ake binsu Sallah na ramko su sallace ta a jam'I idan sallar su ta dai-daita”*

Wato ya halatta ga waɗanda ake binsu sallar ramuwa iri ɗaya da su gabatar da ita a jam’I, idan siffar sallar da adadinta sun zama ɗaya kamar Azahar da Azahar, la’asar da La’asar…

**. وَمَنْ نَسِيَ عَدَدَ مَا عَلَيْهِ مِنْ الْقضَاءِ صَلَّى عَدَدًا لاَ يَبْقى مَعَهُ شَكٌّ**

*"Wanda ya manta adadin abinda ake binsa na ramuwa, yayita Sallah har sai yaji a ransa ya biya duk abinda ke kansa"*

Duk wanda ya manta yawan sallolin da ake binsa; wajibi ne akansa ya yi ta rama Sallah bayan kowacce sallar lokacin har sai ya ji a ransa ya biya duk sallolin da ake binsa.

## BABI CIKIN RAFKANUWA

Wannan babi zai yi bayani ne akan hukuncin rafkanuwa da abin da yake jawota da siffarta da inda take faruwa da kuma yadda ake gyarata.

**وَسُجُودُ السَّهْوِ فِي الصَّلاَةِ سُنَّةٌ،**

*"Ita sujjadar rafkanuwa a Sallah Sunna ce"*

- ✓ Ma'aiki tsira da amincin Allaah su tabbata a gare shi ya ce: "Idan ɗayanku ya yi shakka a cikin sallarsa ta yadda bai san adadin abin da ya sallata ba, raka'a uku ko huɗu ce; ya bar shakka ya yi gini akan abin da yake da yaƙini sa'annan ya yi sujjada biyuy kafin ya yi sallama. Idan Raka'a biyar ya sallata sai ya cika ta zama shida, in kuwa huɗu ya sallata cikakku sai ya zama turmuzar hancii ne ga Shaiɗan"
- ✓ Haka Ma'aiki ya sake cewa cikin wani hadisin daban: "Duk wanda ya yi shakka a cikin Sallarsa; ya kirdaji daidai ya yi gini a kansa, sannan ya yi sallama sannan ya yi sujjada guda biyu bayan Sallama."
- ✓ Rakanuwa tana samuwa ta hanyoyi guda Uku:
    - Ko dai tauyewa,
    - Ko ƙarawa,
    - Ko kuma tauyewa da ƙarawa a lokaci guda.
- ✓ Ko da abubuwa Ukun da suka gabata sun maimaitu fiye da sau ɗaya; sujjada biyu za a yi masu kamar yadda yazo a cikin hadisi.
- ✓ Babu bambanci tsakanin Sallar farilla da ta nafila dangane da hukuncin rafkanuwa.
- ✓ Ba dukkan rafanuwa ce ake mata sujjada guda biyu ba. Idan aka samu rafkanuwa a cikin abin da yake rukuni ne na Sallah; sujjada ba ta gyara shi sai an zo da shi.

- ✓ Mustahabbai da Sunnoni marasa ƙarfi ba a yi masu sujjada.
- ✓ Ana yin sujjada ne kaɗai idan an bar Sunna mai ƙarfi. Ita kuwa Sunna mai ƙarfi guda shida ce:
    - Karatun Sura,
    - Bayyanawa ko ɓoye karatun a gurin da ya kamata a ɓoye ko a bayyana,
    - Barin kabbarori fiye da guda biyu ban da kabbarar harama.
    - Haka, wanda ya bar faɗin Sami'allahu Liman Hamidahu,
    - Tahiyar farko da zamanta,
    - Tahiyar ƙarshe da zamanta.
- ✓ Ba a yin sujjada a guraren da ba waɗancan ba a mazahabin Imamuna Malik

فَلِلنُّقْصَانِ سَجْدَتَانِ قَبْلَ السَّلَامِ بَعْدَ تَمَامِ التَّشَهُّدَيْنِ يَزِيدُ بَعْدَهُمَا تَشَهُّدًا آخَرَ،

وَلِلزِّيَادَةِ سَجْدَتَانِ بَعْدَ السَّلَامِ يَتَشَهَّدُ بَعْدَهُمَا وَيُسَلِّمُ تَسْلِيمَةً أُخْرَى

*"Idan mutum ya tauye zai yi sujjada biyu kafin sallama bayan kamala tahiyar karshe. Zai ƙara wata tahiyar bayansu, shi kuma ƙari ana yi masa sujjada bayan Sallama, zai yi tahiya sannan ya yi Sallama"*

- ✓ Wanda ya bar wani abu cikin Sunnoni masu ƙarfi da aka ambata zai yi sujjada biyu kafin Sallama bayan ya kammala tahiyar ƙarshe.
- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: "Wanda ya miƙe bai yi zaman tahiya na farko ba; in ya kammala Sallarsa ya yi sujja biyu kafin Sallama"
- ✓ Haka Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi rafkanuwa a cikin Sallah, ya yi sujjada guda biyu sa'annan ya yi tahiya kamar yadda Hadisin Imran ɗan Hussaini ya bayyana.

*"Wanda ya yi ƙari zai yi sujjada biyu bayan Sallama, zai yi tahiya a bayansu sa'annan ya yi wata Sallamar"*

- ✓ Wato wanda ya yi ƙari a cikin Sunnoni masu ƙarfi lamarinsa da sha'aninsa zai yi sujjada biyu ne bayan Sallama sa'annan ya zo da tahiya

sannan ya yi Sallama a bayyane kamar yadda yazo a cikin Hadisin Zul Yadaini.

**وَمَنْ نَقَصَ وَزَادَ سَجَدَ قَبْلَ السَّلَامِ،**

*"Wanda yayi ragi da kuma ƙari zai yi sujjada kafin Sallama"*

- ✓ Wato wanda ya tauye wani abu daga cikin Sunnoni masu ƙarfi sannan ya ƙara wani abu kaɗan daga cikinsu; hukuncinsa zai yi sujjada kafin Sallama domin ana rinjayar da ɓangaran tauyewar a kan ɓangaran ƙari.
- ✓ Babu saɓanin a tsakanin malamai cewa idan mai Sallah ya yi rafkanuwa guda biyu ko sama da haka sujjada guda biyu kafin Sallama za ta isar masa gabaɗaya.

**وَمَنْ نَسِيَ السُّجُودَ الْقَبَلِيَّ حَتَّى سَلَّمَ سَجَدَ إِنْ كَانَ قَرِيبًا، وَإِنْ طَالَ أَوْ خَرَجَ مِنَ الْمَسْجِدِ بَطَلَ السُّجُودُ وَتَبْطُلُ الصَّلَاةُ مَعَهُ إِنْ كَانَ عَلَى ثَلَاثِ سُنَنٍ أَوْ أَكْثَرَ مِنْ ذَلِكَ وَإِلاَّ فَلاَ تَبْطُلُ.**

*"Wanda ya manta sujjada ƙabli har ya yi Sallama zai yi sujjadar idan a kusa ne, idan kuwa ta tsawaita har ya fita daga masallaci sujjadar ta ɓaci, kuma tana ɓaci tare da Sallah, idan ya kasance Sunnoni Uku ya bari ko fiye da haka, idan kuma bai kai Sunnoni uku ba to Sallarsa bata ɓaci ba"*

- ✓ Wanda sujjada Kabli ta kama shi sannan ya manta bai zo da ita ba har ya yi Sallama zai yi sujjaada ne bayan Sallama da niyya ta ƙabli in lokaci bai tsawaita ba. In kuwa ya tsawaita har ta kai ga fita daga masallaci sujjadar ta ɓaci haka ita ma Sallar ta ɓaci in sababin sujjadar ya zama barin Sunnoni uku ne zuwa sama.

**وَمَنْ نَسِيَ السُّجُودَ البَعْدِيَّ سَجَدَهُ وَلَوْ بَعْدَ عَامٍ.**

*"Wanda ya manta sujjada ba'adi, zai yi ta ko da bayan shekara ne"*

- ✓ Wanda ya bar Sujjada ta bayan Sallama a bisa mantuwa ko da ganganci; zai zo da ita ko da kuwa bayan shekara ne a kowanne guri ya samu kan sa, ba lallai sai ya koma in da sujjadar ta kama shi ba.
- ✓ Zai yi kabbarar harama domin buɗe Sallar sannan ya zo da sujjadar.

- ✓ Zai iya gabatar da ita ko da kuwa a lokacin da aka hana yin Sallah ne.

**وَمَنْ نَقصَ فَرِيضَةً فَلاَ يُجْزِيهِ السُّجُودُ عَنْهَا. وَمَنْ نَقصَ الْفَضَائِلَ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ.**

*"Wanda ya tauye farilla; sujjadar rafkanuwa ba za ta gyara ba. Wanda ya tauye mustahabbi; babu sujjada a kansa"*

- ✓ Malamai sun haɗu a kan sujjadar rafkanuwa ba ta ɗauke tawaya cikin farillai, domin wajibi ne a zo da aikin da yake farilla ne in an samu dama in kuwa ba haka ba; Sallar ta ɓaci.
- ✓ Haka, wanda ya bar mustahabbi ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.
- ✓ Misali kamar wanda ya bar Alƙunutu a Sallar Asuba ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba, in kuwa ya yi sujjada kafin Sallama; Sallarsa ta ɓaci, sai ya sake wata.

**وَلاَ يَكُونُ السُّجُودُ الْقَبْلِيُّ إلاَّ لِتَرْكِ سُنَّتَيْنِ فَأَكْثَرَ. وَأَمَّا السُّنَّةُ الْوَاحِدَةُ فَلاَ سُجُودَ لَهَا إلاَّ السِّرَّ وَالْجَهْرَ، فَمَنْ أَسَرَّ فِي الْجَهْرِ سَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ، وَمَنْ جَهَرَ فِي السِّرِّ سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ**

*"Ba a yin sujjada Kabli sai an bar Sunnoni biyu zuwa sama, amma Sunna ɗaya ba a yi mata sujjada sai in sirrantawa ne ko bayyanawa. Wanda ya sirranta inda ake bayyanawa zai yi sujjada kafin Sallama, wanda kuma ya bayyana a inda ake sirrantawa to zai yi sujjada bayan Sallama"*

- ✓ Sujjada kafin Sallama ana yin ta ne idan masallaci ya bar Sunnoni guda biyu zuwa sama, kamar faɗin Sami'Allah Liman Hamdahu da kuma faɗin Allahu Akbar (Ban da kabbarar shiga Sallah).

**وَمَنْ تَكَلَّمَ سَاهِيًا سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ**

*"Wanda ya yi zance yana me rafkanuwa a cikin Sallah, to zai yi sujjada bayan Sallama"*

- ✓ Duk wanda ya yi wani zance kaɗan wanda ba ya cikin Sallah, kuma ba na gyaran Sallar ba ne a bisa rafkanuwa, Sallarsa bata ɓaci ba, zai sujjada bayan Sallama.
- ✓ Idan Liman yake bi kuwa; Liman ya ɗauke masa rafkanuwar.
- ✓ Haka, in ya yi zancen da ba ya cikin Sallah da ganganci Sallarsa ta ɓaci, sai ya sake wata.

، وَمَنْ سَلَّمَ مِنْ رَكْعَتَيْنِ سَاهِيًا سَجَدَ بَعْدَ السَّلَامِ،

*"Wanda ya yi Sallama a raka'a biyu bisa rafkanuwa zai yi sujjada bayan Sallama"*

- ✓ Wato wanda ya yi Sallama kafin cikar Sallah a bisa rafkanuwa yana mai ƙudurce cikar Sallarsa, daga baya ya gano bata cika ba, zai sake kabbarar harama sa'annan ya ciko ragowar Sallar kuma ya yi sujjada bayan Sallama.
- ✓ Idan kuma bai tuna ba sai bayan dogon lokaci ko kuma ya yi nisa da in da ya yi Sallar; Sallarsa ta ɓaci, wajibi ne ya sake wata.

وَمَنْ زَادَ فِي الصَّلَاةِ رَكْعَةً أَوْ رَكْعَتَيْنِ سَجَدَ بَعْدَ السَّلَامِ وَمَنْ زَادَ فِي الصَّلَاةِ مِثْلَهَا بَطَلَتْ،

*"Wanda ya ƙara raka'a ɗaya ko raka'a biyu zai yi sujjada bayan Sallama, wanda ya ƙara kwatankwacin adadin raka'o'in Sallah, Sallarsa ta ɓaci"*

- ✓ Kari ɗan kaɗan a cikin rukunai ba ya ɓata Sallah.
- ✓ Mafi yawan ƙari a Sallah mai raka'a biyu ita ce raka'a ɗaya, in ya ƙara kwatankwacinta Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ A Sallah mai raka'a uku kuma, raka'a biyu, in ya ƙara kwatankwacinta Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Mai raka'a huɗu kuma raka'a uku, in ya ƙara kwatankwacinta Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Hadisi ya zo cewa Ma'aiki ya yi Sallah raka'a biyar. Wasu daga cikin Sahabai suka tambaye shi shin an ƙara yawan Raka'o'in? Ma'aiki ya ce: "A'a". sai ya sake mayar da ƙafafunsa irin yadda ake zaman Sallah ya yi sujjada biyu.

وَمَنْ شَكَّ فِي كَمَالِ صَلَاتِهِ أَتَى بِمَا شَكَّ فِيهِ، وَالشَّكُّ فِي النُّقْصَانِ كَتَحَقُّقِهِ

*"Wanda ya yi shakka cikin cikar Sallarsa; yazo da abin da yake shakka, domin shakka a cikin tauye Sallah, kamar tabbatar da tauyewar ce"*

- ✓ Wanda yake ba shi da cutar wasuwasi idan ya yi shakka game da cikar Sallarsa bai san nawa ya sallata ba, Huɗu ce ko Uku; ya watsar da

shakkar ya yi gini a kan yaƙini, wato ya ƙudurce Uku ya sallata, sai ya ciko ragowar sannan ya yi sujjada bayan Sallama.

فَمَنْ شَكَّ فِي رَكْعَةٍ أَوْ سَجْدَةٍ أَتَى بِهَا وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلَامِ

*"Wanda ya yi shakkar ƙari cikin raka'a ko sujjada to yazo da ita sannan ya yi sujjada bayan Sallama"*

- ✓ Zai yi sujjada ne saboda shakkar da ta aure shi ta ƙari a cikin Sallarsa.

✓ ، وَإِنْ شَكَّ فِي السَّلَامِ سَلَّمَ إِنْ كَانَ قَرِيبًا وَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ، وَإِنْ طَالَ بَطَلَتْ صَلَاتُهُ

*"Wanda ya yi shakkar yin Sallama; ya yi Sallamar idan a kusa ne, babu sujjada a kansa, idan kuwa lokacin ya tsawaita, to Sallarsa ta ɓaci"*

- ✓ Wanda ya yi shakka a ƙarshen Sallarsa shin ya yi Sallama ko bai yi ba; ya yi Sallamar mutuƙar bai bar gurin Sallar ba kuma bai juyawa alƙibla baya ba, babu sujjadar rafkanuwa a kansa.
- ✓ In kuwa har ya fita daga masallaci ko kuwa ya bar gurin Sallar amma bai ɗau lokaci mai tsayi ba; ya koma ya yi kabbarar harama ya zauna ya yi tahiya kuma ya yi Sallama sannan ya yi sujjada bayan Sallama.
- ✓ In kuwa ya tsawaita; Sallar ta rushe.

. وَالْمُوَسْوَسُ يَتْرُكُ الْوَسْوَسَةَ مِنْ قَلْبِهِ، وَلاَ يَأْتِي بِمَا شَكَّ فِيهِ وَلَكِنْ يَسْجُدُ بَعْدَ السَّلَامِ سَوَاءٌ شَكَّ فِي زِيَادَةٍ أَوْ نُقْصَانٍ

*"Mai yawan kokwanto ya bar kokwantonsa kar yazo da abin da yake kokwanto a kansa amma zai yi sujjada bayan Sallama, wato ya yi kokwantan ne cikin ƙari ko ragi"*

- ✓ Wanda shakka ta aure shi a cikin Sallar; ya watsar da abin da yake shakka, ka da ya damu da yawan shakkar domin cut ace kuma aikin Shaiɗan ne wand aba shi da magani face watsar da ita.
- ✓ Duk wanda shakka ta aure shi; ko da yaushe zai yi sujjada bayan Sallama ne, ba zai gyara Sallar ba.
- ✓ Mai shakka ba ya iya kiyaye abubuwan da ya aikata a cikin Sallarsa a kowana lokaci, amma wanda ya yi rafkanuwa kuwa yana da yaƙinin ƙari ko ragi da ya afku a cikin Sallarsa, sai ya yi gini akan yaƙininsa.

. وَمَنْ جَهَرَ فِي الْقُنُوتِ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ وَلَكِنَّهُ يُكْرَهُ عَمْدُهُ،

*"Duk wanda ya bayyana karatun Alƙunut, babu sujjada a kansa, sai dai aikata hakan bisa ganganci makaruhi ne"*

- ✓ Ɓoye ta mustahbbi ne a Mazahabar Malikiyya.
- ✓ Babu laifi a bayyanata, sanadiyyar wata musiba ko annoba da ta samu al'umma.
- ✓ Ma''aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana bayyana alƙunuti, yana ɗaga hannayensa, waɗanda suke bayansa suna cewa Amin.
- ✓ Imamu Ash'hab ya ce: "Duk wanda ya yi sujjada kafin Sallama bisa ganganci saboda ya bayyana alƙunuti; Sallarsa ta ɓaci"

وَمَنْ زَادَ السُّورَةَ فِي الرَّكْعَتَيْنِ الأَخِيرَتَيْنِ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ

*"Wanda ya ƙara karatun Sura a Raka'o'in ƙarshe babu komai a kansa"*

- ✓ *Wato cikin Raka'o'i biyun ƙarshe na Sallar Azahar da La'asar da kuma Isha'i, ko kuma raka'ar ƙarshe ta Sallar Magriba ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba domin Fatiha kaɗai ake karantawa a cikinsu.*

، وَمَنْ سَمِعَ ذِكْرَ مُحَمَّدٍ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ وَهُوَ فِي الصَّلاَةِ فَصَلَّى عَلَيْهِ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ، سَوَاءٌ كَانَ سَاهِيًا أَوْ عَامِدًا أَوْ قَائِمًا أَوْ جَالِسًا،

*"Duk wanda ya ji an ambaci sunan Annabi alhalin yana cikin Sallah; sai ya yi masa salati, babu komai a kansa, ya aikata hakan a kan rafkanuwa ko kuma bisa ganganci a zaune, ko a tsaye"*

- ✓ Babu sujjadar rafkanuwa a kan mai Sallah in ya yi wa Ma'aiki Salati ya yin da ya ji an ambaci sunansa a cikin Sallar Farilla ko kuma ta Nafila saboda tsananin soyayya da kuma girmamawa ga Ma'aiki.

وَمَنْ قَرَأَ سُورَتَيْنِ فَأَكْثَرَ فِي رَكْعَةٍ وَاحِدَةٍ أَوْ خَرَجَ مِنْ سُورَةٍ إِلَى سُورَةٍ، أَوْ رَكَعَ قَبْلَ تَمَامِ السُّورَةِ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ فِي جَمِيعِ ذَلِكَ

*"Wanda ya karanta Surori guda biyu, ko sama da haka a cikin raka'a ɗaya ko ya fita daga wata Surar zuwa wata Surar, ko ya yi ruku'u kafin ya cika sura, duk waɗannan abubuwan babu komai a kansa"*

- ✓ Wato babu sujjadar rafkanuwa ga wanda ya aikata hakan a bisa mantuwa ko kuma da ganganci.
- ✓ Makaruhi ne Liman ya zaɓi wasu Surori kaɗai ya yi ta maimaita su a Sallarsa.
- ✓ Makaruhi ne fara karatun Sura ba a ƙarasa ba.
- ✓ Haka, makaruhi ne karanta sama da sura ɗaya a Sallar farilla, sai dai ga mai bin Liman a Sallar da ake ɓoye karatu, babu laifi ya karanta fiye da Sura ɗaya in ya ji tsoron shiru ɗin zai jawo masa tunanin duniya, ya kuma tafiyar masa da kushu'insa.

، وَمَنْ أَشَارَ فِي صَلاَتِهِ بِيَدِهِ أَوْ رَأْسِهِ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ،

*"Wanda ya yi nuni da hannunsa ko da kansa a cikin sallarsa, babu komai a kansa"*

- ✓ Wato babu sujjadarr rafkanuwa a kansa, sai dai hakan yana kama da wasa da aka yi hani da aikata shi a cikin Sallah.
- ✓ Babu laifi a yi nuni da hannu, ko da kai don mayar da Sallama ko kuma gargaɗi.
- ✓ Babu laifi in aka tambayi mai Sallah ya ba da amsa ta hanyar amfani da kansa ko kuma hannunsa, mutuƙar haka ba zai shagaltar da shi daga barin samun kushu'i ba kamar yadda hakan yazo a ƙissar Nana Ai'isha Allah Ya ƙara mata yadda.

وَمَنْ كَرَّرَ الْفَاتِحَةَ سَاهِيًا سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ، وَإِنْ كَانَ عَامِدًا فَالظَّاهِرُ الْبُطْلاَنُ

*"Wanda ya maimaita karatun Fatiha bisa rafkanuwa zai yi sujjada bayan Sallama, amma idan bisa ganganci ne a zahiri Sallar sa ta ɓaci"*

- ✓ Duk wanda ya maimaita Fatiha sau biyu a raka'a ɗaya bisa rafkanuwa zai yi sujjada bayan Sallama.
- ✓ Wanda ya aikata da ganganci; a mafi rinjayen zantukan malamai Sallarsa ta ɓaci.

، وَمَنْ تَذَكَّرَ السُّورَةَ بَعْدَ انْحِنَائِهِ إِلَى الرُّكُوعِ فَلاَ يَرْجِعُ إِلَيْهَا،

*"Wanda ya tuna karatun Sura bayan ya yunƙura zai yi ruku'u ba zai dawo gareta ba"*

- ✓ *Wato wanda zai aikata wajibi ba zai dawo baya saboda Sunna ba, kaɗai dai zai yi ruku'insa sannan bayan ya cika Sallah ya yi sujjada bayan Sallama saboda barin Sunna mai ƙarfi (wato karatun Sura).*

**وَمَنْ تَذَكَّرَ السِّرَّ أَوْ الْجَهْرَ قَبْلَ الرُّكُوعِ أَعَادَ الْقِرَاءَةَ، فَإِنْ كَانَ ذَلِكَ فِي السُّورَةِ وَحْدَهَا أَعَادَهَا وَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ، وَإِنْ كَانَ فِي الْفَاتِحَةِ أَعَادَهَا وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ، وَإِنْ فَاتَ بِالرُّكُوعِ سَجَدَ لِتَرْكِ الْجَهْرِ قَبْلَ السَّلاَمِ وَلِتَرْكِ السِّرِّ بَعْدَ السَّلاَمِ سَوَاءٌ كَانَ مِنَ الْفَاتِحَةِ أَوِ السُّورَةِ وَحْدَهَا.**

*"Wanda ya manta sirrantawa ko bayyanawa kafin ya yi ruku'u to ya maimaita su: idan ya kasance karatun Sura ne kawai, to iya ita zai maimaita, babu sujjada a kansa, idan kuwa karatun Fatiha ne zai sake ta sannan ya yi sujjada bayan Sallama. Idan har ya yi ruku'u to zai yi sujjada kafin Sallama saboda barin bayyanawa , idan kuma sirrantawa ne, zai yi sujjada bayan Sallama, hakan cikin karatun Fatiha ne ko Sura"*

- ✓ Wanda ya bayyana karatu a wurin da ake ɓoyewa, ko kuma ya aikata akasin haka sannan ya tuna kafin ya ƙulla ruku'u; zai maimaita sirrantawa in sirrantawa ne bai yi ba, ko kuma ya bayyana idan bayyanawar ce bai yi ba.
- ✓ Idan kuwa ya tuna bayan ya yi ruku'u n da ya ɓoye a in da ake bayyanawa zai yi sujjada bayan Sallama, domin ƙari ya yi a cikin Sallah. Idan kuwa ɓoyewa ya yi a in da ake bayyanawa zai yi sujjada kafin Sallama, domin ragi ya yi a cikin Sallah.
- ✓ Idan karatun Sura ya maimaita kafin ruku'u; babu sujjada a kansa.
- ✓ Idan kuma na Fatiha ne; zai yi sujjada bayan Sallama, saboda ya yi ƙari.

**وَمَنْ ضَحِكَ فِي الصَّلاَةِ بَطَلَتْ سَوَاءٌ كَانَ سَاهِيًا أَوْ عَامِدًا، وَلاَ يَضْحَكُ فِي صَلاَتِهِ إِلاَّ غَافِلٌ مُتَلاَعِبٌ،**

*"Wanda ya yi dariya a cikin Sallah, Sallarsa ta ɓaci, ya aikata a bisa rafkanuwa ne ko da ganganci, ba kowa yake dariya a cikin Sallarsa ba sai marafkani mai wasanni"*

- ✓ Dariya a cikin Sallah na daga cikin abubuwan da suke ɓata Sallah.

- ✓ Duk wanda ya yi dariya Liman ne ko mai bin Sallah ne, ko mai Sallah ne shi kaɗai wajibi ne ya sake Sallar gabaɗayanta, amma ba zai sake alwala ba.
- ✓ Idan Liman ya yi dariya a bisa rafkanuwa ko kuma ta rinjaye shi sanadiyyar wani abu da ya tuna ko kuma ya ji an furta; wajibi ne ya jawo wani daga cikin masu binsa ya maye gurbinsa domin shi Sallarsa ta ɓaci amma ban da ta masu bin sa mutuƙar su ma bas u yi dariyar ba.
- ✓ Wanda yake dariya a cikin Sallarsa gafalallai ne, wanda ba ya ganin girman Ubangijinsa kuma Majiɓancin lamarinsa.
- ✓ Hakan kuma, alamu ne na cewa ba shi da kushu'i wanda shi ne ginshiƙin Imani.
- ✓ Mai dariya a cikin Sallah ya zama abin wasan Shaiɗan wanda zai taɓar da shi kuma ya tozarta shi.

**وَالْمُؤْمِنُ إِذَا قَامَ لِلصَّلاَةِ أَعْرَضَ بِقَلْبِهِ عَنْ كُلِّ مَا سِوَى اللهِ سُبْحَانَهُ وَتَرَكَ الدُّنْيَا وَمَا فِيهَا، حَتَّى يُحْضِرَ بِقَلْبِهِ جَلاَلَ اللهِ سُبْحَانَهُ وَعَظَمَتَهُ، وَيَرْتَعِدُ قَلْبُهُ وَتَرْهَبُ نَفْسُهُ مِنْ هَيْبَةِ اللهِ جَلَّ جَلاَلُهُ، فَهَذِهِ صَلاَةُ الْمُتَّقِينَ**

*"Amma Mumini idan zai yi Sallah yana karkaɗe zuciyarsa daga dukkan wanin Allah, yana barin duniya da abin da yake cikinta, yana halarto girman Allah da ƙasaitarsa, zuciyarsa tana raurawa, ransa yana cika da ganin girman Allah, wannan shi ne Sallar masu taƙawa"*

- ✓ Malam yana nuni a kan muhimmancin ganin girman Allah a cikin Sallah, da kuma kiyaye duk abin da zai shagaltar da Masallaci cikin al'amuran Duniya.
- ✓ Ya nemi taimakon Allah ta hanyar fakewa gare shi da kuma ƙanƙan da kai izuwa gare shi.
- ✓ Wanda Sallarsa ta zama a irin wannan yanayi; ita ce irin Sallar masu tsoron Allah, waɗanda suke da yaƙinin Allah yana tare da su a cikin dukkan al'amuransu kuma yana sane da abin da yake cikin ƙoƙon zuciyarsu.

، وَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ فِي التَّبَسُّمِ،

*"Babu laifi yin murmushi ga mai Sallah"*

- ✓ Wato babu sujjadar rafkanuwa ga wanda ya ɗan yi murmushi a cikin Sallarsa, ya saki fuskarsa, sai dai hakan makaruhi ne, in ya yi yawa Sallarsa ta ɓaci domin hakan na daga cikin aiki mai yawa da baya cikin Sallah.

وَبُكَاءُ الْخَاشِعِ فِي الصَّلاَةِ مُغْتَفَرٌ،

*"Kuka saboda tsoron Allah a cikin Sallah, abin gafartawa ne"*

- ✓ Wato ana gafartawa mai Sallah da kuka ya rinjaye shi saboda jin tsoron Allah, irin wannan ba ya ɓata Sallah kaɗai dai mai yinsa yana samun lada.
- ✓ Alƙama ɗan Waƙas Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Na yi Sallar Isha'i a bayan Sayyadina Umar, ya karanta Suratu Yusuf, lokacin da yazo wata gaɓa ta ambaton Annabi Yusuf sai ya fashe da kuka, ina ƙarshen Sahu amma sai da naji shassheƙarsa"
- ✓ Wanda ya yi kuka ba saboda tsoron Allah, ba ya yi ne saboda wani yanayi na rayuwa da yake ciki ko kuma ya tuna da wata matsalarsa ta duniya ba; wannan ba ya ciki masu kukan da ake gafartwa.
- ✓ Duk kukan da aka ƙirƙire shi hukuncinsa kamar hukuncin magana ne a cikin Sallah.

وَمَنْ أَنْصَتَ لِمُتَحَدِّثٍ قَلِيلاً فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ

" *Wanda ya saurari mai zance kaɗan yana cikin Sallah, babu komai a kansa"*

- ✓ *Wato wanda ya saurari wani yana wata magana ko rediyo to talabijin sauraro ɗan kaɗan; babu komai a kansa, ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.*
- ✓ *In kuwa sauraran ya yi tsaho; Sallarsa ta rushe domin ya shagaltu da wani abun da ba it aba.*
- ✓ *Haka, wanda ya karanta wani abu da baya cikin Sallah (kamar wani rubutu a cikin masallaci, ko ya ɗakko wayarsa yana duba waye yake*

*kiransa, ko kuma yana karanta yadda zai kasheta, ko karanta wata riga mai rubutu da wani yake Sallah da ita) duk wanda ya aikata ɗaya daga cikinsu ko makamantansu Sallarsa ta ɓaci.*

، وَمَنْ قَامَ مِنْ رَكْعَتَيْنِ قَبْلَ الْجُلُوسِ، فَإِنْ تَذَكَّرَ قَبْلَ أَنْ يُفَارِقَ الأَرْضَ بِيَدَيْهِ وَرُكْبَتَيْهِ رَجَعَ إِلَى الْجُلُوسِ وَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ، وَإِنْ فَارَقَهَا تَمَادَى وَلَمْ يَرْجِعْ وَسَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ، وَإِنْ رَجَعَ بَعْدَ الْمُفَارَقَةِ وَبَعْدَ الْقِيَامِ سَاهِيًا أَوْ عَامِدًا صَحَّتْ صَلاَتُهُ وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ

"Wanda ya miƙe bai zauna ba bayan raka'a ta biyu; Idan ya tuna kafin ya rabu da ƙasa da hannayensa da gwiwarsa to ya koma ya zauna, babu komai a kansa. idan kuwa ya rabu da kasa to ya zarce kar ya dawo sannan ya yi sujjada kafin Sallama. Idan kuma ya dawo ya zauna bayan ya rabu da ƙasa ya miƙe bisa rafkanuwa ko da gangan Sallarsa ta yi, zai yi sujjada bayan Sallama"

- ✓ Malam yana bayani dangane da halin wanda yake Sallah mai raka'a huɗu ku uku, lokacin da yazo zaman raka'a ta biyu sai ya manta bai yi zaman tahiya ba.
- ✓ Irin wannan, hukuncinsa ba ya fita daga ɗayan abu uku:
- ✓ Ko dai ya tuna bai yi zaman tahiyar ba bayan ɗagowarsa daga sujjada kafin ya ɗauke hannuwansa da kuma gwiwarsa daga ƙasa, irin wannan halin babu komai a kansa, ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.
- ✓ Idan kuwa ya rabu da ƙasa da hannayensa da kuma gwiwarsa bai dawo ba; zai yi sujjada kafin Sallama kasancewar ya tauye tahiya wadda take Sunna ce mai ƙarfi.
- ✓ Idan ya miƙe sannan ya sake dawowa ya zauna domin zaman tahiya da ganganci ko bisa rafkanuwa; Sallarsa ta yi kaɗai dai zai yi sujjada bayan Sallama saboda ya yi ƙari.

. وَمَنْ نَفَخَ فِي صَلاَتِهِ سَاهِيًا سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ، وَإِنْ كَانَ عَامِدًا بَطَلَتْ صَلاَتُهُ

"Wanda ya yi busa a cikin Sallah bisa rafkanuwa, to zai yi sujjada bayan Sallama, idan kuwa da ganganci ne Sallarsa ta ɓaci"

- ✓ Irin wannan halin baya fita da hali guda biyu:
- ✓ Ko dai masallaci ya yi busa da bakinsa mai ƙarfi ta yadda wasu harufa zasu bayyana saboda ƙarfin busar, hakan, daidai yake da Magana idan ana iya fahimtar wasu harufa daga busar, idan ya aikata hakan abisa ganganci Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Ko kuma ya yi busar da hancinsa, wannan ba ya ɓata Sallah, ya aikata hakan a kan kuskure ko kuwa da ganganci.

. وَمَنْ عَطَسَ فِي صَلاَتِهِ فَلاَ يَشْتَغِلُ بِالْحَمْدِ وَلاَ يَرُدُّ عَلَى مَنْ شَمَّتَهُ وَلاَ يُشَمِّتُ عَاطِسًا، فَإِنْ حَمِدَ اللهَّ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ

"Wanda ya yi atishawa yana Sallah, kar ya shagaltu da cewa "Alhamdulillah", ba a mayar da gaisuwa ga wanda ya ce "Yarhamukallah", shi ma ba zai gaisar da mai atishawa ba, idan kuma shi mai Sallah ya ce "Alhamdulillah"babu komai a kansa"

- ✓ Wato Masallaci ba zai furta "Alhamdulillah" ba yayin da ya yi atsiahwa a cikin Sallah ba amma in ya furta babu laifi a kansa, wato babu sujjadar rafkanuwa akansa.
- ✓ Idan kuma wani ya yi atishawa ya ce "Alhamdulillah" ba zai ce masa "Yarhamukallah" ba a yayin da yake cikin Sallah, idan kuwa ya yi gangancin hakan Sallar ta ɓaci.

. وَمَنْ تَثَاءَبَ فِي الصَّلاَةِ سَدَّ فَاهُ، وَلاَ يَنْفُثُ إِلاَّ فِي ثَوْبِهِ مِنْ غَيْرِ إِخْرَاجِ حُرُوفٍ.

"Wanda ya yi hamma a cikin Sallah; ya toshe bakinsa, kar ya tofar da kaki sai a cikin tufafinsa, ba tare da wani harafi ya fita ba"

- ✓ Kamar yadda Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yake cewa: "Idan ɗayanku ya yi Hamma; ya rufe bakinsa domin Shaiɗan yana shiga"
- ✓ Idan masallaci ya yi kaki sanadiyyar rashin lafiya ko wata matsala; kar ya tofar da kakin a gefen damansa ko hagunsa ko kuma gabansa kaɗai ya tofa a cikin aljihunsa ko kuma gefen rigarsa ko wani tsumma da yake goge-goge da shi a hankali ba tare da fitar wani sauti ba.

وَمَنْ شَكَّ فِي حَدَثٍ أَوْ نَجَاسَةٍ فَتَفَكَّرَ فِي صَلاَتِهِ قَلِيلاً، ثُمَّ تَيَقَّنَ الطَّهَارَةَ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ

"Wanda yayi kokwanto cikin kari ko najasa alhalin yana cikin Sallah, sai ya yi tunani kaɗan sannan ya samu yaƙinin yana da tsarki, babu komai a kansa"

- ✓ Irin yana faruwa da ɗayan mutum biyu:
  - Ko dai wanda shakka ta aure shi ko da kuwa yana samun shakkar ne sau ɗaya ko sau biyu a cikin kowacce Sallah lamarinsa da sha'aninsa zai jefar da abin da yake shakkar, ya yi gini akan abin da yake da yaƙini wato tsarki.
  - Ko kuma, mutumin da shakka ba ta aure shi ba lamarinsa da sha'aninsa zai yi gini a kan rashin najasar sai dai in ya samu yaƙinin samuwar najasar.
  - Ma'aiki tsira da maincin Allah su tabbata a gare shi ya gayawa wannan da yake yawan jin motsi a dubararsa cewa "Kar ya yanke Sallarsa har sai yaji fitar iska ko kuma wari"

. وَمَنِ الْتَفَتَ فِي الصَّلاَةِ سَاهِيًا فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ، وَإِنْ تَعَمَّدَ فَهُوَ مَكْرُوهٌ،

"Wanda ya yi waiwaye a cikin Sallah yana mai rafkanuwa, babu komai a kansa, idan kuwa da ganganci ne; ya aikata makaruhi"

- ✓ Wanda ya yi waiwaye a cikin Sallah tabbas Shaiɗan ne ya wafci wani abu daga cikin Sallarsa saboda faɗin Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi: "Allah ba ya gushewa yana fuskantar bawansa a cikin Sallah mutuƙar bai yi waiwaye ba, In ya yi; sai ya bar shi"

وَإِنِ اسْتَدْبَرَ الْقِبْلَةَ قَطَعَ الصَّلاَةَ

"Wanda ya juyawa alƙibla baya, Sallarsa ta ɓaci"

- ✓ Waiwaye ba ya ɓata Sallah mutuƙar masallaci bai kaucewa alƙibla da dukkan gangar jikinsa ba, in kuwa ya kauce mata Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Fuskantara alƙibla yana daga cikin sharuɗan Sallah.

وَمَنْ صَلَّى بِحَرِيرٍ أَوْ ذَهَبٍ أَوْ سَرَقَ فِي الصَّلاَةِ أَوْ نَظَرَ مُحَرَّمًا فَهُوَ عَاصٍ وَصَلاَتُهُ صَحِيحَةٌ.

"Wanda ya yi Sallah da alhariri ko zinare ko ya yi sane a cikin Sallah, ko ya kallaci haramun, Sallarsa ta yi, amma shi mai saɓo ne"

- ✓ Aikata waɗancan abubuwan guda huɗu da suka gabata a cikin Sallah haƙiƙa babban saɓo ne kuma haramun ne, amma tare da haka basa ɓata Sallah in basu yi tsaho ba.
- ✓ Ko shakka babu wanda ya aikata waɗancan; ladan Sallarsa tauyayye ne, asali ma bai cacanta ya samu ladan wannan Sallar ba.

. وَمَنْ غَلِطَ فِي الْقِرَاءَةِ بِكَلِمَةٍ مِنْ غَيْرِ الْقُرْآنِ سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ، وَإِنْ كَانَتْ مِنَ الْقُرْآنِ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ إِلاَّ أَنْ يَتَغَيَّرَ اللَّفْظُ أَوْ يَفْسُدَ الْمَعْنَى فَيَسْجُدَ بَعْدَ السَّلاَمِ.

"Wanda ya yi kuskuren karatu da wata kalmar bata Al-ƙur'ani ba; ya yi sujjada bayan Sallama, idan kuwa a cikin Alƙur'ani take to babu sujjada a kansa, sai dai idan ya canzaa lafazi ko ya ɓata ma'ana; zai yi sujjada bayan Sallama"

- ✓ Hukuncin cakuɗa karatun ƙura'ani a Sallah da wasu kalmomin daban kamar hukuncin zancen da aka yi ne bisa rafkanuwa a cikin Sallah, don haka, Masallaci zai yi sujjada bayan Sallama saboda yazo da ƙarin abin da babu shi.
- ✓ Wanda ya cakuɗa karatun wata ayar da na wata ayar daban babu komai a kansa.
- ✓ Wanda ya canza lafazin Alƙur'ani ko kuma ya ɓata ma'anar karatun ta hanyar canza wasali ko kuma wata kalma, ko wani harafi a bisa rafkanuwa; zai yi sujjada bayan Sallama, saboda ƙari ya yi.
- ✓ In kuwa ya canza ma'anar Alƙu'rani ko kuma wani lafazi ko wani harafi a bisa ganganci; Sallarsa ta ɓaci domin yazo da zancen da ba ya cikin Sallah.

وَمَنْ نَعَسَ فِي الصَّلاَةِ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ، وَإِنْ ثَقُلَ نَوْمُهُ أَعَادَ الصَّلاَةَ وَالْوُضُوءَ.

"Wanda ya yi gyangyadi a cikin Sallah babu komai a kansa, idan kuwa ya yi nauyi, zai sake Sallah tare da alwala"

- ✓ Wanda gyangyanɗi ya ɗauke shi a cikin Sallah babu komai a kansa, ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.

- ✓ In gyangyaɗin ya yi nauyi har ya zama barci Sallarsa ta ɓaci haka ma alwalarsa ta warware, sai ya sake alwala da kuma Sallah.

وَأَنِينُ الْمَرِيضِ مُغْتَفَرٌ وَالتَّنَحْنُحُ لِلضَّرُورَةِ مُغْتَفَرٌ، وَلِلإِفْهَامِ مُنْكَرٌ وَلاَ تُبْطَلُ الصَّلاَةُ بِهِ

"Nishin mara lafiya, abin yi wa gafara ne. Yin nishi mai ƙarfi saboda lalura abin gafartawa ne, amma in don fahimtarwa ne, ba a son haka ba, Sallah ba ta ɓaci saboda shi"

- ✓ Sallah ba ta ɓaci sakamakon hakin mara lafiya asali ma shi abin yi wa gafara ne.
- ✓ Haki wani sauti ne da yake bayyana daga mara lafiya, hukuncinsa hukuncin zance ne a cikin Sallah, sai dai an yi afuwa saboda uzurin rashin lafiya.
- ✓ Wanda ya yi gyaran murya don ya fahimtar ko ya yi nuni ga wani abu kuma ya tsawaita; haƙiƙa ya aikata abin ƙi amma Sallarsa bata ɓaci ba.

وَمَنْ نَادَاهُ أَحَدٌ فَقَالَ لَهُ: سُبْحَانَ اللهِ كُرِهَ وَصَحَّتْ صَلاَتُهُ.

"Wanda wani ya kira shi yana Sallah, sai ya ce masa "Subhanallah" ya aikata abin ƙi amma Sallar sa ta inganta"

- ✓ Wanda aka kira shi alhalin yana Sallah ba a son ya yi wata Magana amma in ya ce "Subhanallahi" ya aikata abin ƙi amma Sallarsa bata ɓaci ba.
- ✓ Da kuwa zai amsa kiran da wanin wancan lafazin Sallarsa ta ɓaci.

وَمَنْ وَقَفَ فِي الْقِرَاءَةِ وَلَمْ يَفْتَحْ عَلَيْهِ أَحَدٌ تَرَكَ تِلْكَ الآيَةِ وَقَرَأَ مَا بَعْدَهَا، فَإِنْ تَعَذَّرَتْ عَلَيْهِ رَكَعَ. وَلاَ يَنْظُرُ مُصْحَفًا بَيْنَ يَدَيْهِ إِلاَّ أَنْ يَكُونَ فِي الْفَاتِحَةِ فَلاَ بُدَّ مِنْ كَمَالِهَا بِمُصْحَفٍ أَوْ غَيْرِهِ، فَإِنْ تَرَكَ مِنْهَا آيَةً سَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ، وَإِنْ كَانَ أَكْثَرَ بَطَلَتْ صَلاَتُهُ.

"Wanda ya tsaya yana cikin karatu, babu wanda ya ɗaura masa ko ya tuna masa, ya bar wannan ayar ya koma wata, idan hakan ya gagara to ya yi ruku'u. Ba zai duba Alƙur'ani a cikin Sallah ba, sai dai idan karatun Fatiha ne, idan ba zai iya ba. Idan ya bar wata aya (a cikin Fatiha), zai yi sujjada kafin Sallama, idan kuwa ya haura aya ɗaya, Sallarsa ta ɓaci"

- ✓ Lokacin da Liman ya kakare ko ya maƙale a wata aya ya kasa gaba ko baya; ya bar Surar ya koma wadda zai iya karantawa. In ya kasa gaba ko baya, ya kasa ɗauko wani gurin; ya yi ruku'u, babu komai a kansa.
- ✓ Ba ya halatta ga mai sallar (Farilla) ya ɗauki Allo ko Alƙur'ani ya karanta a cikin Sallah sai dai in Fatiha ce, ita ma in ba zai iya biyawa da ka ba.
- ✓ Duk wanda ya bar aya guda a cikin Fatiha zai yi sujjada kafin Sallama kasancewar ya yi tawaya a cikin farilla.
- ✓ Wanda ya bar aya fiye da guda; Sallarsa ta ɓaci.

وَمَنْ فَتَحَ عَلَى غَيْرِ إِمَامِهِ بَطَلَتْ صَلاَتُهُ. وَلاَ يَفْتَحُ عَلَى إِمَامِهِ إِلاَّ أَنْ يَنْتَظِرَ الْفَتْحَ أَوْ يُفْسِدَ الْمَعْنَى.

"Wanda ya yi wa wani gyaran karatu, ba kuma limaminsa ba ne, Sallarsa ta ɓaci. Ba a daurawa limami karatu, sai idan ya buƙaci a ɗaura masa, ta hanyar ya yi shiru, ko kuma idan ya ɓata ma'anar Alƙur'ani"

- ✓ Idan Limaminka ya kakare a cikin karatu babu laifi ka tuna masa in ya buƙaci hakan ta hanyar yin shiru ko kai-komo.
- ✓ Amma wanda yana bin liman Sallah, sai ya ji wani Limamin daban a gefe ya kakare sai ya yi masa gyara; Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Haka, wanda ya ɓata karatun Alƙur'ani a cikin Sallah; za a gyara masa.

وَمَنْ جَالَ فِكْرُهُ قَلِيلاً فِي أُمُورِ الدُّنْيَا نَقَصَ ثَوَابُهُ وَلَمْ تَبْطُلْ صَلاَتُهُ

"Wanda ya yi tunani kaɗan a cikin al'amuran duniya; ladansa ya tawaya, amma Sallarsa ta inganta"

- ✓ Wanda zuciyarsa ta tafi tunani kaɗan na wani abu na duniya babu komai a kansa, ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba amma ladansa ya samu tawaya.
- ✓ An so ga mai Sallah ya ajiye dukkanin wani tunanina al'amuran duniya kafin ya shiga Sallah domin hakan sababi ne tafiyar kushu'i.

وَمَنْ دَفَعَ الْمَاشِي بَيْنَ يَدَيْهِ أَوْ سَجَدَ عَلَى شِقِّ جَبْهَتِهِ أَوْ سَجَدَ عَلَى طَيَّةٍ أَوْ طَيَّتَيْنِ مِنْ عِمَامَتِهِ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ.

“Wanda ya tunkuɗe mai wucewa ta gabansa, babu komai a kansa. Wanda ya yi sujjada ta gefen goshinsa, ko ya yi sujjada a kan yadi, ko ninkin yadi biyu na rawaninsa, babu komai a gare shi”

- ✓ Babu laifi ga mai Sallah in ya ture wanda zai gifta ta gabansa kamar yadda Ma’aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya bayyana.
- ✓ Turewar ta zama yar kaɗan ba kamar ta faɗuwa ba, domin babban abin da shari’a take so shi ne hana shi wucewa ba rigima da shi ba.
- ✓ Haka babu laifi ga wanda ya yi sujjada a gefen goshinsa ko hular da ta rufe goshi.

وَلاَ شَيْءَ فِي غَلَبَةِ الْقَيْءِ وَالْقَلَس فِي الصَّلاَةِ

“Wanda kumallo ko magwas ya rinjayeshi a cikin Sallah, babu komai a a kansa”

- ✓ Wanda ya same su sanadiyyar rinjayar tashin zuciya ko rashin lafiya babu wani abu a kansa, haka ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.

وَسَهْوُ الْمَأْمُومِ يَحْمِلُهُ الإِمَامُ إِلاَّ أَنْ يَكُونَ مِنْ نَقْص الفَرِيضَةِ،

“Rafkanuwar mai bin Sallah, limami yana ɗauketa, sai idan ko a cikin farillah ne”

- ✓ Dukkan rafkanuwar mai bin Sallah Liman yana ɗauketa sai dai in rukuni ya bari, amma ban da Fatiha.

وَإِذَا سَهَا الْمَأْمُومُ أَوْ نَعَسَ أَوْ زُوحِمَ عَنِ الرُّكُوعِ وَهُوَ فِي غَيْرِ الأُولَى، فَإِنْ طَمِعَ فِي إِدْرَاكِ الإِمَامِ قَبْلَ رَفْعِهِ مِنَ السَّجْدَةِ الثَّانِيَةِ رَكَعَ وَلَحِقَهُ، وَإِنْ لَمْ يَطْمَعْ تَرَكَ الرُّكُوعَ وَتَبِعَ إِمَامَهُ وَقَضَى رَكْعَةً فِي مَوْضِعِهَا بَعْدَ سَلاَمِ إِمَامِهِ.

“Idan mai bin liman ya yi rafkanuwa, ko ya yi gyangyadi, ko saboda cunkoson mutane ya kasa cikakken ruku'u, kuma ba a raka'ar farko ba, idan yana da tabbacin zai riski liman kafin ya ɗago daga sujjada ta biyu, sai ya yi ruku'un ya riski liman, idan kuwa ba shi da tabbacin riskar liman, to ya bar ruku'un ya bi liman, ya sake wannan raka'ar bayan Sallamar limaminsa”

- ✓ Wanda gyangyaɗi ko mantuwa ko cunkoson sahu ya hana shi samun ruku'u tare da Liman; in yana da tabbacin zai riski Liman kafi ya ɗago daga sujjada ta ƙarshe, ya yi ruku'un ya ɗago sannan yay a tafi sujjada ta farko ya ɗago sannan ya rsiki Liman a sujjada ta biyu.
- ✓ In ba shi da tabbacin samun Liman kafin ya ɗago daga sujjada ta biyu; ya bar ruku'un ya tafi in da liman yake sa'annan in ya kammala Sallah sai yazo da raka'ar da ta kufce masa.

وَإِنْ سَهَا عَنِ السُّجُودِ أَوْ زُوحِمَ أَوْ نَعَسَ حَتَّى قَامَ الإِمَامُ إِلَى رَكْعَةٍ أُخْرَى سَجَدَ إِنْ طَمِعَ فِي إِدْرَاكِ الإِمَامِ قَبْلَ الرُّكُوعِ وَإِلاَّ تَرَكَهُ وَتَبِعَ الإِمَامَ وَقَضَى رَكْعَةً أُخْرَى أَيْضًا، وَحَيْثُ قَضَى الرَّكْعَةَ فَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ إِلاَّ أَنْ يَكُونَ شَاكًّا فِي الرُّكُوعِ أَوْ السُّجُودِ،

"Idan ya yi rafkanuwa game da sujjada ko kuma matsi ya hana shi ko ya yi gyangyaɗi har liman ya miƙe izuwa wata raka'ar, zai yi sujjadar idan yana da tabbacin riskar liman kafin ya yi ruku'u. Idan kuwa ba shi da tabbacin riskarsa, to zai bar shi, saiya rama wata raka'ar daban, ba zai yi sujjada ba sakamakon rama raka'ar da ya yi, sai dai ko yana kokwantone cikin ruku'un ko sujjadar"

- ✓ Wanda gyangyaɗi ko mantuwa ko cunkoson sahu ya hana shi samun sujjada tare da Liman; in yana da tabbacin zai riski Liman kafin ya ƙulla ruku'u, ya yi sujjadar ya ɗago sannan ya yi riski Liman a tsaye ko kuma a cikin ruku'u
- ✓ In ba shi da tabbacin samun Liman kafin ya ɗago daga Ruku'u; ya bar sujjadar da ta kufce masa, ya riski Liman a in da yake.

وَمَنْ جَاءَتْهُ عَقْرَبٌ أَوْ حَيَّةٌ فَقَتَلَهَا فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ إِلاَّ أَنْ يَطُولَ فِعْلُهُ أَوْ يَسْتَدْبِرَ الْقِبْلَةَ فَإِنَّهُ يَقْطَعُ

"Wanda maciji ya nufo shi ko kunama, sai ya kashe shi ko ya kasheta, babu komai a kansa, sai idan aikin kashewar ya tsawaita har ya juyawa alƙibla baya; Sallarsa ta ɓaci"

- ✓ Haka hukuncin yake ga wanda ya ga wata dabba mai cutarwa kamar cinnaka ko tumadigayya ko Tururruwa da makamantansu.

- ✓ Duk zai iya kasha su ne idan suna kusa da shi kuma yana da abin kashewar a kusa ba tare da ya haifar da wani aiki mai yawa ba, ko kuma ya juyawa alƙibla baya ba, in ɗaya daga cikinsu ya faru Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Ma'aiki tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi umarnin da a kashe baƙaƙe biyu (Kunama da Maciji) ko da kuwa a cikin Sallah ne.

وَمَنْ شَكَّ هَلْ هُوَ فِي الْوِتْرِ أَوْ فِي ثَانِيَةِ الشَّفْعِ جَعَلَهَا ثَانِيَةَ الشَّفْعِ وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ ثُمَّ أَوْتَرَ.

"Wanda ya yi kokwanto shin a wutiri yake ko a kuma a raka'a ta biyu a cikin shafa'i yake; ya sanya ta biyun shafa'in, sai ya yi sujjada bayan Sallama, sannan ya yi wuturi"

- ✓ Wanda yake gabatar da Sallar Nafila (Shafa'i da Wutiri) sai ya yi shakkar a wutiri yake ko kuma a raka'a ta biyu cikin shafa'i yake; hukuncinsa shi ne ya ɗauketa a matsayin ta biyu ce a cikin shafa'i sai ya yi sujjadar rafkanuwa bayan Sallama -kasancewar akwai yiwuwar ya yi ƙari sannan ya sallaci wutirin.

وَمَنْ تَكَلَّمَ بَيْنَ الشَّفْعِ وَالْوَتْرِ سَاهِيًا فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ، وَإِنْ كَانَ عَامِدًا كُرِهَ وَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ.

"Wanda ya yi zance tsakanin shafa'i da wuturi, yana mai rafkanuwa, babu komai a kansa, idan kuwa da ganganci ne, an ƙyamaci hakan, amma babu komai a kansa"

- ✓ Wanda ya sallaci shafa'i an so ya yi wutiri ba tare da ya rarrabe tsakaninsu da wata Magana ba, in ya yi Magana a tsakaninsu a bisa mantuwa ko kuma bisa ganganci babu komai akansa.

وَالْمَسْبُوقُ إِنْ أَدْرَكَ مَعَ الإِمَامِ أَقَلَّ مِنْ رَكْعَةٍ فَلاَ يَسْجُدُ مَعَهُ لاَ قَبْلِيًّا وَلاَ بَعْدِيًّا فَإِنْ سَجَدَ مَعَهُ بَطَلَتْ صَلاَتُهُ

"Wanda aka tsere masa a Sallah, idan ya riski abin da bai kai raka'a ba, to ba zai yi sujjada ƙabali ko ba'adi ba, idan kuwa ya yi sujjada tare da shi, to Sallar sa ta ɓaci"

- ✓ Wanda ya samu ƙasa da sujjada guda biyu ta ƙarshe ba zai yi kowace irin sujjadar rafkanuwa tare da Liman ba, in kuwa ya aikata Sallarsa ta ɓaci.

- ✓ Wanda ya tsinci kansa a irin wannan halin sannan Liman ya yunƙura don yin sujjada kafin Sallama; ba zai bi shi ba, zai zauna har Liman ya kammala sujjadarsa ya dawo ya zauna ya yi Sallama sannan sai ya miƙe ya ciko sallolinsa gabaɗaya.
- ✓ In kuwa Liman yayi Sujjada bayan Sallama; babu ruwanka da shi.
- ✓ Wanda ya riski Liman yana sujjadar rafkanuwa sai ya yi Kabbara ya bi shi yana tsammanin Sallar asali ce; babu komai a kansa, zai ɗaura Sallarsa

✓ وَإِنْ أَدْرَكَ رَكْعَةً كَامِلَةً أَوْ أَكْثَرَ سَجَدَ مَعَهُ الْقَبْلِيَّ وَأَخَّرَ البَعْدِيَّ حَتَّى يُتِمَّ صَلاَتَهُ فَيَسْجُدَ بَعْدَ سَلاَمِهِ، فَإِنْ سَجَدَ مَعَ الإِمَامِ عَامِدًا بَطَلَتْ صَلاَتُهُ وَإِنْ كَانَ سَاهِيًا سَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ،

"Idan kuwa ya riski cikakkiyar raka'a ɗaya ko sama da haka, to zai yi sujjada ta ƙabali tare da liman, ya jinkirta sujjada ba'adi har sai ya cika Sallarsa, sai ya yi sujjada bayan Sallama, idan yayi sujjada tare da liman da ganganci, Sallarsa ta ɓaci, idan kuwa bisa rafkanuwa ce, zai yi sujjada bayan Sallama"

- ✓ Wanda ya riski cikakkiyyar raka'a tare da Liman ko fiye da haka in Sajjadar rafkanuwa kafin Sallama ta kama Liman, shi ma zai yi tare da shi ko da kuwa da shi aka yi rafkanuwar ko ba da shi aka yi ba.
- ✓ Idan rafkanuwar sujjada bayan Sallama ce; zai cika Sallarsa sannan ya kawo ta, in kuwa ya yi sujjadar tare da Liman Sallarsa ta ɓaci.

وَإِنْ سَهَا الْمَسْبُوقُ بَعْدَ سَلاَمِ الإِمَامِ فَهُوَ كَالْمُصَلِّي وَحْدَهُ

"Idan wanda Sallah ta kubce masa ya yi rafkanuwa bayan liman ya yi Sallama, hukuncinsa kamar mai yin Sallah shi kaɗai ne"

- ✓ Wato Liman ya rabu da shi don haka ba zai ɗauke rafkanuwarsa ba, sai ya gyarata da kansa ta hanyar sujjadar rafkanuwa.

وَإِذَا تَرَتَّبَ عَلَى الْمَسْبُوق بَعْدِيٌّ مِنْ جِهَةِ إِمَامِهِ وَقَبلِيٌّ مِنْ جِهَةِ نَفْسِهِ أَجْزَأَهُ الْقَبْلِيُّ.

“Idan sujjada ba'adi ta kama wanda aka tsere masa a Sallah ta ɓangaren limaminsa, kuma sujjada ƙabali ta kama shi a lokacin da yake cika Sallarsa; Sujjada kafin Sallama ta isar masa”

- ✓ Hukuncin yana keɓanta ne kan wanda ya samu wani sashi na Sallah tare da Liman, shi kuma ya cika wani ɓangaran shi kaɗai.

وَمَنْ نَسِيَ الرُّكُوعَ وَتَذَكَّرَهُ فِي السُّجُودِ رَجَعَ قَائِمًا، وَيُسْتَحَبُّ لَهُ أَنْ يُعِيدَ شَيْئًا مِنَ الْقِرَاءَةِ ثُمَّ يَرْكَعُ وَيَسْجُدُ بَعْدَ السَّلَامِ

“Wanda ya manta ruku'u bai tuna ba sai yana halin sujjada, to ya koma ya tsaya, kuma an so ya sake wani abu na karatu, sannan ya yi ruku'u ya yi sujjada bayan Sallama”

- ✓ Wanda ya manta ruku’u yana mai mantuwa, sai ya tuna lokacin da yake cikin sujjada; zai miƙe tsaye, in da hali ya karanta wani abu daga cikin Kur’ani kafin ya yi ruku’un domin abin da yake kafin ruku’u shi ne karatun Sura, bayan cikar Sallarsa sai ya yi sujjada bayan Sallama saboda ƙarin da ya faru a cikin Sallar.

. وَمَنْ نَسِيَ سَجْدَةً وَاحِدَةً وَتَذَكَّرَهَا بَعْدَ قِيَامِهِ رَجَعَ جَالِسًا وَسَجَدَهَا إِلاَّ أَنْ يَكُونَ قَدْ جَلَسَ قَبْلَ الْقِيَامِ فَلاَ يُعِيدُ الْجُلُوسَ. وَمَنْ نَسِيَ سَجْدَتَيْنِ خَرَّ سَاجِدًا وَلَمْ يَجْلِسْ وَيَسْجُدُ فِي جَمِيعِ ذَلِكَ بَعْدَ السَّلَامِ،

“Wanda ya manta sujjada guda ɗaya, sannan ya tunata bayan ya miƙe, to ya koma ya zauna sai ya yi sujjadar, sai ko idan ya riga ya zauna kafin ya miƙe, to ba zai sake zaman ba. Wanda ya manta sujjada guda biyu, toh ya yi sujjadar take, ba zai zauna ba, cikin duk abinda ya gabatan nan zai yi sujjada bayan Sallama”

- ✓ Wanda ya manta sujjada guda a bisa rafkanuwa sai ya tuna bayan ya miƙe hukuncinsa shi ne zai dawo ya yi zaman tsakanin sujjada sa’annan ya kawo sujjadar da bai yi ba. Zai yi sujjada bayan Sallama saboda ƙarin da ya yi a cikin Sallarsa.
- ✓ Wanda ya yi sujjadar farko sannan ya zauna tahiya bai yi sujjada ta biyu ba a bisa rafkanuwa; zai zo da wannan sujjadar amma ba zai sake Ttahiya ba. Zai yi sujjada bayan Sallama.

- ✓ Wanda ya manta sujjada guda biyu a raka’a ɗaya, zai tafi sujjada daga tsayen don kawo sujjada guda biyun da ya manta, bayan kammala Sallarsa ya yi sujjada bayan Sallama.

وَإِنْ تَذَكَّرَ السُّجُودَ بَعْدَ رَفْعِ رَأْسِهِ مِنَ الرَّكْعَةِ الَّتِي تَلِيهَا تَمَادَى عَلَى صَلاَتِهِ وَلَمْ يَرْجِعْ وَأَلْغَى رَكْعَةَ السَّهْوِ وَزَادَ رَكْعَةً فِي مَوْضِعِهَا بَانِيًا وَسَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ، إِنْ كَانَتْ مِنَ الأُوْلَيَيْنِ وَتَذَكَّرَ بَعْدَ عَقْدِ الثَّالِثَةِ، وَبَعْدَ السَّلاَمِ إِنْ لَمْ تَكُنْ مِنَ اَلأُوْلَيَيْنِ أَوْ كَانَتْ مِنْهُمَا وَتَذَكَّرَ قَبْلَ عَقْدِ الثَّالِثَةِ لِأَنَّ السُّورَةَ وَالْجُلُوسَ لَمْ يَفُوتَا.

“Idan ya tuna sujjada bayan ya ɗago kansa daga raka'ar da take bin ta ya zarce ba zai dawo ba, sai ya jefar da raka'ar da ya yi rafkanuwar, ya ƙaro wata raka'ar sannan ya yi sujjada kafin Sallama, idan ya kasance daga cikin raka'o'in farko ne, sai ya tuna bayan ƙulla raka'a ta uku. Idan kuma ta kasance bata cikin Raka'o'in farko, ko kuma tana cikinsu sannan ya tuna bayn ƙulla raka'a ta Uku. Domin Sura da zama basu wuce ba”

- ✓ Duk wanda ya bar wani rukuni daga cikin rukunan Sallah har ya shiga wata raka’ar; zai cigaba da Sallarsa, sai ya jefar da raka’ar da ya bar rukunin a cikinta, kuma ya yi sujjada bayan Sallama.
- ✓ Fita daga raka’a yana tabbatuwa da ɗagowa daga ruku’u.
- ✓ Wanda ya manta karatun Sura a Raka'o'i biyun farko bai tuna ba sai bayan da ya ƙulla raka’a ta uku; zai cigaba da Sallarsa bayan ya kammala sai ya yi sujjada kafin Sallama saboda barin karatun sura da ya yi.
- ✓ Amma in ya tuna kafin ya shiga raka’a ta uku; zai zo da surar sannan ya yi zaman tahiya, zai yi sujjada bayan Sallama domin karatun Sura da zaman tahiya basu kufce masa ba.

وَمَنْ سَلَّمَ شَاكًّا فِي كَمَالِ صِلاَتِهِ بَطَلَتْ صَلاَتُهُ،

“Wanda ya yi Sallama yana mai kokwanton cikar Sallarsa; Sallar sa ta ɓaci”

- ✓ Wanda ya yi shakka a cikin cikar Sallar; zai zo da adadin abin da yake shakkar, sannan ya yi sujjadar rafkanuwa daidai da abin da ya bari.

- ✓ Idan kuma ya yi Sallama ba tare da yazo da abin da yake kokonto a kansa ba; Sallarsa ta ɓaci, sai dai ga mai yawan kokonto, wannan hukuncinsa ya gabata.

وَالسَّهْوُ فِي صَلاَةِ الْقَضَاءِ كَالسَّهْوِ فِي صَلاَةِ الأَدَاءِ

"Yin rafkanuwa a Sallar ramuwa, kamar rafkanuwa ne a Sallar da ba ta ramuwa ba"

- ✓ Domin dukkansu farillai ne kuma hukuncinsu ɗaya ne.

وَالسَّهْوُ فِي النَّافِلَةِ كَالسَّهْوِ فِي الْفَرِيضَةِ إِلاَّ فِي سِتِّ مَسَائِلَ: الْفَاتِحَةِ وَالسُّورَةِ وَالسِّرِّ وَالْجَهْرِ، وَزِيَادَةِ رَكْعَةٍ وَنِسْيَانِ بَعْضِ الأَرْكَانِ إِنْ طَالَ،

"Yin rafkanuwa a Sallar nafila kamar rafkanuwa ne a Sallar farillah, idan ban da gurare guda shida: Fatiha, Sura, sirrantawa, bayyanawa, ƙarin cikakkiyar raka'a, manta sashin farillai idan ya tsawaita"

- ✓ Duk hukunce-hukuncen rafkanuwa a sallolin farilla haka suke a sallolin nafila ban da a guri Shida kamar yadda malam zai bayyana su a gaba.

فَمَنْ نَسِيَ الْفَاتِحَةَ فِي النَّافِلَةِ وَتَذَكَّرَ بَعْدَ الرُّكُوعِ تَمَادَى وَسَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ بِخِلاَفِ الْفَرِيضَةِ فَإِنَّهُ يُلْغِي تِلْكَ الرَّكْعَةَ وَيَزِيدُ أُخْرَى وَيَتَمَادَى وَيَكُونُ سُجُودُهُ كَمَا ذَكَرْنَا فِي تَارِكِ السُّجُودِ

"Wanda ya manta karatun Fatiha a Sallar nafila, sai ya tuna bayan ruku'u, to ya zarce da Sallar sa, sai yayi sujjada kafin Sallama saɓanin Sallar farillah, domin a Sallar farillah zai jefar da raka'ar ce ya karo wata raka'ar daban, sai ya zarce, sujjadarsa za ta kasance kamar yadda muka ambata a cikin wanda yabar sujjada"

- ✓ Malam ya fara bayanin hukunce-hukuncen da suke da bambanci tsakanin Sallar farilla da kuma Sallar Nafila.
- ✓ A Sallar nafila wanda ya bar karatun Fatiha bai tuna ba sai bayan da ya ɗago daga ruku'u zai cigaba da Sallarsa idan ya kammala sai ya yi sujjada kafin Sallama. Amma in a Sallar farilla ce babu makawa zai

jefar da wannan raka'ar yazo da wata sa'annan ya yi sujjadr rafkanuwa kafin Sallama.

. وَمَنْ نَسِيَ السُّورَةَ أَوِ الْجَهْرَ أَوْ السِّرَّ فِي النَّافِلَةِ وَتَذَكَّرَ بَعْدَ الرُّكُوعِ تَمَادَى وَلاَ سُجُودَ عَلَيْهِ بِخِلاَفِ الْفَرِيضَةِ.

"Wanda ya manta karatun Sura ko bayyanawa ko sirrantawa a Sallar nafila, sai ya tuna bayan ya yi ruku'u; ya zarce da Sallar sa, babu sujjada a kansa saɓanin Sallar farilla"

- ✓ Ba a sujjadar rafkanuwa saboda barin karatun Sura kasancewar karatun Sura Sunna ne mai ƙarfi amma a Sallar farilla kaɗai.
- ✓ Haka ɓoye karatu a cikin sallolin dare na nafila ko kuma bayyana karatu a cikin sallolin nafila na yini ba a yi masu sujjadar rafkanuwa.

وَمَنْ قَامَ إِلَى ثَالِثَةٍ فِي النَّافِلَةِ فَإِنْ تَذَكَّرَ قَبْلَ عَقْدِ الرُّكُوعِ رَجَعَ وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ، وَإِنْ عَقَدَ الثَّالِثَة تَمَادَى وَزَادَ الرَّابِعَة وَسَجَدَ قَبْلَ السَّلاَمِ بِخِلاَفِ الْفَرِيضَةِ فَإِنَّهُ يَرْجِعُ مَتَى مَا ذَكَرَ وَيَسْجُدُ بَعْدَ السَّلاَمِ

"Wanda ya miƙe izuwa raka'a ta uku a Sallar nafila, idan ya tuna kafin ƙulla raka'a to zai koma ya zauna, ya yi sujjada bayan Sallama, idan kuma ya ƙulla raka'a ta uku , to ya zarce sai ya ƙara raka'a ta hudu sannan ya yi sujjada kafin Sallama, saɓanin Sallar farillah, domin a Sallar farillah, zai koma a lokacin da ya tuna, sa'annan ya yi sujjada bayan Sallama"

- ✓ Wanda ya miƙe zuwa raka'a ta Uku a cikin nafila hukuncinsa baya fitra daga ɗayan abu biyu:
- ✓ Ko dai ya tuna kafin ya ƙulla ruku'u na raka'a ta ukun,
- ✓ Ko kuma ya tuna bayan ya ƙulla ruku'u na raka'a ta uku to zai cigaba da wannan raka'ar (ta uku) sannan ya ƙara ɗaya su zama huɗu, ya yi sujjada bayan Sallama idan ya kammala Sallarsa.

. وَمَنْ نَسِيَ رُكْنًا مِنْ النَّافِلَةِ كَالرُّكُوعِ أَوْ السُّجُودِ وَلَمْ يَتَذَكَّرْ حَتَّى سَلَّمَ وَطَالَ فَلاَ إِعَادَةَ عَلَيْهِ بِخِلاَفِ الْفَرِيضَةِ فَإِنَّهُ يُعِيدُهَا أَبَدًا،

“Wanda ya manta wani rukuni a cikin Sallar nafila, kamar ruku'u, ko sujjada, sannan bai tuna ba, har sai da ya yi Sallama, sannan ya tsawaita, ba zai sake ba, saɓanin farilla, domin sai ya saketa har abada”

- ✓ Idan masallaci ya bar wani rukuni a bisa mantuwa daga cikin Sallarsa ta nafila (Kamar Sujjada da kuma Ruku’u) kuma bai tuna ba sai bayan dogon lokaci; ba zai sake Sallarsa ba kuma ba zai yi sujjadar rafkanuwa ba.
- ✓ Idan kuwa a Sallar farilla ce; sai ya sake Sallar gabaɗayanta.

وَمَنْ قَطَعَ النَّافِلَةَ عَامِدًا أَوْ تَرَكَ مِنْهَا رَكْعَةً أَوْ سَجْدَةً عَامِدًا أَعَادَهَا أَبَدًا.

“Wanda ya yanke nafila da gangan, ko ya bar wani abu daga cikinta, kamar raka'a ko sujjada; ya sake ta har abada”

- ✓ Wanda ya fara Sallar nafila sannan ya bar ta da gangan, kuma ya bar wani rukuni ko kuma wata Sunna mai ƙarfi bisa ganganci; Sallarsa ta ɓaci, wajibi ne ya saketa gabaɗaya.

وَمَنْ تَنَهَّدَ فِي صَلاَتِهِ فَلاَ شَيْءَ عَلَيْهِ إِلاَّ أَنْ يَنْطِقَ بِحُرُوفٍ.

“Wanda ya turo ƙirjinsa sanadiyyar numfashi mai ƙarfi a cikin Sallah, babu laifi a kansa, sai dai idan ya furta harufa”

- ✓ Wanda ya yi doguwar ajiyar zuciya sanadiyyar wani abu da yake tunani na duniya ko na Lahira babu komai akansa kasancewar wani abu ne ya yi rinjaye a kansa, sai dai in sanadiyyar hakan ya jawo wani harafi ya fito; hukuncinsa sai ya zama kamar hukuncin mai zance a Sallah ne.
- ✓ Yin hakan a bisa ganaganci zai lalata Sallah, aika haka hakan a bisa rafkanuwa kuma zai tilasta masa yin sujjada bayan Sallama, kasancewar furta harafi kamar ƙari ne a cikin Sallah.

وَإِذَا سَهَا الإِمَامُ بِنَقْصٍ أَوْ زِيَادَةٍ سَبَّحَ بِهِ الْمَأْمُومُ،

“Idan liman ya yi rafkanuwa ta hanyar ƙari ko ragi, to masu bin sa Sallah sai su yi masa tasbihi”

- ✓ Ta hanyar cewa “Subhanallah”.
- ✓ Babu laifi Mace ko Namiji su faɗakar da Liman ya yin da ya yi rafkanuwa ta hanyar yi masa Tasbihi.

وَإِذَا قَامَ إِمَامُكَ مِنْ رَكْعَتَيْنِ فَسَبِّحْ بِهِ، فَإِنْ فَارَقَ الأَرْضَ فَاتْبَعْهُ،

“Idan Limaminka ya miƙe daga raka'a ta biyu, to ka yi masa tasbihi, idan har ya riga ya rabu da ƙasa, to ka bi shi, idan ya zauna a raka'ar farko ko ta uku; kar ka zauna tare da shi”

- ✓ Bayan Liman ya ɗago daga sujjada a raka’a ta biyu, maimakon ya zauna tahiya sai ya yi yunƙurin miƙewa, a irin wannan halin masu bin sa Sallah za su yi masa Tasbihi, in ya faɗaku ya zauna kafin tafukansa da gwiwarsa su rabu da ƙasa; babu sujjada a kansa.
- ✓ In kuwa tafukansa da gwiwarsa suka bar ƙasa har ya miƙe; ba zai dawo ba, sai ya yi sujjada kafin Sallama saboda tauye Tahiya da ya yi.
- ✓ Idan Liman ya manta ya zauna a raka’a ta farko ka ta uku, masu bin sa Sallah za su yi masa Tasbihi don faɗakar da shi.

وَإِنْ جَلَسَ فِي الأولَى أَوْ فِي الثَّالِثَةِ فَقُمْ وَلاَ تَجْلِسْ مَعَهُ، وَإِنْ سَجَدَ وَاحِدَةً وَتَرَكَ الثَّانِيَة فَسَبِّحْ بِهِ وَلاَ تَقُمْ مَعَهُ إِلاَّ أَنْ تَخَافَ عَقْدَ رُكُوعِهِ فَاتْبَعْهُ وَلاَ تَجْلِسْ بَعْدَ ذَلِكَ مَعَهُ لاَ فِي ثَانِيَةٍ وَلاَ فِي رَابِعَةٍ، فَإِذَا سَلَّمَ فَزِدْ رَكْعَةً أُخْرَى بَدَلاً مِنْ الرَّكْعَةِ الَّتِي أَلْغَيْتَهَا بَانِيًا وَتَسْجُدُ قَبْلَ السَّلاَمِ، فَإِنْ كُنْتُمْ جَمَاعَةً الأَفْضَلُ لَكُمْ أَنْ تُقَدِّمُوا وَاحِدًا يُتِمُّ بِكُمْ،

“Idan Liman ya yi sujjadar farko ya bar ta biyu, to ka yi masa tasbihi, kar ka tashi tare da shi, sai idan ka tsoraci ƙulla ruku'unsa, sai ka bi shi, kada ka zauna tare da shi bayan haka, hakan kuwa a raka'a ta biyu ko raka'a ta huɗu, idan ya yi Sallama; sai ka ciko raka'a daya, madadin raka'ar da ka jefar da ita, sai ka yi sujjada kafin Sallama, idan kun kasance kuna da yawa, to abin da yafi ku gabatar da ɗayanku ya cika muku Sallah”

- ✓ Idan Liman ya bar sujjada ta biyu a raka’a ta farko, yana da hali biyu:
- ✓ Ko dai masu bin sa Sallah su faɗakar da shi ta hanyar yi masa tasbihi, shi kuma ya faɗaku ya dawo ya gyara, wannan babu wata matsala.

- ✓ Ko kuma masu Sallah su faɗakar da shi amma kuma ya ƙi dawowa ya gyara; in irin haka ya faru masu bin sa Sallah za su ciko ragowar sujjadar da bai yi ba, sannan su miƙe su cigaba da binsa.
- ✓ Sai dai in suna tsoron kafin su gyara abin da ya ɓata zai ƙulla ruku'u, sai su bar sujjadar su bi shi.
- ✓ Idan Liman ya zauna yin tahiya a raka'a ta biyu masu bin sa Sallah ba zasu zauna tare da shi ba, saboda su raka'ar Liman ta biyu ita ce ta farko a gurinsu, saboda sun jefar da raka'ar farko da Liman ya yi kuskure a cikinta kuma bai gyara ba.
- ✓ Haka, Idan Liman ya zauna yin tahiya a raka'a ta huɗu masu bin sa Sallah ba za su zauna tare da shi ba, saboda su raka'ar Liman ta huɗu ita ce ta uku a gurinsu, saboda sun jefar da raka'ar farko da Liman ya yi kuskure a cikinta kuma bai gyara ba.
- ✓ Idan sun kammala Sallar za su yi sujjada kafin Sallama saboda ƙarin raka'a da kuma tauye karatun Sallah da kuma zaman tsakiya.
- ✓ Idan mutum biyu ne zuwa sama suka samu riin mnatsalar da ta gabata tare da Liman; su sanya wani daban daga cikinsu ya zama Limaminsu.
- ✓ Amma in suka kammala a ɗaiɗaikun su Sallarsu ta yi.

وَإِذَا زَادَ الإِمَامُ سَجْدَةً ثَالِثَةً فَسَبِّحْ بِهِ وَلاَ تَسْجُدْ مَعَهُ،

"Idan liman ya ƙara sujjada ta uku; ku yi masa tasbihi, kar ku yi sujjada tare da shi"

- ✓ Domin shi Lima nana yi masa biyayya ne kaɗai cikin abin da aka umarce shi da shi.
- ✓ Idan ya aikata ƙarin sujjada ta uku a bisa rafkanuwa kuma aka yi masa Tasbihi don faɗakar da shi kuma ya faɗaku bayan kammala Sallah zai yi sujjada bayan Sallama tare da masu bin sa.
- ✓ Idan kuwa ya aikata haka a bisa ganganci kuma masu bin sa Sallah suka bi shi a kan haka; Sallarsa ta ɓaci gabaɗayanta, haka suma masu bin sa tasu ta ɓaci.

وَإِذَا قَامَ الإِمَامُ إِلَى خَامِسَةٍ تَبِعَهُ مَنْ تَيَقَّنَ مُوجِبَهَا أَوْ شَكَّ فِيهِ وَجَلَسَ مَنْ تَيَقَّنَ زِيَادَتَهَا، فَإِنْ جَلَسَ الأَوَّلُ وَقَامَ الثَّانِي بَطَلَتْ صَلاَتُهُ،

"Idan Liman ya tashi raka'a ta biyar, wanda yake da yaƙinin cikar Sallar zai bi shi, ko idan ya yi kokwanto a kan cikar Sallar, sai ya zauna, wanda ya samu tabbacin wannan raka'ar ƙari ce ko ta biyar ce, idan ya zauna a ta farko sannan ya tashi a ta biyu, to Sallar sa ta ɓaci.

- ✓ Wanda yake da yaƙinin cikar raka'a ta huɗu sannan Liman ya miƙe zuwa ta biyar; wajibi ne ya zauna ya yi masa tasbihi, idan ya faɗaku shi ke nan, idan kuwa bai faɗaku ba, ba za ka bi shi ba, in kuwa ka bi shi da gangan Sallarka ta ɓaci.
- ✓ Wanda yake da yaƙinin raka'a ta huɗu ce; zai bi Liman, in kuwa bai bi shi ba; Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Wanda yake kokwanto a kan cikar Sallah ko akasinta; zai bi Liman, in kuwa ya zauna bai bi shi ba Sallarsa ta ɓaci.
- ✓ Wanda bai fahimci adadin raka'o'in da liman ya yi ba sai ya zauna; Sallarsa ta ɓaci.

وَإِذَا سَلَّمَ الإِمَامُ قَبْلَ كَمَالِ الصَّلاَةِ سَبَّحَ بِهِ مَنْ خَلْفَهُ، فَإِنْ صَدَّقَهُ كَمَّلَ صَلاَتَهُ وَسَجَدَ بَعْدَ السَّلاَمِ. وَإِنْ شَكَّ فِي خَبَرِهِ سَأَلَ عَدْلَيْنِ وَجَازَ لَهُمَا الكَلاَمُ فِي ذَلِكَ،

"Idan liman ya yi Sallama kafin cikar Sallah, wadanda suke bayansa za su yi masa tasbihi, idan ya gaskatasu, to zai cika Sallar sa, sai ya yi sujjada bayan Sallama. Idan ya yi kokwanto a cikin labarinsa, to sai ya tambayi adalai guda biyu, domin magana ta halarta a cikin haka"

- ✓ Idan liman ya yi Sallama kafin cikar Salla yana mai ƙudurce cikarta wanda suke bin sa za su yi masa tashibi, idan ya faɗaku sai ya cika Sallarsa sa'annan ya yi sujjada bayan Sallama saboda ƙari da ya yin a Sallama.
- ✓ Idan kuwa ya yi shakka (wato yana ganin Sallarsa ta cika) sai ya tambayi mutum biyu da suke bayansa, in suka tabattar da ragi ko ƙari sai ya ciko abin da ya bari.

- ✓ Babu laifi yin magana a cikin irin wannan halin domin duk gyaran Sallah ne.

وَإِنْ تَيَقَّنَ الْكَمَالَ عَمِلَ عَلَى يَقِينِهِ وَتَرَكَ الْعَدْلَيْنِ إِلاَّ أَنْ يَكْثُرَ النَّاسُ خَلْفَهُ فَيَتْرُكَ يَقِينَهُ وَيَرْجِعَ إِلَيْهِمْ.

"Idan ya samu yaƙinin cikar Sallarsa, zai yi amfani da yaƙininsa, ya bar maganar waɗannan adalai guda biyu, sai idan mutane sun yawaita a bayansa, to ya bar yaƙininsa ya koma zuwa gare su"

- ✓ Idan Liman ya samu tabbas a kan cikar Sallarsa babu buƙatar tambayar adalai biyu.
- ✓ Idan ya samu ƙorafi daga mafi rinjayen masu binsa a kan rashin cikarta; zai bar yaƙininsa ya yi hukunci da na su.
- ✓ Idan rabin masu bin Liman suka ƙudurce cikar Sallah, rabi kuma suka ƙudurce rashin cikarta; kowana ɓangare zai yi gini akan tabbacinsa.

DUKKAN YABO DA GODIYA SUN TABBATA GA UBANGIJIN HALITTU.

WASU LITATTAFAN MAWALLAFIN DA SUKE TAFE

1. HAKIKANIN JANA'IZA A MUSULUNCI DA KURAKURANTA
2. RAYUWAR AURE A MUSULUNCI DA KURAKURANTA
3. KASUWANCI A MUSULUNCI
4. RIBA DA ILLOLINTA
5. TSARIN DA'AWA A MUSULUNCI DA KURAKURANSA
6. HANYOYIN CIN NASARA A RAYUWA
7. FASSARAR LITTAFIN TA'ALIMUL MUTA'ALLIM
8. USULUL-IMAN WA SAMARATUHU أصُول الإيمان وثمراته للمعاهد والكليات
9. SIYASA A MUSULUNCI DA AMFANINTA

Ana maraba da dukkanin wani gyara ko shawara mai kyau, ga mai buƙatar ɗaukar nauyin buga ɗaya daga cikin waɗannan litattafai, ko gabaɗaya; sai a tuntuɓi cibiyar fassara ta Ar-Rayhan:

GSM: 08036223067
Whatsapp: 07049325138
Email: abuamatullahi83@gmail.com